[12/30/2020, 8:27 PM] 🅰️ " AXEEX✌🏼 D'🅱️🅾️Y😎: *ABBAKAR*

*PAGE 1---5*
* da sunnan Allah Mai rahma Mai Jin Kai*

Juyi kawai yake baccin yak'i zuwa, tun bayan hutun dasukai na semester ending bacci yai masa k'aura koya kwanta baya iyawa saidai yaita juyi farin ciki tuni ya da'de da masa k'aura komai yake yak'e kawai yakeyi......Yau take jajiberin komawarsu makaranta duda ba al'adarsa bace shiga sch ranar da aka koma anman segashi tun watan da ya wuce yake tsimayin ranar dawowa..

Ji yake gabaki daya daren ya masa nisa gani yake kamar garin bazai wayeba ganin da yai baccin da gaske bazaizo ba yasa shi mik'ewa dan dauro alwala.

Asubar fari ya farka daga gajeren baccin da besan sanda ya 'daukeshi ba duda kuwa yadda wani bacci me dadi ke 'dibansa ayanzun haka ya daure yai wanka yafice masallaci.

Shida dai-dai ya gama shiryawa ko abinci bai tsaya ci ba ji yake kamar yai tsuntsu yaje makarantar, Da 'dan saurinsa ya sakko daga samansa yai sashin Hajiyarsu yana 'daura agogonsa.

Kamar yadda ya zata tana zaune tana wutiri kamar yadda al'adarta take ya'dan zauna kamar minti talatin bata shafa ba yana duban agogo yaga shida da rabi ya mik'e yai wajen falon yana kiran maryam dasauri ta fito daga magirka rik'e da cokali....Yaya ina kwana lafiya lau agogo sarkin aiki har'antashi kenan eh yaya to yayi kyau kicew Hajiya nazo tana addu'a  nafita to yaya abincinfa a'a kibarshi innaje office nasha ruwan zafi to yaya seka dawo.

Harya kai bakin k'ofar dazata sadashi da babban falon gidan Hajiya tace Allah ya dawo dakai lafiya dasauri ya dawo ya zube har 'kas ina kwana Hajiya lafiya lau ta fada tana murmushi ni zan futa to Allah yakaika lafiya ya dawo da kai lafiya Amin Hajiyarmu ya mi'ke yabar falon.
Bakwai da rabi a B.U.K ta masa office dunsa ya wuce ya 'dan shisshirya takardun dazai bu'kata yasha tea sannan ya fito zuwa
class.

Ahankula yake tafiya burinsa koda sau dayane ya doro idanunsa akanta dan abinda yada'de yana muradi kenan.

Kamar daga sama yaji ance good morning sir har cikin ransa yaji wani abu yar yasokeshi tabbas ita ce dan muryarta ta da'de da zama daram a kwanyarsa duk inda ya jita cikin mata 'dari sai ya ganeta.
Be juyo ba ko nuna alamar ya kula ya amsa da morning yai gaba kamar ko yaushe bata damuba Aisha tace kuyi sauri mu tafi aji kunsan halin mutumin nan inyashiga minyi rashin tayau

inyaso se yai attendance.......gaskiya ni fitsari nakeji kamar ya zubo sai dai inna rasa dan bazan iya zama dashi ba inji Ummulkhairi se kindawo inji Aisha.

Muje in raka ki inji Fatima a'a Fatina ki tafi karkiyi missing banso mu biyu mu rasa inkinanan kamar inanan ne a'a wallahi se naje kina da matsala muje.
Ina captain yake ya fada yana tsaye jikin madogarar malamai bezoba yayi kyau wani yazo ya gogen allo ya fada yana mik'o duster din .

Yayin da 'dalibi guda ke goge allo shikuma yana duba takaddun da yazo dasu saidai ahak'ik'anin gaskiya bawai takaddun yake dubawa ba afakaice 'daliban dake zaune yake kallo kaf ya dubesu sedai idanunsa sun kasa hango masa ita wato bata zo ba kenan kome.
No to muryar wa yaji hakan kenan na nufin santa yafara zautar dashi ta yadda inyaji muryar wata zai zata ita ce .....wani tunani ne yazo masa yai bakin k'ofa inda makararun 'dalibai ke tsai tsaiye duda sunsan bazai barsu su shigoba.
Kaf yabisu da kallo bata cikinsu yadan fito kadan suna zaune ita da k'awarta sai wata dabai saba ganinsu tareba sai namijin da indai zaigansu zaigansu dashi shima yana zaune kome suke tattaunawa yafada aransa oho.

Sannunku wato kune shafaffu da mai ko dabazaku iya tsaiwa ba sukai zuru zuru da ido suka kuma kasa mik'ewa yayi kyau yace .

Kuna tsayen zaku iya shigowa wannan yazama last time dazaku zomin aji a makare. Mungode malan ku godewa kanku ya shige ajin sukuma suka bi bayansa.
Bayan ya rubuta Topic din dazasuyi yau yajuyo kamar yadda na fada muku a first semester wata'kil in zama mutumin da zan daukeku wannan course din wata'kil a canza to ba'acanzaba kunsan dokoki na dan haka bana bu'katar sanar daku wanda suka mance su tambayi sauran 'Yan aji.
Yadan matsa bakin k'ofar kai yanzu bakaji kunya ba kana namiji kana cikin mata azaune ragwanci ba na maza bane yai shiru any way wato ku baza iya mik'ewar ba ko a'a malan munyi zaton bazaka barmu mushigo bane inji Fatima yayi kyau to yajuya Sorry sir yaji muryarta ta daki zuciyarsa yadan murmusa burinsa daman tai magana be juyo ba yace sorry for ur self pls sir amana afuwa ta kuma fade yadan juyo fuakar nan murtuk zaku iya shigowa but this should be ur last time coming to my class late. Ya shige ciki.

Yana rubutu suka shigo juyowar dazaiyi Ummulkhairi na 'kok'arin zama me idonsa zai gani ciki gareta dan da'kyarma ta zauna anya kuwa ba gaskiya idansa ya fada masa.
I have to get my self prove ke da kika zauna yanzu dawo gaba, Ummi da suka shigo tare ta mi'ke no bakebafa I mean Ummulkhairi bemasan ya fadi sunan ba gabaki daya ajin suka juya suna kallon Ummulkhairi watoyama san sunanta kenan wannan dan girman kan malamin. Itakuwa mutuwar zaune tai jin yakira sunanta wato bama afuska kawai yasantaba harda by name wai bakiji ni bane Fatima ta tab'ota ki koma karya koreki.

Ta mik'e daK'yar tayo gaba innalillahi wa'inna inna ilaihirraji'un dagaske cikin gareta mesan

samu nane yafa'da cikin ransa wato matar aure yake ma masifar so san da baijin zai iya rayuwa without ita a rayuwarsa.
Tazo inda ya nuna mata ta zauna da sauri ya juya ya ya goge hawayen da yatawo masa dan besan sauran 'daliban su gani.
Wayarsa ya'dauka kamar yana waya ya hau salati to ganinan ya maida aljihu captain dinkuwa yazo ya mi'ke 'dalibin dake zaune dasu ummu ne ungo wannan out line yana ciki gameso zai iya photostat dinsu inada wani abune me mayin manci pls am sorry yafice bai jira amsarsu ba........
*Zancigaba insha Allah*
[12/30/2020, 8:27 PM] 🅰️ " AXEEX✌🏼 D'🅱️🅾️Y😎: _POST BY GROUP OF HYPE HAUSA NOVELS BOOK WHATSAPP 08064400100_ 📚📚
[12/31/2020, 5:45 PM] 🅰️ " AXEEX✌🏼 D'🅱️🅾️Y😎: *ABBAKAR*

*PAGE 6---15*

Yana barin sch gate 'din hawayen da ya boye suka kwace seda yai nisa ka'dan da makarantar sannan yai packing kuka kuwa me 'karfi ya kwace masa yai kuka sosai har saida dankansa ya fara rarrashin kansa da zuciyarsa ya'dan jima a gun kafin ya goge hawayensa yabar wajen.

Acan sch kuwa bayan fitarsa 'dalubai sukayo kan Ummu suna tambayarta waike taya akai wannan 'dan rainin hankalin yasan sunanki ta ta'be baki taya zan sani "bakuga mutuwar zaune nayi ba dajin sunana abakinsa" "Ai wallahi naso ni yakira" inji Aisha "kunifa nasan da sansa zan mutu maryam ta fada suka saka dariya gabaki daya"

Maryam wai me damun yayanki ne? Hajiya ta tambaya "wallahi bansani ba naga dai kamar yana cikin damuwa " bari inje 'dakinnasa inji ta mi'ke tai section d'insa, yana zaune kan doguwar kujera kansa sama sai filo dake ri'ke a 'kirjinsa hawaye na bin fuskarsa "subhanallahi mezan gani inji Hajiya"

Me ke damunka ni mamarka ce ka'dan meke damunka I a sure u i will clear them all cikin zuciyarsa yace "Naso zaki iya mum sedai wannan ya wuce tunaninki naso zaki iya sharen hawayena saidai bazaki iyaba bakuma naso in saka ki cikin damuwa" Allah hajiya ba komai ta kalleshi cikin fushi yanzu kanunan ban isa dakaiba tinda bazaka iya fadan damuwarka ba ta juya zata fice.

Yai saurin kamo hannunta wallahi ba haka bane kawai na tuna da Baba Alhaji ne shiyasa nashiga damuwa bakuma nasan kema insaku come kin damuwa shi yasa naga gwanda inzauna a'daki ta juyo ta goge masa hawayensa bata iya cewa komi ba tabar 'dakin dan batasan yaga hawayenta.

Ahankula yace ki yafemin Hajiya na miki 'karya na kuma tuno miki da Alhaji ki yafemin.

Ummu pls kiyi sauri karki makara katafi kawai i can drop my self kinga ni kiyi sauri bakya

ganin cikin ne dake tai dariya na rasa me yasa kullun kake ganin kamar wannan cikin zaisa nazama lazy to da ke din mece pls be quick kin isheni da surutu au surutu nake ma to na fasa shiga motar taka haba abar sona pls ki tawo mutafi ta bude ta shiga tana turo baki ya rufe motar gami da jan motar yabar gun.

Allah ummu ban ta'ba ganin couples da suka dace da junaba kamar keda yayanki Allah ko sosaima tai dariya kawai.kinga kuma ni ban taba ganin dacewarmu dashi ba shi yasa ai kullin kike sansa kamar ranki baki da dama Aisha ni nace miki ina sansa any way mubar maganar.

Pls Fatina wai mene damu ne ummu ta tambaya. ina zaton 3304 muke au kina zato ne ma u are not serious wallahi anman ai nafiki tunda ke tambaya ma kike tai sukai dariya baki daya kinga mutafi aji koma mene magani acan suka wuce ajin.

Duk yadda Abbakar yaso mantawa da ummulkairi abin yaci tura kullin kamar 'kara masa santa ake innalillahi wa'inna ilaihirraji'un waime kesan samu nane Allah ka yaye min ka kuma yafemin ya fa'da.

Wayarsa ya 'dauka ya kira khairiyya wata frnd 'dinsa ta facebook be ta6a ganin yarinyar ba anman ya rasa me yasa ya yadda da ita sosai.

Wayar tata akashe take hakan yasa ya kunna Data 'dinsa ko Allah zaisa tana online aikuwa kafin ya shiga inbox 'dinsa message 'dunta ya shigo sallama ce kamar kullin wani ma ya shigo yayana yakake kwana biyu banjika ba na kira number dinka akashe yai murmushi.

Lafiya 'kalau 'Kanwata na'dan shiga matsala ne anman Alhamdulillah everything is normal ya tura mata wasu 'yan seconni sa'konta yashigo ayya Allah ya sau'ka'ka komai amin 'kanwata.

Wai yaushe zamu hadu ne? Ya tambaya ta turo hoton emoji alamar she is thinking matsalarki kenan kullin na miki maganar ha'duwa sekiyi tamin wala wala tai dariya let's give time some time yai dariya kullun haka kike cewa yayana mu hadu anjima yanzu malami ya shigo ajinmu ok .

Yau sati biyu kenan rabon Abbakar da sch tun randa yaga ummul kairi da ciki yaji a tsani makarantar ji yake kamarma yabar aikin sedai tuno yadda yasamu aikin yashi dolensa ya yanke shawarar komawa kodan kar ya cutarda students dinsa.

Yau yashirya zuwa hakan yasa yagama komi section din Hajiyarsu yaje sukai sallama ya wuce.

Yana tu'ki yana addu'a Allah yasa yau bata gaba wata'kil inbata gaban inbaya ganinta sosai yafijin kwarin gwiwar yin lecture din.

Aikuwa yana 'dora kafarsa acikin ajin idanunsa ita suka fara gani tana dariya ita da Fatima

'kawarta da alamun tanajin dadin firar dasike tai masa kyau sosai a ido innalillahi wa'inna'ilaihirraji'un abinda kawai ya fara fa'de kenan jiyai kamar 'kafafunsa bazasu 'daukeshi ba juyawa yau dan barin ajin........

Haba Abbakar be strong mana wani 6ari na zuciyarsa ya fa'da masa ya juya kawai ya shiga ajin duda yadda 'kirjinsa ke bugun uku- uku.

"Good morning class ya fa'da" morning sir suka fa'da suma "am sorry for my absence banji da'di bane kwana biyu hope u all read the manual i gave?" Yes gabaki 'daya ajin suka fa'da yayi kyau "I just have to guide u kunmin aikin" suka saka dariya gabaki 'daya.

Daurewa kawai yake ji yake like 'kafafunsa bazasu iya supporting 'dinsa ba dole in nemo ma kaina mafita ya fa'da.

Kamar yadda na fa'da muku banji da'di ba kwanakin baya sabida haka bazan iya tsaiwa na 2 hours anan ba inaganin zan koma baya zanyi anfani da microphone 'dinnan danku fi jina.

Captain ne ya mi'ke sir bari in samo maka kujera no kabarshi ga empty sit can Anman sir se minfi ganewa in muna ganinka inji Aisha eyye but i might ended the two hours standing before this ur lazy lout captain find the sit for me, i just don't me kuka gani kuka zabeshi as ur captain but sir He is a hard worker fa inji wani student, oh I see shiyasa He can't stand for 30m ya gwammaci zama cikin mata pls let me go back before u just called me lazy teacher gabaki daya student 'din suka sa dariya.

Bayan ya gama lecturing student 'din ya fice at list ya'danji sanyi cikin ransa, yana fita wasu cikin 'yan iskan ajin ya mi'ke ai mu daman tuni muka gane dan Haka kai captain ka shirya zamu sayo ma zani da hijabi ka koma 'daurawa, babawo ya mi'ke ai se aha'do dana malan inda yai dedai da shigowar Abbakar dan 'daukan takardun daya mance oh abie ya fa'da se asayon me kyau, yabar ajin be jirayi amsarsu ba. Gabaki daya ajin suka sa musu dariya ganin yadda suka tsure.

Yau kimanin sati hu'du kenan Abbakar bega Ummu a class 'dinsa ba ada zatonsa da tunaninsa inbaya ganinta santa da kullin ke ruruwa a zuciyarsa zai ragu sedai rashin ganinta na 'yan kwanakinnan ya dameshi tunaninsa kullin me yasa bata zuwa.

Kota mutu ne ya fa'da no she won't die in ta mutu am dying too but she belong to some one zuciyarsa ta fada masa Ya'ilahi save me out of this.

Ashe sani ne beba 'dan ganinta da yake ba 'karamin 'debe masa kewa yake ba gashi khairiyya Facebook friend 'dunsa bata online sati biyu kenan ko wayarta ya kira bata shiga gabaki 'daya duniyar tai masa zafi ya rasa wazai fa'dama damuwarsa yaji da'di.

Hello wai kana ina ne gani a gidanku Hajiya tace yanzu ka fita mahfuz ne ya kirashi, No ban fitaba in garden ok ganinan yana zaune yaji anyi sama da littafin da yake dubawa na lecture da zaiyi gobe mtss yai tsaki wai kai mahfuz yaushe zaka girma ne bakamin sallama to al'uztaz Assalamu alaikum ya amsa ga guri.

Kasan Allah banyi zaton ganinka yanzu ba mahfuz ya'dan 6ata rai eyye wato ban isa inzo gunka ba kenan No ba haka bane kawai ina tuna rabuwarmu ta baya ne mtsss matsala ta dakai ru'kon tsiya inji mahfuz pls forget that's was bygone .

Pls Abbakar kafa'dan gaskiya me ke damunka jibi duk ka rame ka kuma yin ba'ki, me kuwa zai da men banda abunka mahfuz kasan munsha strike kullin ina gida yanzu ankoma kullun kana tafe ga hayaniyar student dole in 'dan rame kafin jikina yasaba.

No Abbakar kark layance min mana look at how u are turning to skeleton bawai fa ramewa kawai ka'danyi ba kamar yadda kake fa'de yasa dariya kaifa 'dan iskane mahfuz wato ni ne skeleton 'dinma no bance kai bane nadai ce kana komawa am ok nothing is wrong inji Abbakar.

Any way what's the urgent call for eyye lallai mutumin wato ma tambaya kake to sarkin mita calm down ba haka nake nufiba kawai dai nasan me zakace maganar kwanaki ce kai wallahi kafi matsala that's was bygone pls learn to forget mana ok ya wuce.

Yanzu dai bazaka fadan meke daminka ba ko mahfuz ya tambaya oh my Goodness aikaima kasan mahfuz duk duniya babu wanda yasanni ciki da bai kamarka inda akwai matsalar kasan before hajiya taji kaine zakaji bazan 6oye maba.

Ni wallahi matsala ce babba ta taso min inji mahfuz subhanallahi matsala inji Abbakar eh wallahi mahfuz ya fa'da.

Am in love mahfuz ya fa'da cikin muryar tausayi dariya 😂Abbakar yasa kai malan karka bada maza mana being in love isn't problem malan inji Abbakar mtsss mahfuz yaja tsaki kai ana kaika kana tirjewa matsalar shi ne wadda nake so 'din to wace kuwa wannan mesa'ar.

Bafa kowa bace face Ummulkhairi wannan cousin 'din tawa what Abbakar ya fa'di yana zare ido alamar firgici.
[12/31/2020, 5:45 PM] 🅰 " AXEEX✌🏻 D'🅱🅾Y😎: _POST BY GROUP OF HYPE HAUSA NOVELS BOOK WHATSAPP 08064400100_ 📚📚
[12/31/2020, 5:46 PM] 🅰 " AXEEX✌🏻 D'🅱🅾Y😎: *ABBAKAR*

*16---20*

Wai khairiyya dai dakai ta bani labarinta ehfa ita wadda tai sanadin fa'danmu kwanaki ta You must be joking abbakar ya fa'da wallahi Ba wasa nake ba I mean my words.

Anman kaima ka cika tarar aradu da ka how do u think zata so ka Abbakar nasani nima ba lallai tasoni ba nasani zan iya zama mutun na farko da duk duniya ta tsana sedai ba lefi na bane kullin innai 'ko'karin mantawa da ita se abin yaci tura kai nifa kamar 'karan santa ake, Abbakar yai 'dan murmushi irin na tausayawa natausaya ma anman kasan mene alhakinta ke 'dawainiya dakai Yanzu abinda zaka ce kenan nagode no ai gaskiya ce nasan kuma kasani sedai kasallama.

To yanzu kai sa'ace kasan inda take yanzu se kaje kace kanasanta me zai hana shi yasa ma nazo dan ka temakan in nemota dan in convincing 'dinta ta yadda ta aureni hhhhh lallai mutumina ka kamu da yawa inji Abbakar kasan Allah inkana dariyar nan mugun haushinka nakeji inbazaka temakanba ne ka fa'dan.

Kafin Abbakar yace wani abu wayarshi tayi qara da sauri Mahfuz ya le'ka to sarkin gulma kalli da kyau sukai dariya tare sallama ya Amsa gami da fa'din lafiya lau 'kanwata ya gida ya kike sun 'dan ta6a fira kafin suyi sallama.

Daman nafa'da u are in love fa'dan ne bazakayi wato baka yadda dani ba shiyasa bakasan fa'dan sirrinka oh my goodnes kanada matsala wallahi .

Wayarsa ya 'dauka ya kira khairiya bata wani yi ringing da yawa ba ta dauka hello qanwata na'am Yayana lafiya dai yanzu mun gama waya ka kuma kira wannan abokin nawa ne da nake baki labari yakesan magana dake wai yana fa'din muna datin junanmu ne tai dariya baka fa'da masa kaine ma'daurin aurena ba gashi ki fa'da masa dakanki.

Sun gaisa da mahfuz kafin tace abokin yayana be fa'da ma inada miji bane yai dariya taya zai fa'dan to gashi ku gaisa kafin yace wani abu yaji muryar namiji ya amsa suka gaisa ai kullin inajin labarinka gun Khairi se yau Allah yai zamu gaisa mahfuz yace bama Abbakar 'din bane abokinsa ne oh to bashi mu gaisa sun gaisa ya kashe wayar batare da baima khairiyyan ba.

Hope u are now convince yai dariya sosai ma, kaga daga yanzu nagane wallahi u don't trust ne inji Abbakar harfa rantsewa kake eh wallahi inma ka yadda dani not like I trusted u, for me u don't have to prove what u said is gaskiya ko qarya, what I need na yadda shine kawai kace 'din in yadda.

Am sorry nima ai bance dole se ka kirata ba impact ma bani nace ka kirata ba mtss kaji dashi yamiqe yai cikin gida.

Gabaki daya abun duniya ya ishi Abbakar dan ya rasa wazai fa'dama abinda ke damunsa gashi 'dan ganin ummun da yake ma ya dena kwata kwata.

Yau yana zaune gabaki 'daya duniyar ta masa zafi yarasa me zaiyi kamar daga sama idea tazo masa ya miqe yana murmuahi nasan me zanyi.

Wayarsa ya duba kaf babu number 'din da yake nema can ya tuna a littafin da ya rubuta ya'dauko ya kira ringing 'daya ya 'daga.

Daga 'daya bangaren aka yi sallama ya amsa yawwa ina magana da mas'ud ne eh aka bada amsa to ka fasanar da class members 'dinka ranar litinin zanyi C.A 'dina kana magana da Abbakar muhammad Abbakar ok sir nagane zan sanar dasu ya kashe wayar.

Shi ka'dai yasan dalilin yin hakan ada be ma da niyar yin test 'din a 'yan kwanakinnan.

Wallahi Aisha narasa yazanyi kinsan monday mutumin nan zaiyi test gashi Ummu bata da lafiya nasan kuma in nayi mata zai iya ganowa tunda yasan sunanta kumafa haka ne.

Mas'ud yace kawai kuzo muje office 'dinsa inyaso se mu masa bayani in anyi sa'a in taji sauqi in yaso Allah se ya mata
Ni wallahi tsoronsa nake inji fatima daurewa zakiyi muje yazanyi haka zani ai.

Sunyi sa'a kuwa yananan bayan sunyi nocking yace su shigo suka kuwa shiga da sallamarsu, sun gaisheshi kafin captain yace daman sir game da test 'din dakace zakayi ne ok wata matsala ta farune ya fa'da yana duba takaddunsa a'a daman daya daga cikin student dince lafiya shine mukazo mu fa'da ma ko in taji sai'ki za'a mata make up.

Wace kenan Ummulkhairi muhammad Dalhat saida gabansa ya'dan kafin yace meke damunta eh daman an mata CS ne tazo haihuwa a'dan ratsane ya 'dago what cs ya fa'da ayanayin dashi kansa besan sanda ya shiga ba eh ok Allah ya bata lafiya suka amsa da amin.

Ungonan ya miqo paper rubutan sunanta da registration number 'dinta ok sir gashi na rubuta to intaji sau'ki sai tazo ta sameni ta tawo da shaida 'din tabbas bata da lafiya ok to sir mungode suka fuce.

Hankalinsa gabaki 'daya ya tashi tausayinta duk ya kamashi ashe Aiki akai mata yadda ya damu wani 6arin na zuciyarsa ke fa'da masa matar wani ce fa kake damuwa akanta subhanallahi ya fa'da yai saurin miqewa ya shige toilet.
[12/31/2020, 5:46 PM] 🅰️ " AXEEX✌🏼 D'🅱️🅾️Y😎: _POST BY GROUP OF HYPE HAUSA NOVELS BOOK WHATSAPP 08064400100_ 📚📚
[12/31/2020, 5:49 PM] 🅰️ " AXEEX✌🏼 D'🅱️🅾️Y😎: *ABBAKAR*

*PAGE 20---30*

Miqewa yai ya shiga toilet ya dauro alwala yazo ya alwala gabaki daya yarasa abunyi hakan yasa shi tada sallah ko Allah zaisa yadanji sanyi cikin ransa.

Saida yai azahar sannan yabar office din bayan ya gama nemawa Ummu sauqi da datan Allah ya raya abinda ta haifa.

Yunwa yakeji sosai hakan yasashi wucewa gida duda a yan kwanakinnan be cika san zama cikin jama'a ba.

Da maryam qanwarsa yaci karo a farfajiyar gidan tana baima Habu me tuqi saqon ta qara fada da murmushin fuakarta yah sannu da zuwa shima ya amsa yana dariya yawwa gami da shaqar numfashi hmmm qanwar me ake dafa mana ne wani abin dadi ne kamar kinsan yunwa nakeji aikuwa dai sha kuruminka yanzu cikinka zai cika yabi bayanta batare da yace komaiba.

Pls qanwar ki fadan me kike dafa mana ne kaidai kawai kabari azubu ta shige madafa yabi ta kitchen din zai leqa tukunyar pls yaya to sanmin kar qamshi ya qosar dani ta dan debo miyar a ludayi ta bashi yana kaiwa baki yasaki wata qara gami da cillar da ludayin.

Tai saurin matsowa daf dashi yah lafiya ya dago ya galla mata hara anman ke muguwa ce wallahi kinsan da zafi zaki bani tasa dariya kai yaya anman kai ragone wallahi ni nadauka wani abune ashema dan zafinnan ne zaka wani saka ihoo au dariya ma kike to anma fasa cin abincin naki danma inai miki kara ina cewa kin iya girki to ki sani ba abinda kika iya fuuu ya fice daga madafar ta ci gaba da dariyarta.

Saida ya watsa ruwa yaji dagaske yunwa yakeji gashi qamshin abincin ya cika masa hanci ya sauko daga sama yai sa'a bata falon sai hajiya.

Kai tsaye dinning area ya wuce ya debo a plate yai sama hajiya tace ina zuwa inazuwa hajiya bari inkai daki kar wannan mara kunyar ta ganni hajiya tasa dariya kwaji dashi.

Saida yakai matattakala ta biyar yajiyota tana dariya ahab ashedai na iya abincin tunda har yasamu matsayin akaishi daki aboye mtss ya saki tsaki anma fasa ci yazo ya dire eh ya qara afki au haka kika ce to sema naci.

Yq haukan kujera ya fara zubawa ai yarinya da dakudinki kika siya to bazanci ba eh anman ni na dafa abinda bama dadi ci karka mutu ne fa yana fade yana yamitsa fuska ya turawa abaki kamar anai masa dole eh shiyasa naga anata saka loma.

Hajiya innaje masallaci bazan dawo da wuriba zan biya ta gidansu mahfuz karkiga nayi dare ok inka dawo nayi bacci katashi maryam ta shiga daki katabbatar dik sun rufe dakunansu ok hajiya.

Yau ya yanke shawarar samun mahfuz ya fada masa komai ko yaji sanyi aransa dan zatonsa rashin fadawa kowa da barin komi cikin ransa yasa abin ke damunsa sosai.

Yaje gidansu mahfuz sun dan gaggaisa da mutan gidan dan gidan yawane mahfuz baya dakinsa hakan yasa ya zauna a farfajiyar gidan suna fira da mamar mahfuz din ya tura ummi ta kira masa shi danshi bashi da al'adar zuwa gidan yai ta shige shige tun yana yaroma balle

yanzu duda ba inda aka masa katanga da shiga.

Maman maufuz tace kudai zanga lokacin da zakuyi hankali yasan kwanan zancen dan haka yai shuru ace kuduk qannenku sunyi aure ku godai godai daku kunkasa sai yawo kuke waiku samari bakusan kun tasanma zana tuzurai ba ta sosa qeya aishi hajiya sure lokacine eh haka kullin kuke cewa mahfuz yafito riqe da yaro ya miqawa hajiya kai kana da matsala ace kai bazaka taba zama dan gida ba Tashi muje sukai bangaren mazan gidan.

Sun dan taba fira kafin mahfuz yace nasan da magana shi dan haka kawai bazan ganka da daddareba kaidai bari inji Abbakar ina cikin matsala.

Mahfuz ya zaro ido matsala eh wallahi am in love mahfuz yasa dariya kaji wai matsala love isn't a problem malan wace me sa'a ce haka student dina ce and she is married with baby mafa what mahfuz ya fada.

Taya haka ta kasance zakayi kuskuren kamuwa dasan matar aure nima bansani bafa sedaga baya subhanallahi da matsala babbama inji Abbakar kullin wallahi kamar qaran santa ake a zuciyata narasa meke min dadi.

Inada mafita Abbakar yace mafita kamarya kace she is ur student eh and kasan students can do anything to pass there exam kayi anfani da wannan daman ta zama secret wife inka what me kake nufi nasan ka gane ka nuna mata if bata yadda dakaiba she is failing ur course kawai yaja tsaki wannan ai ba mafita bace shirmene.

Cemaka nai inasanta bawai ina sha'awarta ba and i wanted us to be together for the rest of our life not for wani lokaci kayadda dani once ka sameta zakaji abinda ke daminka aranka aqalla rabi ya ragu ko kuma ta qaruba yaja tsaki koda banyi shashanci ba sai yanzu da girma ya kamani ya fice daga dakin afusace.

Zaune yake yana marking test din daya yi aka kwankwasa kofar yace yes shigo ta shigo da sallamarta ummu ce ya fada dan ko cikin mata dari yaji muryarta sai ya ganeta .

Ita dince kuwa tai masa kyau sosai kana ganinta kasan me danyen jego ce nan da nan shaidan yafara qawata masa ita maganar mahfuz ta fara dawo masa .

Bangaren zuciyarsa ya fara fada nasa yes maganar mahfuz is the only solution to ur proble this is the best chance tazo dan test ne kayi anfani dahakan wani barin na fadin no karkayi .

This is the best chance and the right time ya fada ya miqe yai inda take atsaye itakuwa sai baza ido take yayin da zuciyarsa ke bugawa anya kuwa dedai ne hakan ya fada but this is the only solution u have if not ka mutu da ciwon santa ganin yazo dab da ita yasata faduwar gabanta yq qara qaruwa..........

Jiyai kamar an tsikareshi yai saurin cewa muje wajeko tai saurin budewa dan gabaki daya jikinta rawa yake Time in sallah yayi so u come back letter tace ok sir shi kuma yai C.mosque.

Acan masallaci yai sallarsa ya roqi Allah gafara na yunqurin saba masa dayai ya kuma gode masa da yasa bai saba masanba.

Tabbas yanasan Ummu so bana wasaba saidai yasan tai masa nisa ya rasa me yasa duk yadda yaso ya cireta aransa yake kasa wa yarasa wane irin so yake mata.

Wayarsa ce tai qara hakan ya dawo dashi daga dogon tunanin da ya fada ya kai duba kan screen din wayar Qanwata yagani yai murmushi khairiyya ce frnd dinsa ta facebook ya kai hannu zaidauka kiran ya tsinke yabi bayan kiran.

Da sallamarta ta Amsa shima ya amsa mata qorafunta ya biyo baya yanzu yah na ka kyauta kenan kanaji ina kiranka kaqi dauka to sarkin qorafi nazo dauka ta katse ayimin afuwa tai dariya bakamin komi ba.

Yanzu abunda kike kina kyautawa kenan duk kin barni da tunaninki ta zaro ido kamar tana gabansa me menayi kyace me kika yi mana saiki kashe wayarki innemi in rasa yau wajen sati uku fa kenan ko a online bana ganinki tai dan murmushi amin afuwa haka kullin kike cewa wallahi ba ina sane na kasheba wayarce ta sami matsala aishikenan ya wuce suka dan taba fira kafin suyi sallama.

Ya kashe yana murmushi yasani yanasan Ummu wanda be taba yina wata mace shiba sedai yasani ya yi trusting din khairiyya fiye da kowacce mace yasani aduniya in aka dauke ummansa sai maryam qanwarsa babu wata mace da yake sakewa yayi fira da wasa da dariya kamar khairiyya duda kuwa betaba ganinta ba.

Asannu a hankali tunaninsa ya fara sauyawa kanasan ummu anman ka yadda da khairiyya har kana iya sakewa da ita why not ka mata tayin soyayya inyaso kayi aure ko ka rabu da san ummu ya aminta da zuciyarsa but dole se yaga khairiyya before yai gabatar mata da abunda ke ransa yasan duk duniya babu abinda ta gijini kamar ya nemi su hadu anman yanzu dole ta yadda if not zai yanke alaqarsu.

Ummu ke zaune tana kallo ya shigo da baby a hannunsa ungoshi kuka yake ta karba tana dariya Allah yaya kana shagwabashi infa ka tafi ya dinga kuka kenan sai zainab ta daukeshi tai masa rawa kasan ni ba iyawa naiba ace kaita jijjiga yaro sai kace wata yar tsana.

Yai dariya to banda abinki inban jijjigashi ba wa kikeso injijjga kinsan kuwa yadda nakesansa tai dariya ai basai ka fada ba kowa yasan baba nasan dansa to ni nawa san da nakema nawa dan yafi na kowanne baba harke mamarsa suka saka dariya gabaki daya.

Mutumina ya kaji shawarar tawa kuwa tayu ko yai tsaki wace shawara kuma au har kamance eh

tunamin kan yarinyar da kake so mana yaja tsaki shawara ko cuta Allah mahfuz baka sona inda kana sona bazaka bani shawarar indauki qafata da kaina inkai jahannama.

Kagani tunda kaga zaka iya jurewa aishikenan ni kaban shawara wallahi bana iya bacci kullun da tunanin cousin dinnan tawa dashi nake tashi kai ko ni daya na zauna ita kawai nake hangowa haquri zakai matarma dabu san inda takeba balle kawai kaita addu'a Allah ya yaye maka.

Hawaye suka biyo kuncinsa Abbakar kafadamin taya zan iya haqurin wallahi ni asan khairar bansan wani abu waishi haquriba kafadan yazanyi inba haka ba wallahi santa zai iya hallakani a kwanannan.

Uhum mahfuz kenan kadunga saka dangana a'al'amranka wallahi nasan abinda kakeji aranka bekai nawaba kawai nafika haqurine kadena sama ranka komai kakeso zaka samu in kuma mutuwa taifa.

Kadinga sama ranka ta mutune bakuma zata dawoba zakaji sassauci to Habu nagode zan gwada insha Allah yawwa nawan be a Man dan Allah.

Wayarsa yadauka ya kira Khairiyya sun gaisa kamar koyaushe be bari ta fara surutunnanta ba yace magana nakesan muyi me mahinmanci to yah na inajinka.

Wallahi ina cikin matsala inasan kiban shawara kamar yadda kika saba sai dai ba ta onkine ko through phone calk ba a'a inasan ganinki face to face tace what eh sai ta kashe wayar.

Saqo ya tura mata khairiyya nagaji da kullin sedai mudinga magana a waya ko through chat if baki yadda mun hadubu wallahi wannan shine qarshen alaqarmu bazan kuma kiranki ba and kuma bazan kuma daga kiranki ba and in facebook u will be out of my frnd list and I will soon block u in WhatsApp.

Har safe ba reply be kuma yi abinda yace ba.

Yashirya zashi aiki saqo ya shigo wayarsa yana dubawa nata ne ayi haquri abin be kai ga haka ba kasa kuma kwatancen gidansu ne but kazo ran Friday ko lahadi sauran ranaku inada sch yai murmushi yau talata Allah ya kaimu juma'ar.

Bayan ya dawo yaje gidansu mahfuz sunsha fira mahfuz din duk yai baqi saidai ba kamar randa yazo gunsaba ya dan ciko.

Kasan me ya kawoni zuwa nai infada na zaka rakani gidansu khairiyyar nan frnd dita ta Facebook ok yaushe gobe Allah ya kaimu yace amin.

Baisan me yasa yaketa rawar kafar zuwa ganinin khairiyyanba ji yake kamar zashi ganin ummu

ne rasa kayanma da zaisa yai qarshe ya nemo milk shadda dinsa mai dunkin coffee sai yasa hularsa ita kalar dunki da ratsi ratsin milk takalminsa coffee yai kyau sosai kai kace wani sabon ango ne.

Kamar sun hada baki shigar da mahfuz yai kenan dan yawancin kayansu iri dayane tun suna yara komai tare suke halinsu ne kawai ya ban banta.

Hajiya na ganinsu ta baro girginsu ah kace yau in sadaka nayi suruka suka hau sosa qeya bata tambayi ko ta wayeba ta musu fatan alkairi suka fice.

A qofar gidan suja faka motar suka fito Abbakar ya kirata tace gatanan.

Tai kyau sosai dan kaya ma na qasan kwaba tasa ko mace yar uwarta ce ta ganta saita yaba balle kuma namiji.

Alamar bude qofar gidan da suka ji yasasu gabaki daya maida hankalunsu kan qofar kowa da tunanin yadda zai ganta.

Gabaki daya sukai mutuwar tsaye daga su har ita da gudu ta koma cikin gidan tana kuka mahfuz na fadin Abbakar khairi ce yayin da Abbakar yarasa abinyi bakowa shi kuma idansa ya gane masa face kuma ummu dalibarsa ya riqe mahfuz wace khairin causing dintawa mana kasan me kake fade khairiyyace fa da nace ka rakoni gunta mahfuz ya zube agun sumamme inna lillahi wa'inna ilaihirraji'un kawai Abbakar yake fade.....
[12/31/2020, 5:49 PM] 🅰️ " AXEEX✌🏼 D'🅱️🅾️Y😎: _POST BY GROUP OF HYPE HAUSA NOVELS BOOK WHATSAPP 08064400100_ 📚📚
[12/31/2020, 5:50 PM] 🅰️ " AXEEX✌🏼 D'🅱️🅾️Y😎: *ABBAKAR*

*PAGE 30----40*

Ganin bashi da amsar tambayarasa yasa shi katse musu shirun nasu da fadin bari muje asibiti amaka dressing in ciwon da kaji naga kamar ma yana buqatar dunki ok kawai mahfuz yake dan yasan yanzu magana kadan zata iya sa shi fashe wa da kuka.

Adedai gurin Parker motoci na emergency na asibitin nasarawa Abbakar ya ajiye motar dan dare yayi yasan OPD yanzu ba doctor muje ko yace da mahfuz ya fito yana dingishi sukai ciki.

Kamar yadda Abbakar yaje har gida ya tawo da Mahfuz haka ya rakashi suka rabu kowa da abinda ke damunsa a rai.

Bacci ya qi zuwarwa idanun mahfuz gabaki daya tunaninsa yaushe ne yayansa yai aure shi be saniba.

Zumbur ya miqe yai area din da dakin yayyansu yake ahankula ya tura qofar kamar yadda ya

zata baya dakin dakin baccinsa ya shiga anman ga mamakinsa kwance yake kan gadon yana baccinsa cikin kwanciyar hankali to me hakan ke nufi.

Gabaki daya kansa ya kulle rasa me zaiyi yai abinda be saba ba ya mike ya dauro alwala ya hau nafilfilu.

Shima dai Abbakar kusan abu guda ne da mahfuz din ya kasa bacci saidai abu guda ke daminsa wato tausayin kansa yasani ayanzu san ummu ya gama kassarashi yasani santa bazai barshi ba duniyar yaji gabaki daya ta masa zafi kamar ya kashe kansa ya huta.

Hawayene kawai kebin idansa ya rasa shi kuwa wannan wace irin gaddara ce ta afka masa shi yasani yana kuma fade So be masa adalci ba ya mike yai toilet dan dauro alwala.

Washe gari da safe kamar yadda yake al'adar gidansu mahfuz an hadu a babban falo ana breakfast wasu na kan dinning tsoffi na kasa dansu sunfi san ci a qas juya cokali kawai mahfuz yake gami da baza idanu so yake kawai yaga ta ina yah nasir zai billo.

Baikai ga dire tunaninsa ba yaji muryar nasir din na fadin kai hajiya se kace wani yaro beji farkon maganar ba dan haka be fahinci abinda suke maganar akaiba.

Kamar yadda yake al'adar gidan koda da kwana mutun ya girmeka zaka gaidashi hakan yasa Mahfuz fadin Yah nasir ina kwana ya amsa lafiya qalau qanina yahau zubama kansa abincin.

Kusa da mahfuz din ya zauna yanaci yana nazarinsa saida yakai lomar qarshe kafin yace wai qanina meke damunka ne naga duk ka rame gashi ka rigani fitowa anman har na cinye na barka bakomi yaya kawai banajin dadi ne.

Ayya anman ai daurewa zakai kaci abincin seka sha maganin cuta da yunwa ai sai abin yai yawa to yaya zanci yawwa ko kaifa ya miqe zai bar wajen.

Yai saurin dawowa subhanallahi ciwon mene haka a qafarka mahfuz ya kalleshi da mamaki kamar bashine jiya ya ji masa shi ba.

Ina tambayarka ciwon me ne haka ta yaya ka jishi ya hqu sosa qeya gqnin yadda mutanen falon suka zuba masa na mujiya kowa nasan jin yadda akai faduwa nai jiya munje unguwa da Aminin sunan da mutanen gidan ke fadawa Abbakar Ayya to Allah ya kiyaye ya fuce.

Sama sama Abbakar yaci Abincin karinsa sauran ya faki Hajiyarsu yaje ya kaiwa kaji yana yo kwana daga gurin kajin nasu yaji dariyar maryam Allah ya kamaka wato kaji kake kawowa to abakun hajiya tai saurin juyawa zatai cikin gida.

Yabita da sauri yana roqonta haba yar qanwata ki tsaya kiji mana tai masa banza ganin tai falon hajiyar yasashi kai kwanon kitchen ya bita da sauri.

Haba qanwis bafa ma haka dake karaf kunnen hajiya zonan autana me yayi fadamin ta kalleshi duk yai wani kalar tausayi vashi bane nace ya temaka yaje yamin test yace ba inda zashi ya saukar da ajiyar zuciya dan yasan indai hajiya taji yaqi cin abinci ya gama yawo.

Hajiya tasa dariya kyaleshi kije kiyi abinki da kanki zaki ci fiye dashi kinji autana anman hajiya kedai kawai ki yadda dani zakici zan miki addu'a to hajiya ai shi kenan yawwa ko kefa Hajiya ni na tafi yace mata ok seka dawo Allah bada sa'a amin ya fice.

Yakai bakin gate a cikin motarsa yana shirin fita maryam ta fito da gudunta yaja ya tsaya ta tsaya bakin tagar me zaman banxa to sarkin rigima lafiya zaki tsaidani eh kace haka mana I save u today dole kabani tukwici ko in fada mata ai daman nasan da biyu ya ciro kudi ya miqa mata ta karba tana dariya shima ya kada kai yana dariya.

Inba dan dole ba da ba'abinda zai hanashi dena zuwa buk koyarwa tun da ya fara tuqin abinda ke faman kai kawo a ransa kenan har ya isa yai parking yai qofar office insa.

Kamar ance kalli gefe ya hango ummu riqe da babyn ta a hannu Fatima na gefenta suna ta dariyarsu cikin nishadi wani qululun takaici yazo masa wuya lallaima yarinyar nan ta rainashi wato shi ta gama raina masa hankali ita tana cikin farinciki da aurenta tana chat dashi tasa ya shaqu da ita rasa abinda ma zaiyi yai.

Jiyar Fatima na fadin lah Aminiyar yafazo dan bari ya dan jima da shiga kar yaga daga zuwansa min takura masa haka ne kuma.

Da sallama suka shiga office din ita da fatima suka gaisheshi a ciki ya amsa kafin yace lafiya me ya kawoku Daman make up din dakace zakamin kullin in nazo bakanan oh shine daga zuwana zakuzo ku takuran basu ce komi ba any way zan baki assignment kiyi submitting jibi but ki baima captain inku sai ya kawon ta amshi question in tana godiya suka fice.

Binsu yai da ido zuciyarsa na ayyana masa abu buwa da dama masu kyau da akasunsu yaja tsaki gami da diban kasan zuwa inda zaima wadanda yace suzo yau lecture.

Koda yaje ma ajin be iya tabuka komi ba ya rasa wannan wace irin masifa ce ya kawo lecture insa asabar dan duk sanin yan ajinsu ummu basa karatu week end akalla bazai ganta ba anman se ace yana shigowa ita zai fara gani.

Abu daya zakai zuciyarsa ke fada masa nigeria sa fadi take kawai ka nemi aiki a wani state in ka koma can wataqil ka huta da wannan takaicin jiyai yayi na'am da shararar ya miqe dan dauko paper a dara barin dan fara rubuta takardar neman aikin in ya tashi yakai amasa printing dan bezo da system inshi va bama yasan se yaje gida ya sauya ra'ayi......

Ko me ya tuna oho ya hau yayyaga paper din ya miqe yabar office din.

Abinda bai saba ba wato yawo cikin sch din shi yaji yana sha'awa tafe yake cikin nishadi ransa fes yakejinsa .

Daga nesa ya hango yarinyar da kema ummu raino haka kawai yaji yanasan ganin babyn ummun ya dan matso dab da inda yarinyar keta faman jijjiga yaron yace ki miqama mamanshi shi mana tana test ne ta fada ayya kawoshi to.

Tai saurin kuma ruqun qumeshi tace kar inbama kowa to ai ba guduwa zan dashi ba ta miqa masa shi sabida kwarjinin da yai mata bawai dan taso ba cikin ranta kuwa tsoron kar uwar dakin ta tazo tazo taga ta bawa wani ne.

Masha Allah ya fada a fili yayin da a ransa yake fatan inama ace yaronsa ne yaron kuwa ya bangale da dariya dimple insa me kyau ya bayyana yasunansa ya fada sunansa Mahfuz ya kuma mai maitawa mahfuh tace eh anman abbasa ke kiransa dashi ummansa tace sunan danta Abbakar wani abu ya ziyarci zuciyarsa yai saurin kawar da tunanin da fadin Allah ya raya shi tace amin ya miqa mata shi yabar gurin zuciyarsa cike da tunanin sunan yaron.

Abin duniya duk ya ishi mahfuz hakan yasashi shi yanke shawar zuwa yasamu yayansa nasir.

Yana zaune yana rubutu a system insa Mahfuz yashigo da sallamar Nasir ya amsa batare da ya dago kai ya kalleshi yaci gaba da abinda yake Yah gurinka nazo ok yace ya rufe system in ya maida hankalinsa gareshi.

Inajinka maganar me zamuyi akan matarka ne What ya fada mata ta kuma kai kamin auran yadda yawani hade gira yasa mahfuz shiga taitayinsa ina tambayarka kaikamin auran yai saurin cewa ba.....bame ba .

Daman kan ummu ne ta gidan baba yasir anganta ne ya fada a'a kwanaki ne daman mukaje gun wata nida Amin naga ashe tayi aure ta aureka.

Bai nuna wata razanaba ko tsoro yahau fada ni ta aura kuma sanin kanka ne banida aure bakuma ni da niyarsa ayan kwanakinnan se dai in har alhakinta ne yafara haukata ka kake zaton kowa ka gani ita ce yarinyar da ba'asan inda take ba ake zaton tabi uwatta shine zaka zo kana tunanun na aureta.

Wallahi yah ita nagani kuma wallahi yah kai nagani a matsayin mijinta ai ko na haukace naganka zan ganeka saukar marin da yaji yasashi saurin miqewa a firgice fitar min adaki da alamin ka haukace din da gaske sha_sha kawai.

Washe gari da sassafe yai dakin yayan nasa ya ganshi yana bacci yai sauri ya fice daga gidan sai gidan ummun.

Bugun da yake faman musu na hauka yasa gabaki daya suyo bakin gate in da abinda basu saba ji bane.

Daba dabaya ya fara ja ganin yayansa Nasir sanye da rigar bacci yana mittsika ido alamin baccin be isheba.

Shima mittsika idon ya fara kodai dagaske na haukace ne ya fadawa kansa no wallahi da hankali.

Malan lafiya mutumin ya fada nazo tafiya da qanwata ne abarsona what kanada hankali kuwa mata ta cefa ganin bazai bashi hanya ba yasa tankadashi ciki ya hau jan ummu tana tirjewa.

Mutumin ya dauko waya ya kira police sukai gaba da mahfux din yana faman kuru ruwar sai yadauki masoyiyarsa
[11/22/2017, 9:17 PM] Fadimafayau: *Abbakar*
*Na*
*F.A.Ya'u*
*Wattpad Fadimafayau*
*40-45*
Haka mahfuz yana ji yana gani police sukai gaba dashi yana faman ihuu tuni yan kallo suka cika gurin duda kasantuwar lokacin sassafe ne.

Saida mahfuz ya kwan ya yini a police station kafin asamu labari a gida dan hankalinsu gabaki daya ya gama tashi anata tunanin ko lafiya Nasir da hajiya ne suka fara zuwa aikuwa yana ganin nasir ya hau fada da zage zage mugu azzalumi wallahi saika saketa ya shaqe nasir dagyar aka fitar daga nasir din daga dakin.

Shine wallahi hajiya shine haka kawai yake fade.
Hajiya ta riqe mahfuz cikin kuka tana fadin shine mene yaci gaba da fade ta jijjagashi sosai kafin ya koma hayyacinsa ka nutsu kafadan me ya faru.

Hajiya tah nasir ne yai aure ta miqe a razane haba dannan ni na haifeku gabaki daya yaushe kuma nasir in yai aure ka fada min wallahi hajiya shine kuma Ummun baba yasir ya aura dan naganshi yasa aka daureni ka tabbatar da abinda kake fade eh umma.

Ta koma tazauna haba biri yai kama da mutun shi yasa yaronnan yake cewa haukacewa kayi muje ina zuwa ta fice tabar dan dakin da suke ganawar.

Tana zuwa ta share Nasir da mari ya dafe gurin cikin qwalla ya kalleta menayi hajiya bansaniba ashe kai shasha ne da har zakayi aure bamu sani ka rasa wa zaka aura se yarinyar nan wadda uwatta bata ganin kowa da qima.

Ya dafe qirji cikin kuka yake magana hajiya ke kin yadda ina da aure in inadashi ai da tuni na

dena kwana agida aje gidan da yace yaganni inyaso se agani inni inne tadan yi jim kafin ta koma dakin.

Mahfuz ta tambaya kwatancen gidan ya mata.

Eh kam yarinyar kamarsu daya da Ummu sedaifa yarinya tace ita ina batasan wani nasir ko mahfux ba har gidan iyayanta ta nuna mijinta ma ko kama basu hada Nasir ba police ma sun tabbatar ba nasir ne ya kawo mahfuz ba wanda yakawo mahfuz daban.

Aikoda su hajiya suka dawo da labarin komi Mahfuz ya miqe yahau dukan Nasir wallahi saina kasheka wallahi shine.

Ala dole su hajia suka yadda tabbas Mahfux ya haukace hakan yada sukayi bail insa suka kaishi asibitin kula da kwa kwalwa.

Duk wani bincike anyi anman ba'agano komi ba wato kwakwalwarsa normal take.

Saidai yadda inyaga Nasir yake tuburan dole hajiya naji na kallo ta yadda ya haukace tasa hannu dan kaishi gidan kula damasu tabin kwakwalwa.

Duk halun da ake ciki Abbakar baya da labari sai yau hankalinsa ya tashi danshi be yadda Mahfuz dinsa ya haukace ba.

Kai tsaye asibutun ya wuce aikuwa mahfuz din naganinsa yahau kuka tausayinsa ya cika Abbakar yadda kwana biyu kawai yaga mahfuz din duk yai baqi ya rame kamar bashi ba.

Ya hau rarrashinsa dan Allah amin kaje kacewa hajiya wallahi da hankalina Allah van haukace ba kai nasan zaka yadda.

Yadda yake maganar yaqarama Abbakar kwarin gwiwa tabbas Amininsa da hankakinsa wata maqirqisa kawai aka shirya masa.

Naji nayadda da hankali anman garin yaya me yafaru har aka kawoka nan ya bashi kabarin komi tabvas raina musu hankakin da yarinyar nan take ya isheshi yau zai maganin komi dan yanasan abokinsa yanaji yana gani baza'a mayar masa da Amini mahaukaci ba.

Ya kwantarma da Mahfuz hankali kafin yq fito daga gidan masu rangwamen hankalin.

Kai tsaye gidan Su mahfuz ya wuce baibi ta ko inaba yai bangaren hajiya abinda yake ba sabonsa ba shiga cikin falon gidan kai tsaye.

Yai sa'a tana falo suka gaisa kafin ya mata jaje ya dora da fadin yanzu hajiya kina kallo za'a maida mahfuz mara hankali vazakiyi magana ba.

Tai dan murmushi Habu kenan ai ba maidashi akaiba ya haukace din ne wallahi hajiya be haukace ba da hankalinsa haba dannan taya zakace be haukace ba mutumin da yake iqirarin kashe dan uwansa agabana fa.

Yana ihuuu yana shine ajalunsa yace yai aure alhalin qarya yake masa yace yaganshi alhalin bamashi bane bakajin wannan duk ba alamomin hauka bane.

Wallahi hajiya shi yagani tare muka ganshi taja tsaki daman ai abokin barawo barawo ina yabonka ashe kaima ka fara shan qwayar da yake sha nasan itace ta fara tamvayarsa inzaka tashi katafi to inkuma ansn zaka kwana sekayi tayi tamiqe tai sama dan wallahi kaima ban yadda dakaiba kar inje a afkamin.

Ya miqe yabar gidan takaici fal cikinsa.

Gidan da sukaje da mahfuz yai inda sukaga Nasir da ummun.

Yaro ya aika amasa sallama da me gidan yaron ya fito wai baya nan can saigata tafito.

Wake nemansa yai saurin dagowa daga daddanna wayar da yake dan ko a ina yaji muryarta sai ta gane nine ta fada.

Tace oh baya nan sedai inzaka jira ok va matsala yace ta koma ciki.

Ya kusa minti goma sha biyar mutumin ya parkee motarsa qofar gidan ga mamakin Abbakar ba Nasir vane anman yadan daurewa mamakinsa barka sannu ko yawwa kai kake nema na eh nine ok muje daga ciki ko suka shige.

Bayan ya shiga ya fito riqe da yaronnan da kodaga bacci Abbakar ya tashi saiya ganeshi dan tabbatar da abinda ke masa yawo arai na shakku yasashi miqa hannu kawoshi.

Ya amsheshi dadinsa da yaron kwai fara'a ya sunansa nahfuz yace ataqaice Allah sarki Allah ya rayashi amin yace ya miqo hannu ya amshe abinsa.

Nikam Kamar nasanka wataqil kwanaki dai munzo da abokina mahfuz oh naganeku kune yan iskannan masu shigarwa matan aure gidako yadan cige lebe dan yaji zafin kiransu da yan iska dayayi yaidai basar ehto koma me kakiramu ni ba hayaniya nazo ba nazone dan inasan yin magana dakai da matarka.

Ya miqe a fusace what dan mene inbazaka iyayi dani kadaiba to mata tata haramin alaik no maganece ta fahinta nakeso muyi kan abokina da kuka haukatar.

Kaga nafiskanci haka daikinyi pls tashi kabar min gida tun kan kadaga hankalin matata pls give

me a chance wai baka ji me nace maka bane ko sai na hadaka da police na sassauta maka ne dan kawai na fiskanci kafi abokinka kamala.

Abbakar ya miqe yabar falon but kasani zan dawo kuma time in da zan dawo dole in magana da matar taka hakan kuma shi zai kawo qarshen matsalar nan na fada ma to muza nidakai dan halak ka fasa inji mijin nata.

Tunda yahau titi tunanin muhawarsu da mutumin yake yasan babu ta yadda zai iya magana da matarnan indai mutumin nan nanan but za'a iya kamashi inyaje ya shigar musu gida suka masa ihuuu gabaki daya tunaninsa a cunkushe yake ya rasa mafita.

Sauri kawai yake ya tafi sch ko breakfast din kirki beba ya bar gida.

Ko a office ma jira yai kawai takwas tayi ya wuce inda zaiyi lecture dinsa ta morning bayan ya gama yace wadda aka kawon complain bata da lafiya tazo yau for her make up ya fice be jira amsar student dinsa ba.

Aikuwa kamar tare suke yana shiga ta shigo riqe da babyn ta yadan kalleta ya kalli babyn zaki iya zama tace taja tazauna yai saurin murda makullin office din gami da zareshi ya zura a aljihu jikinta ya dau rawa ta mike ta daka mata tsawa koma ki zauna kika ce tak kome ya faru dake ke kika jawo yado gabanta dab da ita tana kallonsa yana kalkonta yazauna har yana iya jiyo faduwar gabanta suka hada ido ya daka mata harara tai saurin kawai da kai..........
[12/31/2020, 5:50 PM] 🅰️ " AXEEX✌🏼 D'🅱️🅾️Y😎: _POST BY GROUP OF HYPE HAUSA NOVELS BOOK WHATSAPP 08064400100_ 📚📚
[12/31/2020, 5:51 PM] 🅰️ " AXEEX✌🏼 D'🅱️🅾️Y😎: *ABBAKAR*

*PAGE 45---60*

Cikin kuka take magana pls let me go I beg ur pardon dan Allah, mtss yaja tsaki au daman ke kinsan Allah ne da har zaki hada wani dashi munafuka kawai taisaurin dagowa hawayen da ya cika mata ido ya gangaro.

Inkinga kinbar office dinnan to Wallahi kin fadan ke wace taisaurin kallonsa yes kinmaji na rantse sir bangane ba all i know am ur student kawai nop ba wannan nake san sani ba ki fadan mene alaqarki da mahfuz, Ni dakuma Nasir ni bani da wata alaqa dakai balle su ok kin shirya ma kwana ananko.

Ya shige toilet ya dauro alwala gami da fitowa ya tada sallah bayan ya idarne yaci abinci ya miqo mata sauran inkinyi niya kyaci ya sa hannu ya amshe babyn hannunta ya koma inda sallayarsa ke shimfide ya kwanta gami da dora babyn kan cikinsa ya lumshe idonsa hankali ba qaramin tashi yaiba ganin la'asar na shirinyi dagaske bazai barta ta tafiba.

Wata irin yunwa takeji abinka da me jego but batasan cin abincinsa dan bata yadda dashi ba

yadda ta fuskanci yau din kamar a buge yake dan dazu da ya daka mata tsawa ta kalleshi taga idanunsa sun wani sauya launi batasan duk bacin rai bane kawai.

Dole in samu mafita naji zan fada ma alaqata dasu inkamin alqawarin barina in tafi ok inajinki ya fada batare da ya bude ido ba balle nuna concern innaji bayaninki ya gamsar dani mai zai hana inbarki ki tafi.

Mahfuz cousin dinane what ya fada gami da saurin bude ido ta gyada kai alamar da gaske take eh causin dina ne so Nasir fa ya fada.

Tai shiru oh baki shirya tafiya ba kenan ta kada kai cikin hawaye mijina ne ya miqe a tsorace sauran qiris babyn ya fadi ya tallafeshi mijinki ya fada eh ta fada oh i see.

Shiyasa kuka hada kai kedashi zaku haukatan aboki ko dan kawai san zuciyarku dan zalunci pls kabarni in tafi na amsa naka duk tambayoyinka dan Allah.

Naji zaki tafi but baki gama amsan tambayoyina ba baki fadan alaqarmu ba sir ni bamu da wata alaqa da kai banma sanka va sai a Bayero.

Karfa ki rainan hankali nasan me nake am 30 so kinga na fice kizo ki rainan hankali inkasa gano wa taya zakice baki sanniba bacin kinsan frnd dina if i can recall ke kika fara turon frnd requires sai yanxu na gane hakan duk yana cikin shirinku ne keda Nasir.

Sir kayadda dani bansanka ba eh naji baki sanni ba anman taya za'ai da aurenki ki dinga chat da wani harki dinga baima mijinki ku gaisa da wanin inbaya shirinku.

Sir in zaka tuna time in four years back muna chat but inka tuna bama na nigeria muna waya da kai inka tuna na fada ma i never being to Nigeria even though my Father's relative gaba daya suna nigeria na turo ma frnd requires ne dan kawai inasan yan nigeria naga kai dan nigeria ne.

Yai dan tsai yana tunani yes yatuna ok yanxu zamuje ki fadama iyayen mahfuz abokina da hankalinsa kafin inbarki ki tafi ta zaro ido what eh.

Hawaye ya gangaro mata haba sir ba haka mukai dakai ba pls let me go kazamto me cika alqawari any way zaki iya tafiya yabude mata office din gami da bata baby ta wuce.

Harta fita ta dawo sir make up test in tawa yaja tsaki pls sir tace kafin yace wani abu jeki i will think about it dan Allah sir ta kuma fade yaja tsaki gami da fadin oppps kije during exam ki amsa all question in yaso se kisa C.A a biyun zan gane thank you sir ta fada tai saurin ficewa.

Wayarsa ya dauko ya danna recording din da yai nasu yana kuma sauraro at list yasamu evidence against ita da nasir dole yai wani abu he yas to expose them dan kare martabar abokinsa.

Miqewar dazaiyi wayar ta fadi jiyai har cikin ransa faduwar wayar yaisaurin daukowa yai yai ta kunnu taqi oh my goodness ya fada yana dan dukan goshinsa memory din ya ciro yasa ada wayar sedai ba recording shedar yana kan wayar ya Allah ya fada gami da komawa ya zauna wani hawayen baqin ciki ya gangaro masa ya rafka uban tagumi yana tunanin abinyi.........

Koda ummu ta fita daga office din kai tsaye ficewa tai daga sch din saida ta hau dan sahu sannan ta dauko wayarta tafara dialling din number din Aisha yafi sau hudu bata dauka va kawai sai ta kira Fatima ita ma same thing happen kawai sai ta zura wayarta a jaka.

Saida taje gida sannan kiran Aisha ya shigi lafiya dai irin wannan kira haka bata bata amsa ba ta kuma tambayarta kina ina ne ke muke jira fa.

Tun dazufa nake nemanku ban gankuba shine na tafi gida nakirama in ce muku na tafi gida se mun hadu gobe tsaki Aisha taja Fatima tai sautin karbar wayar cikin fada take magana anman wallahi ummu bakida muntuci inba rashin mutunci ba kinsan bazamu tafi ba sai mun jiraki kawai saikiyi tafiyarki ayi hakuri naga tun wajen fitowa ta banganku ba kofa office din ban shiga ba kutt bakishiga ba kika ce muna kallonki fa kika shiga munfi awa biyu baki fitoba.

Ganin yadda Fatima ke fada yasa Aisha karbar wayar haba ummu taya zaki mana hk tsaya ma naji fatima tana cewa wai kince ko office din baki shiga ba No bata fahince ni bane kinsan ta da fushi inta hau bata tsayawa cin ribar zance zata hau fada.

Cewa nayi ina shiga na fito fa baku dai kula bane ni kuma banyi zaton kuna nanba natafi masallaci nemanku da banganku ba na tafi gida anya ummu idanuna fa nakan office din kinsan dai karatu mukazo ko bataji komi kan maganar Aishan ba dan tasan ta da tsantseni da fadar gaskiya gama kowaye .

Ki yadda dani abinda yakaini kawai nayi banmayi make up dinba cewa yayi in answering all question 2 for test in yaso 3 for exam ok yayi kyau yanxu kina ina ina gida ki yadda ina gida bakomi ki shafan kan Abbakar zaiji insa Allah sukayi sallama.

Ta goge hawayen da ya zubo mata wani dacin rai na taso mata tarasa me ke mata dadi ji take inama batazo duniya ba ko inama ta mutu kafin a haifeta.

Gidansu mahfuz

Hajiya wai bakya ganin haqqin ummulkhairi ke dawainiya da dangin nan namu musanman nahfuz taja tsaki me muka mata da haqainta zai dawai niyada mu eyye mara mutunci.

Gani naifa yah mahfuz ya haukace gashi an kasa gano me ke damunsa Hajiya tai shiru kin tunan wani abu nasan tabbas da sahannun uwar yarinyar nan a abinda ya same shi sai yanzu na fuskanta aljanu suka turo masa suka masa farraqu da dan uwansa maza kiramin doctor

yusif.

Yawwa Doctor so nake mahfuz ya dawo gida mu gwada ruqiyya tunda naga na asibitin ba sauqi kinsan nayi tunanin haka aqwada ruqiyya hakan za'ayi.

Kiramin musa ummi ta miqe saigata ta dawo da musa yana biye da ita ya russina ya gaida hajiya gami da cewa gani.

Yawwa musa so nake kaje kadauko min mahfuz a asibiti yadan fada da razana hajiya mahfuz eh shi so nake ya dawo gida mu masa na gida tunda na asibitin yaqi.

Hajiya ya warkene ya fada cikin rawar murya inda ya warke ai dabazance ma zamu masa maganin gargajiya ba ko.

Jikinsa ta hai kyatma anman hajiya taya zan iya tawo dashi cikin sauqi ina tuqi to me kake nufi yai zuru zuru da ido ummi yasa dariya wallahi hajiya da gaskiyarsa taya zai dauko mahaukaci a mota shi daya wanda yake cewa zai kashe mutane kawai ya shaqeshi.

Hajiya ta cilla mata daquwa ungonan dan uwan naki ne mahaukaci to hajiya aiba qarya akaiba ok to naji ku tafi tare sai ki riqe masa shi ta zaro ido hajiya ni eh ke inkuma bazaki ba to kinsan ba ke daya na haifa ba tasan indai hajiya ta fadi haka to taki qololuwar jin haushi.

Ta miqe muje ta hau sama ta dauko gyalenta hajiya mun tafi Allah ya kiyaye tace amin.

Tunda suka fara tafiya ba wanda yacewa kowa ci kanka kowa zulluminsa taya iya tafiya da mahaukaci cikin mota.

Koda suka isa sunje office din doctor usif sunyi cike cike kafina abasu mahfuz, yadda ummi ta ganshi ya daga mata hankali dan mahaukaci sak tagani ya tara uwar suma da gemu wanda dauda har tafara sawa ya koma jaja.

Koda ummi taje dab dashi amai ne kawai batai ba sabida wani tsamin dauda da yake tace yah mahfux ka gane ni ya kalleta ba ummi bace tadanyi ajiyar zuciya aqallah ya ganeta.

Lafiya me ya kawoki nazo mutafi ne nine nace miki inasan mu tafi yadda yake magana cikin fushi da fada ya tsorata ta a'a to ba inda zani pls yah kinga alamar wasa a idona.

Ni nariga na yanke shawar qare rayuwata anan dan haka zaki iya tafiya yah kayi haquri kazo mu tafi kowa na kewarka qarya kike kowa yafisan Nasir gashinan sabida shi kowa ya mance dani kowa ya tsaneni kowa ya gujeni.

Cikin sauri tace yah kayi haquri inkasa wa ranka kowa ya tsaneka ka cire hajiya tanasanka kullin burunta kasamu sauqi pls kazo mu tafi kodan hajiya.

Miqewa yai yabi bayansu ummi ta fara yadda da batun hajiya anwa mahfuz da Nasir farraqu tunda gashi har yasama ransa anfi san nasir duda yana cikin hauka.

Suna tafe tana kaf kaf dashi cikin mota dan tsoronta karya shaqo me tuqi ko ya bude ya fice yana fiskantar ta sosai kasantuwarsa bayan yai degree dinsa a fanni qere qere yaje yayi wani sabon degree din a psychology baisan sanda dariya ta kufce masa ba aikuwa gabaki dayansu ummi da musa hankalinsu ya qara tashi fuskantar haka ne yasa shi yin shiru.

Agida ma kowa kaf kaf yadingayi dashi har suka isa sashen hajiya sai asannan ummi ta saki sanyayyar ajiyar zuciya aqallah sunzo lafiya.

Baibi ta kan kowa ba ya shige
bangarensu toilet ya shige ruwa me dumi ya hada yai wanka ya wanje jikinsa yakai sau goma still bedana jin wani iri ba haqura yai ya daura towel ya hau shaving din gemun ya rarrage sumar kansa sannan ya sake wanka aqalla yadanji dadi.

Ya fito yana saka kaya ne hajiya ta shigo riqe da kofi ummi na biye da ita da flask gabaki daya sunyi mamaki mahfuz ya koma mutun sak hajiya tazauna gefen gadon ummi ta zauna gefen kujera.

Saida ya kammala sakayan yazo ya gaida hajiya aqallah ta danji dadin ganinsa yanzu va kamar dazu ba ga tea kasha ko zakaji dadin cikinka ga danwake kuma sekaci yunwa yakeji hakan yasa be musa ba ya amsa yasha.

Yanasan dan wake sosai hakan yasa ya karba da zumudi yahauci saidai taunar farko yaji ba dadi dan gabaki daya bakinsa ba dadi dagyar ya hadi a hankula ya furta Allah ya isa Nasir hankalin hajiya ya tashi tadai daure.

Ganin ya ijiye yaqi ci ne ta kalleshi kadaure ka ci hajiya wallahi ba test daurewa zakayi kaci se ahankula komi zai koma normal.

Ummi kije ki samo toka ki gasa masa nama da ita zai temakawa test din bakinsa to hajiya.

Da yamma agun cin abinci kowa ya hallara har mahfuz inka dauke Nasir mahfuz yakai lomar abinci baki kenan nasir yazo yaja kujera ya zauna kamar koyaushe kujerarsa kusata da ta mahfuz ya sha kansa qanina yajikin naka ya tankade hannunsa cema akayi banda lafiya ne ya miqe fuuu yabar gurin.

Koda Abbakar yabar office din gida ya wuce dan gabaki daya ransa ya baci yama rasa abinyi.

Da Amira qanwarsa ya ci karo zata fita tace lah yah sannu da zuwa ya amsa yawwa ina zuwa haka da yamma yah zani gidansu khairiyya ne zamu dan tattauna yai dariya zadai asha gulma

tai dariya wallahi yah ba haka ne kyaji dashi se an dawo yai ciki be jira amsarta ba.

Gabaki daya mutan gidan na falo har masu aiki shima anan ya zauna bayan ya gaida hajiya yasa baki cikin firar da suke hakan ya rage masa kashi arba'in na bacin ran dake damunsa.

Kiran sallahr magariba ce ta tashi kowa dan kawo farilla ya kai kayansa samansa kafin ya daura alwala ya fice.

Daga masallaci gidansu mahfuz ya wuce baisan an dawo da mahfux dinba ganinsa ba qaramin dadi ya masa ba sun tattauna kafin suyi sallama har ya fita ya dawo.

Ban fada ma ba wani abin takaici nan ya zayyana masa komi cikin takaici Abbakar ke bashi labarin mahfuz ya goge hawayen da yazo masa ba komai Aminin Allah ya kawon mafita amin Abbakar yace.

Kasan me inji mahfuz sai kafada Abbakar ya fadi ni wallahi bawai gidan mahaukata da aka kaini ne matsalata va babbar matsalata itace San ummu da kullun ke qaruwa cikin raina ko nayi yunqurin cireta araina abu kamar.

Yana daya daga abinda yasa nake jin haushin yah nasir da ya aureta ni wallahi yanxu ji nake da rashin ummu gwanda abanni in dawwama gidan mahaukatan.

Abbakar ya dafa shi se haquri taka qaddarar ce a haka uhun ba qaddarata bace nasani haqqine ke bibiyata tunda Allah ba azzalumin sarki bane yana sakawa wanda aka zalunta kadena sa haka aranka ka ci gaba da qoqarin mancewa da ita ni zan wuce kar hajiya taga na jima.

Yana barin inda mahfuz din yake ya share hawayensa wanda tun dazu suke san fitowa yana jarumtar riqesu shi kadai yasan azabar da yake ji na san dalibar nan tasa dauriya kawai yafi amin nasa.

Ashan gida ma bayan yaci abinci yaje gurin motsa jikinsa jiyai duk jikinsa ba kwari dakinsa ya shige ya rasa abinyi wayarsa ya dauko ya hau kunnawa ko Allah zaisa ta kama amman ina tace batasan zance ba tsaki yaja yahau gado ko Allah zaisa yadan samu bacci.

Baccinma gabaki daya yaqi zuwa daya rufe idanunsa ummu yake gani tana masa murmushinta da yake qara mata kyau agunsa yarasa wace irin zuciya gareshi me nacin tsiya da take jawo masa masifa kala kala ace dik yan matan dake sansa takasa kallonsu sai matar wani.

Ganin da gaske idanunsa basu shirya yin bacci ba yasa ya miqe yashige toilet dinsa ya dauro alwala ya hau nafil filun.

Yau lahadi ba inda Abbakar zaije hakan yasa ya fito babban falo dan yin fira ko zai samu ya raje kewar da ke damunsa.

Hira suke sosai inka ganshi bazaka taba cewa yana cikin damuwa ba danshi din akwaishi da jarumtar boye damuwa duk girmanta shi yasa ko hajiyarsa take cewa yana da zurfin ciki.

Yau litinin yanada kula da masu jarrabawa qarfe biyu hakan yasa tun asuba da yasamu bacci ya debeshi yai me isarsa dan ya dade be yi me dadin sa sai goma ya farka yai wanka sannan ya sauka danyin breakfast dinsa.

Bakowa a falon sai kwanukan abinci dake kan dining da alamu nashi ne kawai saida yaci sannan yaje dan gaida hajiyarsu.

Tana kishin kide tana tasbihi suka gaisa kafin yace hajiya mu zamu fita tadan gyara zama to Allah ya kiyaye ya tsare ya amsa da amin cikin jin dadi.

Gidansu mahfuz ya wuce sun dan taba fira da hajiyar sakamakon mahfuz din na wanka a hankula ya fara sako mata da maganar ummu aikuwa nan danan ta hau wato mun samu ya mance da maganar shine zaka zo ka tayar mana da ita to ahir dinka.

Sin sin ya miqe yai dakin mahfuz din dan jiransa.

Wai mahfuz in tambayeka mana inajinka in har ka yadda ummulkhairi ba matar nasir bace me yasa sukayi qaryar aure mahfuz yai shiru na dan lokaci kafin yace waya fada maka ban yadda ba ni wallahi na yadda matarsa ce.

Kasan kawai meke ban mamaki seka fada inji Abbakar kawai ina mamakin me yasa yah nasir yakesan dole sai ya haukatani ta hanyar nunan bashi nake gani innaje gidan matar tasa.

Abbakar yai dariya ba dole ya haukata ka va fansa suke dauka shida matarsa mahfuz yai danshiru na wani lokaci yes u are right wallahi se yanxu na gano dalili wato ya zabi mace kan dan uwansa.

To wallahi tunda haka ya zabarma kansa ni nasan nafishi santa to zan nuna masa hauka sedai kowa ya rasa dan wallahi kashe shi zan yau bako gobe ba ya miqe ya zari wuqar dake kan kayan marmarin dake bed side drawer yai waje yana huci............
[12/31/2020, 5:51 PM] 🅰️ " AXEEX✌🏼 D'🅱️🅾️Y😎: _POST BY GROUP OF HYPE HAUSA NOVELS BOOK WHATSAPP 08064400100_ 📚📚
[12/31/2020, 5:52 PM] 🅰️ " AXEEX✌🏼 D'🅱️🅾️Y😎: *ABBAKAR*

*PAGE 60---70*

Da sauri Abbakar ya riqoshi yajawo shi zuwa ciki haba mahfuz kasan nasan da hankalinka pls act serious ma katsaya ka saurareni ya amshe wuqar.

Ni ban yadda ummu matarsa bace mahfuz ya zaro ido what bafa ka yadda ba kace eh ban yadda ba to sabida me sabida kawai ban yadda ba ayanzu banda hujja anman ina ji ajikina ba matarsa bace kawai suna maka haka be dan ka fita daga rayuwarta.

Ka yadda dani karka yi abinda zakayi danasani a hankula komai zai koma dedai haka yaita tausarsa har ya samu ya sauko.

Fatima ce riqe da paper din test dinsu tana faman mita wallahi dedai nayi mutumin nan zai kansilemin dan Allah Aisha kalli nan ba haka ake ba ta kalla to ba gwanda keba nida ba'amin recording bafa to ba inkin kai masa zai miki ba.

Pls ku rakani nai photocopy din paper dinnan suna tafe fatima na mita yayin da Aisha itama keyin tata kan rashin mata recording duda yake lefin tane na rashin saka reg. Number dinta.

Ita dai Amina ba abinda take fadi se maganar absent da aka saka mata a last exam yayin da ummu tai shiru ita kadai tasan abinda ke damunta gabaki daya ta dena jin dadin sch din kawai tana daurewa ne.

Kinsan Allah maidama mutumin nan zanyi jibi fa ko makamin nan beba yaushe zaki kaimasa ya shigar miki Fatiman ta tambayi Aisha ko yau ne sai muje inasan zuwa can chemistry lab ma ok se muje gabaki daya.

Sunyi rashin sa'ar samun me photocopy hakan yasa suka kira sauran frnd dinsu kan suzo su tafi daga nan zasu viya suyi ahanya.

Sun hadu a CIT inda student dinnan suke graduating se murna suke se anan ummu tadan ji sukuni aranta dan ita din mutunce me san taga mutane sun kanmala karatu musan man data ga yara qanana se taji dama ita ce.

Tuni qawayenta sunyi gaba ta tsaya sakato tana kallom masu bikin sunata selfie yau batazo da me rainonta ba bata da lafiya koda zasu shiga exam sai wata yar level 4 ta roqa ta riqe mata Abbakar shine ya matso alamar ya tashi tai saurin sakkoshi ta matsa gefe dan bashi abinci.

Da yake yafara shan kamu shi take bashi sha yake sosai alamun yunwa yakeji yadda yakesha da kuma tunanin da zuciyarta ta tafi yasa batasan sa'adda hawayen da suka cika mata idanu ya zuboba.

Jitai an dafata ta baya tai saurin jiyowa Hafsa ce kinsan tun dazu muke nemanki ina su fatima inji maryam assha kukan me kike haba ummu ki dinga ragema ranki damuwa pls inji maryam ke wallahi kina da matsala nasan duk bazai wuce kan exam din yauva kawai ki shateta exam luck ce kawai inji hafsa to Allah ya bamu sa'a su suna waje jen fais muje nace su jirani.

Suna tafe hafsat na selfie da dan surutanta intayi wani tauawo ummu tayi musu su biyu wani ta jawo maryam, yayin da maryam ke faman tambayar ummu wace amsa ta samo a questions din yau wasu ummun ta bata amsa wasu kuma tai shiru.

Sun yi photocopy din inda fatima da amina suka wuce toilet na CIT mosque basu jima ba suka dawo.

A bus stop suka hadu da halima da sauran frnds dinsu sun hau mota tare yan hanya sun sauka ahanya yayin da su suka sauka a old side din sch din tasu dan can ne gun da zasu.

Sinyi rashin sa'ar samun duk wanda sukaje nema hakan yasa kawai ko wannen su ya wuce gida kan zasu hadu ran alhamis.

A gida ummu ta rasa me ke mata dadi dan tun randa Abbakar ya titsiyeta batajin dadi ita ba abin ta fadawa Nasir ba tsoronta daya kar yaje ya ballo mata ruwa abinci ma ba koyaushe take ci ba ko tahajin yunwa data fara ci zataji ya fita aranta.

Ran alhamis da sassafe ummu ta shirya tai sch dan sunyi zasu hadu dasu hafsa 10 na safe.

Basu wani makara ba sukazo duda kuwa ta dade da zuwa Fatima ce last din zuwa suka dunguma sai math department sunyi rashin sa'ar samun wanda sukaje gunsa bayan sun tambayi maqocinsa ko zaizo ya basu tabbacin zuwansa suka koma qasa dan jiransa.

Zaune suke sina hira sama sama yayin da karatin paper din dazasuyi yau yafi qarfi maman humaira ce ta dauko wata paper suna dan tattaunawa akai dagowar da Aisha zatai taganshi yazo suka miqe dan bin bayansa.

Faduwar da Hafsa tai ne yasa har isarsu bakin office din basu bar dariya ba ganin office din abude yasa su shiga taitayinsu suka jira na ciki ya fito kan su shiga.

Bayan sun gaisa cikin hade rai ya ce lafiya me ya kawoku paper dinta Aisha ta nuna wadda ya rubuta not recorded ya amsa da Id dinta ya shigar yayin da fatima tace complain gareta ya karba yana dubawa.

Ya dago a fusace haka na koya muku tai tsuru tsuru ya miqo mata paper dinta yayin damaman humaira tamiaqa tata itama fadan yasa hafsat na gefe tana dariya qasa qasa.

Ganin da taske ficewa zaiyi yasa Fatima yin qarfin halin qara miqa masa nanto sir bakamaka ba ya karba ya soke sir but ka makawa wasu dedai yai tsaki itama ya maka mata

Sir wai zaka bada attendance inji wa ni nai attendance ne a class dinku gabaki daya sukai tsuru tsuru pls ku fita sauri nake.

Aisha ce ta miqa nasa sir nima baka makan nanba kuma nan nayi dedai ya amsa tsaki yaja kowa ma ban maka masa ba nankuma mene sir gashi nan miqo mata takardarta yai pls kumuje nan sawa kikai wallahi sir bafa sawa nayi ba zakace nasa Dallah muje yaje suka fice gabaki daya rai abace.

Sunfi minti goma suna mita yayin da ita dai
ummu bakin naganarma babu jitake kamar tai kuka dan ita bama tayi test dinba gashi exam din se a hankali shi yasa takejin su mitar dadi ma suke.

Se wajen sha biyu maryam tazo suka bata labarin yadda sukai da malamin tai ta dariya kafin su juya akalar firar zuwa karatu.

Sai qarfe Daya da wani abun suka bar old side zuwa new side inda zasuyi exam dinsu ta yau suna tafe a mota suna fira yayin da kadan kadan suke taba muraja'ar abinda suka karanta.

Gidansu Abbakar Hajiya ce ta shigo dakin dan nata da sallama ya dago daga kan computer din gami da dan matsar da ita ya amsa sallamar bata zauna ba tace leqowa nai inga ko lafiya tunda kazo gaisheni banji motsinka ba bakuma kazo kace min ka fita ya yadan sosa qeya gami dayin murmushi yanzu nake shirin fita ina da jire dalibai wajen qarshe biyu da rabi inata faman duba wani assignments ne dana baima yara tai dariya yayi kyau ai gwara ka hanzarta yanzu shabiyu ta kusa ya miqe ahto bari in wanka ta fice shi kuma ya shiga toilet.

Saida ya shirya sannan ya sakko Abinci kadan yaci dan baya san cin abinci da yawa inzai fita yana kuma san zuwa gidansu mahfuz yasan indai time in cin abincine sai haniyar mahfuz tasa yaci abinci ko baya so.

Hajiya ni zan wuce harka shirya eh to Allah ya yemaka amin hajiyata ta fada yana yin gaba.

Haryakai bakin falon ya dawo waiko hajiya ina wannan mara kunyar take tai dariya maza taji kana ce mata mara kunya ta tafi exam af fa hakane tacemin jiya sunada paper yai waje.

Yana shirin barin main falo din wanda dagashi sai farfajiya suka shigo Kadija ce qanwarsa wadda take aure a Zariya sai yaranta guda uku nan danan fara'arsa ta qaru a'a manyan baqi yaran sukayo kansa suna ihuuu uncle uncle ya daga su dai dai kafin su rungumo juna shida sister din nasa suna yaushe gamo ciki ya bisu dauke da qaramin data ke goyo ina hajiya ma na ganinsu murnarta ta qaru.

Yaran sukayi kanta da gudu qaramin ma yasa ihu saida ya saukeshi shima ya fada kanta ohni hashina yarannan so kuke ku qarasani Abbakar yai saurin cewa ku daga mun uwani karku karya min ita a'a kaga malan ka qyalen yan jikokina su mori kakarsu suka juyo suna masa gwalo suka saka daria gabakibdaya.

Keda me gidanne yake tambayar qanwar tasa a'a mu kadaine sai zamu tafi zaizo sai su gaisa da hajiya ok yayi kyau yadan kalli agogo opps zanyi latti inna dawo dai koma mene ne ma tattauna ya miqa mata hannu sukayi musabaha kamar yadda al'adarsu take sun riga sun saba to sai nadawo to yah sai kadawo da labari naga alamu ko tai dariya kaidai bari kawai sai kadawo nagama duk kayi baqi dama can baqin nake kinga sai nadawo ya fice aiko Malan qarami ya taso da gudu yabi bayansa yana kuka uncle uncle mamanshi tai saurin daukoshi ta dawo dashi ciki.

Ko gidansu Mahfuz din baijeba ya wuce sch dan yaga ya makara.

Wayarsa ce ta fara qara time in da suke raba booklet ga student ya migama malama zainab dan basu ina zuwa sunan ummi mabiyar autarsu ya gani kan wayar towo ya fada yasan yanzu ai yakamata tana exam room yai saurin dagawa cikin kuka take magana yah ina cikin matsala subhanallahi mene badai malpractice aka kamaki dashi ba ko tai saurin goge hawayen kamar tana kusa dashi kaji kuma yaya Abinda banyi da ba zanyi yanzu.

Sai yanzu yadanji normal to mene wallahi yaya ina cikin matsala kana ina ne ni ina chemical engineering ok ganinan bata jira cewarsa ba ta kashe ya tsaya kawai yana kallon wayar kome wannan yar rikicin ta jawo musu kuma oho dan ko autansu baya abinda take kai tama zama tafi autan tabara hajiya kuma tai ta goya mata baya kodan shi autan baya qasar ne oho.

Minti biyar sai gata kamar wadda tai gudu tai futu futu da ita kallo daya yamata daga ajin da yake yaja tsaki sannan ya kuma yima malamar da suke kula da daliban magana pls ina zuwa.

Waike lafiya kika dokan kira haka tasa kuka yah na mance ID dina kuma sun hanani shiga towo ni me kike so na miki yanzu ta kamo hannunsa so nake kaje ja roqesu nasa Bala yaje ya karbo min to se ki bari yakawo ai.

Dan Allah yah kaji qaina kasan in aka fara fitowa bazasu barni inyi ba yai shigewarsa ajin ni nace ki dinga sakaci gobe kya rage lalaci da mantuwa aikuwa ganin ya shige ajin ta fashe da kuka.

Wajen minti biyar saiga malan Mansur yazo ya shiga ajin suka gaisa kafin su fito tare tasan mansur lecturer dinsu ne saidai yah nata bai taba ce mata yana da aboki a faculty dinsu ba balle department din datake kullun sai dai ya dinga cewa ta dage tai karatu danshi ba abinda zai iya mata.

Ya dagota yawwa gashinan abokina zaije ya rakaki anman wallahi inkina irin haka karma ki yi tunanin kinsanni tai tsalle tama mance a inda suke ta fada kansa that's why i love u mansur yace muje kina kuma makara tai saurin saukar da ido qasa wai taji kunya tabi bayansa suka wuce.

Duk abinda suke ummu na kallonsu ta tagar ajin da suje wani abu yazo ya tsaya mata arai ita

kadai tasan mene kawai ta cigaba da rubutunta.

Ta gama rubutunta tas tana kuma dubawa na kusa da ita ya mata mgn juyowar da zatai tace me kace a idon Abbakar aikuwa yayo waje submit yace sorry tace bazaki bayar ba kena no ba hk bane ko ki bayar ko ki cike form dinnan ya miqo mata malpractice form tai saurin bashi tana singing out hawaye na bin idanunta ita kadai tasan hawayen me take dan bawai na anqwace bata gama bane.

Tunda ta fito take kuka har Aisha ta fito dagyar suka sa tai shiru ita da halima azahiri kenan anman a badini tai shiru ne kawai bawai dan taji nasihohinsu ba dan sanin bata da wata mafita inma kukan ta cigaba dayi shirun ma shine mafi alkairin kawai.

Sunfito suna masallaci danyi la'asar su tafi gida Hafsa ta dube ta idonnan yai fayau dashi tana riqe fa Abbakar Allah ummu mutumin can sanki yake wa kenan malan Abbakar mana taja tsaki maryam tace mene haka hafsa da aurenta fa yanzu in mijinta yaji yace mene haka nefa na mance ai wallahi kinyi sa'ar miji me sanki gashi me kyau halima tai dariya a'a Hafsa kimana shiru karkisa yanzu muga ta miqe ta hau jibgarki kinsan kishi gabaki daya sukai dariya inka dauke ummu da kana kallonta kasan yaqe take.

A old side Hafsat tace ita zata ta amso wata takadda Aisha tace tunda muka fito nakira mam nace mata munfito nidai na tafi to sai gobe suka hau dan sahu ita da ummu da fatima da halima halima ce ta fara sauka a danja su kuma aka wuce dasu.

Halima na sauka ummu ta dubu Aisha inasan magana daku ina cikin matsala wallahi but me yasa tun dazu baki fada mana ba to yanzu munajinki no inaso mu samu guri ne anman yanzu ki ba sai gobe.

Gobe kuna kun mance an gama exam ah hakane tacema dan sahu pls tsaya anan ya tsaya daidai legal college of islamic studies ku fito what kinafa ji nace miki na ce mam na tawo pls ina buqatar shawararku ne da gaggawa.

Aisha tadan tsaya jim tana tunani me adai daita sahun yace zaku saukanne ko mu wuce fatima ta fito tana juyar da fuska wai ita kar wani fa tasani yaganta ta sauka a qofar sch din akai gulmarta gida ummu ta miqa masa kudi Aisha bata da zabi ta fito.

Sun nuna ID dunsu na BUK sun kuma yi sa'a anbarsu sun shiga cikin kujeran da aka tanada dan zaman students na bakin bishiya suka zauna.

Ai kuwa suna zama ummu ta fashe da kuka dagyar tai shiru saida Fatima ta miqe kinga inbazaki fada mana ba ni zan tafi ta rugo hannunta alamar ta dawo ta zauna.

Ta komo ta zauna ina cikin wani hali mene ya faru munce ki dena wannan damuwar kinqi.

Yah nasir ne matsalata me ya miki inji Aisha fatima ta dafe qirji badai cewa yai kibar masa gida ba in wannan ne ai me sauqi ne to mene suka fada cikin tsoro.

Wai cewa yai yana sona mtssss suka ja tsaki atare to saime ke ba abin farin cikinki bane mutumin da duda yasan komi game dake ya dauki kasadar riqeki duda yasan hakan zai iya rabashi da iyayansa yadauki nauyinki ya rufa miki asiri kika zo cikin Abbakar nanma bece komi ba ya dauki ragamar komi to mene ba damuwa.

Cikin kuka tace ni banasansa indai so na aure ne what ummu kinsan me kika ce kuwa eh nasani to wa kike so in bakya sansa Abbakar suka mike gabaki daya arazane suka maimaita Abbakar eh shi wai wane Abbakar din lecturer dinmi ba thermodynamic badai wanda ya koroki yauba eh shi ni shi nakeso nayi nayi na cire abun araina nakasa.

Tabdi kin dauko dala ba ganmo inji fatima Aisha tace haba ummu karki zama butulu mana ta ture hannunta da ta dafata ni shi kadai nake so shi kadai nake gani shi kadai ne burina shi kadai nake gani dashi na shirya rayuwata gabaki daya pls ya isa haka fatima ta fada cikin fushi bansan shirme wallahi........
[12/31/2020, 5:52 PM] 🅰 " AXEEX✌🏼 D'🅱🅾Y😎: _POST BY GROUP OF HYPE HAUSA NOVELS BOOK WHATSAPP 08064400100_ 📚📚
[12/31/2020, 5:52 PM] 🅰 " AXEEX✌🏼 D'🅱🅾Y😎: *ABBAKAR*

*PAGE 70---80*

Haba ummu kiyi tunani mana ai kinsan ko da Abbakar ba abokin Mahfuz bane babu ta yadda za'ai ya yadda ya aureki kina ganin yadda yan mata masu aji ke faman sansa kuma ya sani bawai be sani ba anman ya sharesu.

Ki daurewa zuciyarki karki zama butulu Yah nasir be cancanci haka ba yacancanci duk wani karamci daga gareki ya miki duk wani halacci na rayuwa kidaure ki sake tunani wallahi.

Nifa ba cewa nayi bazan aureshi ba ni wallahi amatsayin uba na daukeshi koma uwa da uba na taya kuke ganin zan iya zaman aure da wanda nakema kallon iyayena.

Daurewa zakiyi ahankula inkika ce kin amince kuka fara soyayya tuni zaki mance da a ina kika ajiyeshi kina kallonsa haka simi simi zai baki mamaki dan irinsu sunfi sanin takan mace batasan sanda tai dariya ba wallahi baku da dama ko kadan.

Sunji dadi datai dariya yawwa ko kefa ki dena yawan kuka da damuwa kisama ranki dangana yanzu ki daure in yazo ki fada masa bacin yai fushi ya dena zuwa kingani ko duk haqurin bawan Allahn nan.

Yanzu ki kirashi ki bashi hakuri kice kin amince wa ni tab inba bazan iyaba kuma tunda ya hanani kiransa iyanzu sabida yace yana gida ok to ki bari sai dare lokacin ya shiga daki tai jim

tana tunani kinga inbazaki iya kiransa ba ki tura masa saqo kawai to shikenan sai na koma gida.

Shi kuwa Abbakar tun da ya qwace paper din ummu yana kallon ta time inda take singing hawaye na bin fuskarta jiyai kamar ya bita ya rarrasheta ko ya goge mata hawayen saidai ba dama.

Yar firar ma dasuke da daya malamar duk sai ya kasa ransa gabaki daya ba dadi yaji sai faman fada kawai yake qarshe ma tasauran student din karbewa yai danji yai gabaki daya ya tsani ajin.

Futowar da zasuyi hangota tana faman kuka ana bata baki nanma jiyai kamar yaje yashiga sahun masu bata bakin yadai dake kawai.

Sai mangariba ya koma gida shima dan kar hajiyarsa taji wani abu badan yaso ba dam jiyai gabaki daya baisan hayani yama mance da qanwarsa tazo duk dokin da yake na yaje ya dawo su kwashi fira ya tafi.

Saida ya shiga falon yama tuna hakan yasa ya fada da murmushin fuskarka ya shiga da fara'a.

Tana ganinsa ta qunts e fuska inba nayi fushi ba aikasan da zuwanmu shine sai yanzu zaka dawo yazo ya zauna kujerar dataje inba bakiyi fushi ba ya fada yana irin yadda tayi tasa dariya Yaya ta fada shima yasa dariya qanwa bari in shiga in rage kayan jikina sai in sauko to se ansakko.

Danqaramin danta yasa kuka ya daukeshi ya daukeshi sukayi saman tare yana masa fira irin tasu ta yara.

Tare suka sauko yana dauke dashi da alawa ahannunsa aikuwa yana direshi mai bi masa ya sauko daga kujerar da yake faman game ya kwace alawar ya tura baki aikuwa ya tsanyara kuka dasauri Abbakar ya juyo OMG this boy me aka ma ya fara nuna yayan nasa da alawa abaki.

Ah wahid ya zama babban kwabo yai saurin miqa masa alawar wasa nake masa fa suka sa dariya dan wahid bayasan ace masa babban kwabo dan zatonsa kwabon wani abu ne marar kyau.

Shima wata Abbakar yadauko a aljihu ya miqa masa yakoka yana tsalle thank you uncle dayan ma ya taso ya miqa masa sai muskilin nasu baya maga sai yaga dama mutane da yawa nacewa Abbakar yayo musanman babansu danshi yace duk danginsu babu muskili aikuwa ganin anbawa kowa ba'abashi ba ya zumburo baki ya huro hanci sai hawaye da sauri Abbakar yai gunsa haba nawan mene na kuka kuma yai shiru to shikenan ya goge masa hawaye.

Ya bude alawar ya vashi to ungu kaga takama ni na bude maka ya miqe zai koma ya zauna

ya riqo rigaraa ahankula yace thank you uncle yai dariya kawai.

Hira suke sosai gabaki dayansu har hajiya tace kunga ni na gaji saida safenku duk an miqe sai ummi yah Zainab sai da safe inkika biyewa yah Habu saiku kwana anan ya kalleta wato yau rashin mutuncin naki kaina ya koma ko.

Tai dariya ai tunda kasa nai kuka asch na yah Habu zan dinga cewa tai daki da gudu ya kada kai yana dariya dan in ummi ce komaima zatayi shi yamayi mamaki da ya dawo bata sa hajiya ta cakcakeshi va dan yasanta da sharri.

Zainab ce ta juyo daman tun dazu wallahi nakesan muyi magana ya kalleta me ne kuma daman Babansu wahid ne nace masa inasan in koma sch in cigaba da karatu qeme me ya hanani yai saurin kallonta to me kike nufi yaji kika yo kome.

A'a ba yaji nayo ba wallahi kawai ziyara ce nadai fada ma ne dan Allah ka roqarminshi ya yadda ehto ba roqarsa zanyi ba zan saneshi muyi magana in ya yadda to inbe yadda ba ki haqura masters dinki ya isheki keda ba aiki kike ba ina jarin dana baki kwanaki tahau sosa qeya duk sun qare ko tai dariya kawai.

Shikenan kibari inasa ran shigowar kudi na kayan gonata danake na sayar zan yi qoqari in bude miki dan qaramin store in kikai maintaining dinsa ya isheki rayuwa mijinki ba abinda ya rageki to yah na gode.

Sauran daya maganar inajinki yah dan Allah kafadan meke damunka duk kayi baqi ka rame yai dan murmushi me kuwa ke damuna kawai yanayin aikine kullin cikin jele daga han zuwa old site daga can zuwa new site ba dole mutun ya rameba anman yah anman qarya nake ko a'a ni ba haka nake nufi ba.

To tashi muje ku kwanta kar gobe yarannan su tashi da wuri su hanaki bacci kanki yazo yana ciwo ta miqe ta sabi yaro guda shima yadauki biyu qananan ta tashi babban suka wuce dakin da zasu kwanta saida ya kwantar mata dasu ya mata saida safe ya wuce dakinsa.

Zaune take tana ta faman rubuta saqon da zata tura masa tana gigewa ta rasa me zata tura mai qarshe dai ta rubura

_Assalamu Alaikum
Yah nasir barka da dare daman cewa nayi na Amince Alkah ya bamu zan Ipy_

Gabaki daya tama kashe wayar tahau kuka bayan ta tabbatar saqon ya tafu.

Yana kwance idonsa akan fanka shi kansa besan tunanin me yake ba yaji alamar shigowar saqo a wayarsa kamar kar yadauka ya duba yadai daure ya miqa hannu yadauko.

Ganin sunan ummu yasa shi miqewa ya zauna tunkan yaga saqon yai saurin budewa duda ba wata magana bace me yawa sai saqon ya masa dadi sosai jiyai kamar yai tsuntsu yaje ya tabbatar ita dince ta turo ba kuskure bane.

Yaso tashi da wuri saidai kasantuwar bai kwanta da wuri ba yasa sai wajen tara da rabi ya tashi.

Wanka ya fara yi shi kansa baisan meyasa yake dokin zuwa ganinta dinba besan me yasa yake ta dauko kaya yana sauyawa ba duk dan ya burgeta duda yasan tasanshi batun yauna.

Shadaya dedai ta masa a gidan ummu Farida ce a farfajiyar gidan tana karatu abokiyar zaman ummun tana ganinsa ta saki fuska sir barka da zuwa yadan hada rai sau nawa zance a dena cemin sir dunnan a gida tai dan murmuahi sorry sir kika kuma yai shigewarsa ciki ta biyo bayansa tana dariya.

Yai saurin cafe Abbakar ko ince mahfuz da ya rarrafo zuwa bakin qofa yana bin ball insa ya ko tsanyara kuka dan besan waya daukeshi ba Nasir yai saurin juyo da fuskarsa haba yaron babansa jin muryar nasir yasashi yinshiru yana ganowa a hannunsa yake ya bangale da dariya alamar farinciki.

Dan rigima wato da bani bane shikenan sai ayita kuka ko Ummi da ta zo daukansa tasa dariya itama lah yah nasir ashe zakazo yai dariya ce miki akai da nadena zuwa a'a nadai ga kwana biyu baka zuwa ne suka shiga falon gabaki daya har Farida.

Wallah yah nasir nayi missing inka da yawa eyye ko eh mana inji Farida duk ganina da kike a sch ta dan rausayar dakai bayan a sch din nuna wa kake baka san mutane ba Allah ko eh mn inka wani hade rai to shikenan maida wuqar zan dinga dariya sukai dariya baki daya.

Ta miqo masa littafi Allah tun jiya nake karanta nan nakasa pls koyan yakarba ya duba eyye wato duk lecture din da muku bakima gane ba tadan juyar da kai time inne inajin bacci to ynx ma ai inna miki cewa zakiyi bacci kike ji dan Allah yah nasir to shikenan bari sai anjima.

To wannan fa ta miqa masa paper a'a banda wannan ai assignment na baku pla yah inkika isheni ko sauran bazan koya miki ba wai ina Ummu ne ta dan fita ne nasan yanzu zata dawo.

What ina taje mene anfanin ummi da na kawo mata tace batasan aiken ummi bata rufe vaki ba Ummun ta shigo ya hade rai daga ina kike naje shago ne ko dan kinga kwana biyu bana zuwa shi yasa kika tsiri futa yawo.

Idonta yai rau rau kamar zatai kuka haba yah nasir kasan bana maka qarya to me yasa baki aiki ummi ba naga batasan zuwa ne what no bawai qi take ba aikenne kamarta dole taji kunyar zuwa wane irin aikene ta miqa masa always ya gani oh basai ki fadanba da wake sayo muku tadan turo baki to inama muka ganka bacin ka dena zuwa yadan sosa kai aishi kenan.

Farida ta miqe tai waje yah bari inje inci gaba da karatuna ummi tasa hannu zata dauki Abbakar yako sa qara Nasir ya ce jeki abinki kyaleshi tai ciki.

Ummu ta zauna yah ina kwana lafiya kalau yace ya dannawa ta kalli Abbakar ganinan ai.

Jiya sai naga saqo tai murmushi ashe ma shi ya kawoka yai dan murmuahi dadinsa da ita akwai bawa mutun amsa haka nace miki shi ya kawoni to yaya rabonka damu kwana nawa bakiga exam ake a sch ba bani da time inkuma nakai dare kinsan hajiya tai dan murmuahi batare da ta amsa ba.

To anman yah kana ganin family dinmu zasu yadda da aurenmu yai dariya gami da sauko da Abbakar to aiko basu yadda ba abinda nasani ni shine dolene su yadda tunda kin yadda ta kalleshi ya daga mata gira.

Fira sukai sosai sai da aka kira sallah ya miqe bari in sallah ya fice.

Haka kawai ummu kejin takaicinsa ya ragu aranta haka kawai takejin hirarsu ta mata dadi koda tana sallah lokaci kadan kadan take dan murmusawa kodan yadda nasir kesan Abbakar dinta ne oho dan rabon da taga yaron na kyakyata dariya yanata warkajaminsa tun dena zuwan nasir abu kadan ma aka masa sai kuka kodan farin cikin danta zata haqura ta takurama zuciyarta taso nasir .

Yana dawowa yace ni zan wuce sai kinjini yah mun gama abinci kazauna kaci inji ummi ok to kamar kinsan yunwa najeji tai dariya gami da komawa kitchen din.

Farida ta shigo yana cin abinci yanzu yaya da abinci be tsaidaka ba shikenan karatuna yasha ruwa yai murmushi sorry mangofa ynx zamuyi.

Sai da suka gama karatun Nasir ya musu sallama ya tafi cike da kewarsu ji yake kamar karya tafi.

Gidansu Abbakar

Wahidi ke ta faman kuka shi bazai tafi ba shi anan za'a barshi daqyar sai da yaga babansa yazo ya hau murna sannan ya yadda yabisu zainab sun tafi cike da kewar yan uwanta da ummanta.

Shi kansa Abbakar sai yaji gidan wani iri dan dan kwana biyun da sukai agidan gwanin dadi kullin cikin hayaniyar yara hakan yasa zainab suna tafiya yace ma hajiya zaije waje sai dare zai dawo sao kadawo tace ta koma ciki.

A teburin me gadinsu yazauna a qofar gida suka hau fira sai mangariba yabar nan din yai gidansu mahfuz dan ya kwan biyu bai ganshiba kamar yadda ya zata kamar koyaushe Mahfuz

baya bangaren mazan gidan   dole ya zayayo cikin gidan aikuwa abunda bayaso yan matan gidan sunata sha'aninsu waccan na zaune waccan na shanya ko wacce da abun da take bawai abubuwan da suke ke bashi haushi ba face shigarsu basa shigar kwarai indai sina gida duda kuwa abokan yaran gidan kowa shiga gidan yake haka mazan bakowa ne suke shaqiqaiba kawar da kai yai zai yi ciki.

Ya jiyo Aisha na fadin lah yah Abbakar sannu da zuwa yadan saki fuska yawwa qanwarmu ina kuwa mutumin naje dakinsa baya nan lah ai yadawo ban garen hajiya tun rashin lafiyarsa yana nan ma yanzu ok to bari inje.

Yana zaune a falon kansa kan cinyar hajiya Abbakar ya shigo ganinsa hajiya ta fada da murmushinta  mahfuz ya miqe zaune a'a ai da kayi kwanciyarka dan gatan hajiya yai dariya zaka fara ko sun gaisa da hajiya ta miqo ai qwanda da kazo duk yabi ya damu kansa kan ummu ka masa nasiha nasan yafi jin maganarka akan ta kowa.

Sun taba fira Abbakar ya miqe sukai masallaci agidan yaci Abincin dare sannan mahfuz ya leqa dakin hajiya zai tafi zan rakashi shima ya leqa hajiyarmu sai da safe au ba'a nan zaka kwan ba eh hajiya ban fadama hajiyata ba to agaisheta sai da safe suka fita tare.

Sun dade a qarshen layi suna tattaunawa kan batun ummu kasan Allah Aminin in yau akace inada ciwon zuciya ba mamaki kullin cikin tinanin ummu nake bacci ma bayinsa nake sosai ba kai mahfuz kadaure ka cirema kanka damuwa kodan hajiya kasan yau in wani abun ya sameka tafi kowa tashin hankali haka ne shi yasa nake daurewa yawwa ka ci gaba hakuri kaji nawan sukai dariya gabaki daya gami da sallama suka rabu.

Hajiya daman so nake muyi magana inji Nasir ta maida hankalinta kansa inajinka akan nefa yadan sosa qeya eh daman ta miqe kaga inbaka shirya ba inka shirya sai ka same daman hajiya tada miki zanyi na samu matar aure tai saurin juyowa da fara'arta da gaske kake eh hajiya wace kuwa wannan Hajiya ummulkhairin baba yasir what ta fada eh Hajiya alamar faduwar da sukaji yasasu juyawa da sauri Mahfuz ne zube da alamun yaji maganarsu ne hajiya tai gunsa da gudu itama hippp ta fadi a sume.............
[12/31/2020, 5:52 PM] 🅰️ " AXEEX✌🏼 D'🅱️🅾️Y😎: _POST BY GROUP OF HYPE HAUSA NOVELS BOOK WHATSAPP 08064400100_ 📚📚
[12/31/2020, 5:53 PM] 🅰️ " AXEEX✌🏼 D'🅱️🅾️Y😎: *ABBAKAR*

*PAGE 80---90*

Rasa ma kan wazaiyi yayi ta maza yai yadauko ruwa yai kan Hajiya cikin sa'a ta farfado da tana bude ido ta tankade nasir tai kan mahfuz dake kwance tahau jijjigashi miqon ruwa mana ta fada cikin qaraji.

Dasauri ya miqa mata ruwan ta hau shafa masa bai far fado ba da sauri Nasir ya daukeshi sai mota hajiya na biye dashi ganin haka yasa sauran mutan gida dake farfajiya sukayo kansu suna

tambayar lafiya basu basu amsa ba suka bar gidan hakan yasa suma suka biyosu amota sai kadan aka bari agidan.

Kai tsaye asibitin nasarawa suka wuce basu wani sha wuya ba dan babu marasa lafiya sosai a emergency din yau aka karbi mahfux din.

Tun wajen awa guda da'aka shiga dashi dakin bada temakon gaggawa hajiya keta faman kai kawo tana hawaye babu yanda ba'ai da ita tazauna ba taqi da nasirma ya mata magana saita haushi da fada daqyar tai shiru shima dan nurse ce tazo tace ta ishe su.

Ganin hajiya zata iya masa baki yasashi miqewa yabar gurin yai dan nesa kadan dasu dan yaga irin hararar da take sakar masa lokaci lokaci gami da tsaki da qwafa da take ja in suka hada ido.

Doctor yana fitowa sukai kansa bai kulasu ba yai gun Nasir dan yasanshi aikuwa hajiya na ganin haka tabi bayansa tana fada yau naga mara mutuncin likita ya jiyo zai yi magana Nasir ya dafoshi Am sorry Abdul mum dina ce yadan saki fuska kadan gami da cewa Hajiya bawai na share ku bane kunsan irin haka namiji yafi karfin rai.

Eyyye qarfin rai har yafi na cikin sa da nadauka nai naqudarsa ni nasan zafinsa dan haka zanfi kowa iya jure abinda ke damunsa dan in kula dashi ganin tadau zafi yasa Doctor din yace ai yamaji sauqi dan mun shawo kansa dakyar muka dai daita numfashinsa zaku iya shiga ku ganshi bata jira cewarsa ba tayi gaba.

Nasir ke biye da ita saida suka zo dedai dakin ta juyo ta watsa masa harara me kuma zaka shigo kayi masa bai ce komi ba ya koma baya ya tsaya.

Kwance yake idonsa a rufe da alamun bacci yake hajiya taja kujerar gefensa ta zauna gami da kamo hannunsa ta riqe yai saurin bude idanunsa zatonsa Nasir ne ganin hajiya yasashi fashewa da kuka ta hau rarrashinsa dakyar yai shiru.

Da sassafe nasir yabar asibitin saida ya biya ta gida sannan yai wanka ya shirya yai gidan ummu acan yakarya sun dan taba fira kafin ya miqe ni zan wuce yah tun yanzu eh ummu tadan shafa kan Abbakar Allah ji nake kamar karka tafi yai saurin kallonta da alamun har zuciyarta take magana anman bai fasa cewa da gaske kike tai dan murmushi Allah kuwa to banda abinki ai kwanan nan sai kinmace in fita ta rufe fuska anya kuwa yai dariya ina nan dake.

Har waje ta rakoshi ya miqo mata Abbakar yako sa kuka haba dan rigima yi shiru anjima zan dawo ya zura hannu a aljifu ya miqo masa alawa yako amshe yana kiciniyar budewa.

Har ta juya yace aff ban fada miki ba gobe ba lallai inzoba tadan juyo sororo sabida me yah eh mahfuz ne ba lafiya jiyama a asibiti ya kwan tadan tabe baki ayya Allah bashi lafiya gami dayin ciki abinta abinka da dan uwa sai gabaki daya baiji dadin abinda tai ba aqalla ta nuna tadan

ramu ya gyada kai kawai yai gaba.

Ai kuwa da Nasir ya koma asibiti ya sha fada gun hajiya kan yasan dan uwansa ba lpy yai tafiyarsa yawonsa ba ita tai shiru ba sai da Mahfuz yace dan Allah hajiya kice ya fice daga dakinnan inna tanshi numfashina hadewa yake jin haka yasa yace ya fice.

Wajen qarfe uku na rana Abbakar yazo shida Hajiyarsa da qannensa biyu mata sukaita fira da hajiya inda shima sukaita fira da amininsa.

Kwanan Mahfux biyu ummusalma yayar Abbakar tazo dubashi aiko tasha qorafi dan sun saba sosai da Mahfux inma mutun ba sani yai ba zaiyi zaton Mahfuz ne qaninta ha Abbakar ba.

Bakowa adakin sai Mahfuz da ummu salma aikuwa mahfuz yasa mata kuka daqyar ta rarrasheshi yai shiru tahau tambayarsa mene yahau bayani kan ummu ne yar gidan baba yasir yah nasir yasan ita nake so anman yace shi zai aureta tahau masa nasiha haba nawan kabari zamuyi magana dashi nasan baisan kanasanta va inda yasani da tuni ya aura ma ita Allah yasani nace kabar min komi a hannu na zan mai magana ya riqo hannunta nagode yayarmu.

Sai dare ta bar asibitin shima saida Abbakar zai tafi ya tafi ita dan bada mota tazo ba.

Washe gari ta kira nasir a waya har gida yazo ya sameta ta mai bayanin komi yai dan murmushi kafam ummusalma kenan ai duniya ko hajiya bata isa tasa   in fasa aurenta ba lokaci yayi da mahfuz zai dena abin da yaga dama lokaci yayi dazai gane vawai komi kake so kake samu ba arayuwa, tai sakato tana kallonsa eyye tunda hajiya ma bata isa ba inaga ni yar karoro yayi kyau ta miqe ta bar falon shima ya kade rigarsa ya bar gidan.

Kwanan Mahfuz  hudu aka sallamesu sina zaune gabaki daya a falon mahfuz na kwance kujerar da Hajiya take Nasir ya shigo dauke da Abbakar dansa hajiya ta bishi da kallo gami da yaron wannan fa ya dubeshi dana ne what danka kuma eh hajiya dana ne da muka haifa da ummulkhairi ta miqe ashe nasiru haukan da kake cewa Mahfuz yayi ashe kai kayi yai dan murmushi hajiya aikinsan ba qarya nake ba kuma kinsan da hankalina.

Mahfuz ya miqe qarya yake hajiya dana ne wallahi qarya yake kumin shiru da Allah injita ta fada ra qarfi sukai shiru baki daya kafin nasir ya fara magana eh hajiya ki yadda dani gama kamarmu nan kina gani da yaronnan sabida shi na yanke shawarar auren mahaifiyars dan Allah ki yadda in aureta kodan kare mutuncin bawan Allahn nan tai shiru kawai tana kallon yaron da yaketa faman wasansa tabbas kamarsu  nan sosai jitai tsanar yaron ta cika mata rai sosai tai kansa zata takeshi mahfuz da yake atsaye yai kasa asume tai saurin yin kan danta.

Sun samu ya farfado aikuwa ya hau kuka hajiya qarya Nasir yake yaronnan dana ne dan Allah karki yadda ya aure min mata wallahi inban aureta ba mutuwa zanyi Nasir dake zaune tun dazu ko motsi beba tun suman Mahfuz yana ta faman wasa da dansa  yace aikuwa sai dai ka mutu Hajiya tahau rarrashinsa dagyar yai shiru tasa aka kai mata shi daki.

Adakin rokonta kawai yake kanta yadda adaura masa aure da ummu tai shiru kawai da ace wani ne cikin yaranta ke faman kiran suhan wannan yar maqiyarta ta da tuni ta yi maganinsa dan dai kawai mahfuz ne.

Haba mahfuz kayi tunani kwata kwata baku dace da ita ba ko kadan ya miqe haba hajiya inban dace da itaba da waxan dace zuciyata da gangar jikina ita suke so.

Nasir ya shigo dauke da yaron yanata faman dariya yace hajiya ni zan mayar dashi kuma gobe ne za'a daura mana auren kawu nazifi ne wakilinta ni kuma nazama wakilin kaina banasan ko kadan kosau daya yarona yai kukan rashin uba nasan ban kyauta miki ba anman nan gaba nasan zakiyi alfahari dani tai zuru tana kallonsa tama rasa ta cewa wai yau nasirun da ko uhum baiso yaji yace shi ke fada mata baqaqen maganganu haka.

Bai jira cewarta ba ya juya zai fita mahfuz yasa qara wallahi hajiya indai baki dakatar dashi ba ta auren masoyita wallahi yau zan kashe kaina tai saurin kiran sunan nasir yai gaba batare da ya tsaya ba tace nasiru wallahi ka qara taku daya Allah ya isa kuma sai ka biyani shayarwar da naima inyaso ka canja uwa yaja ya tsaya hawaye ya biyo idanunsa.

Juyo nan ka kalleni ya juyo ya kalleta kasani ni uwarka dana haifeka hai haqudarka na shayarda kai na haramtama auren yarinyar nan inko ka aurenta Allah ya isa bazan kuma yafe maba ka kuma sani koda bayan raina ne.

Jiyai kamar an sheqa masa ruwan zafi qafafunsa sunkasa daukansa yana qoqarin yada Abbakar a hannunsa zubewa yai qasa jabas hawaye na bun fuskarsa.

Ummu ce ta fito daga daki tana kwalama ummi kira da sauri ta qaraso gani aunty ina Abbakar tace sun fita tare da babansa tun yaushe wajen magariba ta gyada kai kawai ta koma daki.

Har kusan qarfe takwas bai dawo ba ummu ta kuma futowa  wai ina yace zai jene farida tasa dariya Allah umma bakida kara indai akan wannan yaron naki ne tai kwafa gami da turo baki kuban amsa tukunna kafin afaramin qorafi ummi ce tace cewa yai zashi gidansu dashi zai nunama hajiya shi what ta fada tana zare ido mai yasa kuka kuka barshi baku fadanba ummi tace   cewa yai bazai dadeba.

Kuka kawai ummu ta fashe dashi gami da fadin shikenan nasan hajiya bazata barmin shi da raiba kuka take sosai farida na bata haquri.

Zumbur ta miqe tai daki hijabi ta dauko da wayarta sai kudi dabatasan ko nawa bane ta zari jaka tai waje ummi taso muje tace bata jirata ba tai waje ummi tai saurin binta dan tunda tadan fara girma tadena cire hijabi ko ina dashi take shiga ko bacci zatai duk yadda su ummu sukai da ita taqi ita kunya takeji.

Farida ce tai saurin miqewa ta ruqo ummu haba ummu ina zaki cikin daren nan zani inga halin da yaro na yake ciki ta riqeta dan Allah ummu ki rufa mana asiri karkije dan farine fa tai dan murmushi daga gani na takaici ne tace farida sakeni koma dan mene bazan zauna inaji ina gani akashemin shi ba wai da sunan kunya.

Haba ummu aikin san babu ta yadda za'ai Yah Nasir yabari wani abun ya sami Abbakar kema kinsani ta gyada kai nasani Farida saidai nasan makircin mahaifiyarsa bata jira cewar Farida ba sukai waje ummi ta bi bayanta.

Adai daita sahu ta tara sai da suka fara tafiya yace haija ina zamu ne sunan unguwar ta fada masa.

Adai dai qofar gidan ya parker dan sahun yace hajiya mun iso ta ciro dubu ta miqa masa ya amsa ta juya tana kallon kofar gidan yace hajiya canjinki riqe tace ya juya yana murna dan be mamakiba ganin tamfatsetsen gidan da yasaukesu da alama yarinyar gidan ce ya fada.

Gidan su Abbakar

Tun jiya suke ta gyare gyare da kin tse kintse yau kam girki siketayi tun safe dan hajiya da kanta tashiga madafa ita da maryam da ummi dan yau muktar zai zo hutu da autan hajiya.

Yadda hajiya ta zage tana ta hada kayan datasan yanaso koya kai mistake yanzu ta hau fada abinda ba sabonta bane haushi duk yabi ya ishi ummi dan duk fadanda hajiya dake yawanci akanta ne koya tai mistake. Sai kace ba ita ce take kuka lokacin da zai tafiba kishin sakun takan ya motsa.

Tana sane cikin zobon da hajiya ta gama masa ta zuba zuma duda tasan bayasan zuma a abu me sanyi aikuwa hajiya ta hau fada har saida taji dama batasa ba aikuwa idonta yai rau rau kamar zatai kuka maryam ta faki idon hajiya ta mata gwalo nan da nan hawayen ya zubo hajiya kinganta ko hajiya ta cillama maryam harara fita idona maryam tunkan raina ya baci bansam tsokana ummi tasa dariya gami da mata gwalo zatai magana hajiya tace karki kawon qara aike kika fara shiru maryam tai tana hararar ummi dan tasan kobata ummi komi ba hajiya bazata mata magana ba dan duk gidan sun sani in abu ya hadaka da ummi dole kaine mara gaskiya sedai in ita da dan autane to dole ta dau rashin gaskiya.

Sun gama komi sunyi wanka inda hajiya tai tafiyarta dan cewarta bazata bar dan lelenta ta jirasu ummi su bata mata lokaci wajen kwalliyarsu ta tsiya ba.

Suma sun fito tsab shigarsu iri daya sunyi kyau sosai ummi tai daki da gudu tana kiran hajiya wayam ta gani gaji mai aiki ce take fada mata ai tuni hajiya ta tafi aikuwa ta zunburo baki tai waje tana bubbuga qafa ita ala dole taji haushi da Abbakar taci karo ya riqota yar kelen hajiya ya akaine ta kuma kumburo fuska ba hajiya ce ta tafi ta barni ba yasa dariya ba dole ta tafi ta barki ba mowanta zaizo kin zama bera tasa kuka yaya yai saurin goge mata hawayen da wasa

nake muje inkaiku ta tirje ita bazata ba haba mowar hajiyarta kidaure muje kinji tawan ta dan murmusa yajata suka fice maryam biye dasu.

Seda suka Abbakar ya amshi powder gun maryam yashafa mata kar yaroncan ya rainaki yaga kinyi kuka tai dariya tanasan yayanta sosai duda duk sauran yan uwanta haka sijeji dasu ita da autan hajiya shi yada suke tsula tsiyarsu se kace yara inda azahiri shekarunta ashirin cif kazalika autan hajiya twins ne ita dashi saidai ita aka fara haifa saidama takwana biyu akama hajiya CS aka ciroshi.

Gabaki daya sunyi mamakin yadda autan hajiya ya girma inba kasani ba kai ka rantse shidin yayan maryam nema ba ummi bama.

Tun saukowarsa ajirgi hajiya na hangoshi ta gilas sai washe baki take aikuwa suna fara tawowa suka fito inda zai hangosu ganin yan uwansa wanda rabonsa dasu shekara uku kenan yasa sanyi ya ziyarci ransa.

Yana zuwa inda suke yai gun ummi wanda tunda ta hangoshi murmushinta yaqi tsayawa hajiya ta zuba musu ido eyya wato abun haka ne yar uwarka ka sani banda uwakka yasaki ummi yazo gun hajiya ya rungumeta yana cewa haba hajiyata aikema kinsan ke nafara gani kinsan kishinta ina kula wani ba itaba har in koma ana mita suka saka dariya baki daya.

Agida ummi ce tai dakinta da gudu ta fito riqe da roba tace qanina bude bakinka yasha kunu waye qanin naki ta dubi Abbakar tace yaya dan Allah waye babba yai dariya gami da daga kai alamar tunani bari in tuna kai yaya ya auta shine auta ya daka tsalle yeeee tasa kuka yaya yai saurin cewa shine qarami tai dariya muktar ya amsa yakalla gami da tabe fuska wannan wace qazantarce ta gallah masa harara gami da amshe abunta tai ciki yai saurin bunta sorry babbar yaya ya amsa ya fara sha Vanana ice cream ce tamai dan yanasanta sosai.

Sai da yai wanka yazo yaci abinci sannan suka hau hirar yaushe gamo yadinga basu labarin qasar waje basu ankaraba sukaga daya duk suka miqe sukai daki dan kwanciya.

Anman hajiya ta daga masa hannu na riga na yanke wukunci dole agoben za'a daura mata aure anman bada kaiba da mahfux shi kuma yaron da kake cewa naka ne koma nawaye na qwaceshi na baima mahfuz tunda shi zai auru uwadda............
[12/31/2020, 5:53 PM] 🅰️ " AXEEX✌🏼 D'🅱️🅾️Y😎: _POST BY GROUP OF HYPE HAUSA NOVELS BOOK WHATSAPP 08064400100_ 📚📚
[12/31/2020, 5:54 PM] 🅰️ " AXEEX✌🏼 D'🅱️🅾️Y😎: *ABBAKAR*

*PAGE 90---10*

*Godiya gareku masoyan books dina inajin dadin yadda kuke karantawa gami da addu'o'inku garenk nagode sosai ina Alfahari daku*

Wajen qarfe bakwai Babbar yayarsu ta iso gidan ganin duk suna bacci yasa tai kitchen ta hada musu kari ita da gaji da sauran masu aikin gidan tana cikin jerawa Hajiya ta fito itada ummi ummi ta daka tsalle yaya saikar yaishe tun jiya nazo kunyi bacci gami da durkusawa ta gaida Hajiya ummi tai waje.

Wajen takwas aunty zainab tazo hajiya tai ta fada dan tace tasan ita tasa dole sukayi irin wannan sanmakon bacin tasan cewa batasan tafiyar duhu hajiya wallahi seda aka idarda asuba muka tawo ahab ai duk daya nan cikin wayo zainab ta basar da batun suka shiga wata hirar.

Gabaki dayansu sun taru a falo suna fira Muktar ya sawko suka miqe suprise suka fada da dan qarfi yasauko yana murna sosai yaji dadin ganinsu.

Durkusawa yai ya gaida hajiya da sauran yayyansa kafin yaya babba tace haba autana come give me a hug i miss u sosai ya manne kai bacin jiya kika qi zuwa taroni auni din kaima haka zainan tasa dariya zonan nawan ya juya qeya bacin kinmin buqulu naso yau inzo katsina ke kuma kika wani diro da sassafe gabaki daya suka sa dariya daman sun san halinsa ba'a iya masa fakar yaya babba yai ya fada kanta yana fadin suprise hug wayyo zai karyani ta fada ya miqe yana dariya zainab ta miqe yai dinning wannan suprise din badani ba akaini a baro suka saka mata dariya.

Ita ko ummu gidan take bi da kallo yayin da wani abu dabatasan ko mene ba yazo ya tsaya mata a wuya ada tasa aranta tabar gidan kenan ko unguwar bazata qara zuwa ba sedai yau tanajin kome za'ai ba wanda ya isa ya hanata shiga.

Kukan karen da taji yafara tashi yasa tai saurin dawowa daga tunanin data tafi ta fara buga gidan daga ciki me gadi yace waye ummulkairi ce ta fada bai dauki murya ha be kuma gane sunanba anman jin mace ce yasa ya bude.

Qofar gidan cike yake da hasken wuta hakan yasa yana budewa ya ganeta yadan saki fuska a'a ummu daman kinanan idonta kuwa ya kuma cikowa da qwalla kamin tace baha Sale ina wuni ya amsa lafiya qalau ban taba zaton ganinki yanzu ba.

Ta qaqaro murmushi wanda kana ganin kasan na yaqene nima baba ban taba zaton zuwa na nanba ya gyada kai kafin ya kuma magana tace Yah nasir kuwa yazo.

Eh yazo da wani dan kyakkyawan yaro gabanta ya fadi cikin rawar murya tace ya fito dashi yace a'a tun dazu inanan banga fitarsa ba to baba bari mu shiga ciki.

Bata jira amsarsa ba suka yi ciki.

Kai tsaye bangaren yan mazan gidan tai gabanta sai faduwa yake zuciyarta fal tsoro ta dai daure ta shiga qofar da zata sada ta da gurin nasu.

Ba qaramin mamaki abin ya bata ba ganin gurin shiru ba kowa dan ada saninta dedai wannan lokacin inkazo gurin cike yake da samari kowa na sabgarsa masu hira nayi masu chat masu tireni dan duk suna da kayan yi.

Hakan yaqara tada mata da hankali da sauri tai dakunansu kai tsaye dakin da tasan na Nasir ne ta nufa ta tura a bude take sedai bakowa duk ta shiga ba kowa tabbas akwai abinda ke faruwa ta fada tai cikin gida.

Ai kuwa afalo ta taddasu tsai tsaye sunyi jugun jugun hajiya nata zazzaga bala'i Nasir ta hanga can nesa azaune hawaye nabin kuncinsa  Abbakar na gefensa yana ta faman wasansa a jikinsa ba abinda ya shafeshi sai lokaci lokaci yakan daga ido ya kalli Hajiya dake faman fada.

Da sauri ummu ta qarasa ta suri danta gami da juyawa  zata fita aiko mahfuz da sauri ya miqe cikin murna yayo gun ya rungumeta tai wani kukan kura ta tankada shi gami da bashi mari ya riqe gun yana kallonta dan gaskiya yaji zafin marin daga hannu yai zai rama kome ya tuna kawai yasauke hannun yana murmushi yaja tsaki gami da fadin kada ka qara kuskuren tabani dan akuya kawai.

Murmushi ya kumayi  yai gabanta ya durkushe yana kuka pls ummu kiji kaina duniya ke kadai zuciyata takeso nasani inban aureki ba mutuwa zanyi ta ja hannun ummi gami da fadin wallahi saidai ka mutu in dagani kadai muka rage aduniya to gwara in mutu ba  aure wallahi inda zaka mutu zanfi kowa farin ciki ta juya zata fita.

Hajiya tai saurin fizgota ganin cikin yaran nata bame iya tsai da ita tasa hannu zata fizgi Abbakar tana fadin inadai yaro jika nane dan haka baki isa kin fita dashi  a gidan nanba kema kanki baki isa ki fita ba aure keda Mahfuz yazama dole.

Fizge rigarta tayi gami da fadin wallahi ko gawata ta fi qarfin auren dan iskan danki tasa hannu ta mareta har ta daga hannu zata rama ta sauke gami da fadin wallahi kinci darajar yah nasir da sauri ta faki idonta tai waje da gudu ita da ummi Abbakar na faman sheqa dariya zatonsa wasa take masa.

Mahfuz ne ya miqe zai bisu saidai jirin da ya dibeshi yasashi faduwa kasa tim da sauri  kowa yayo kansa hajiya cikin tsawa take fadin ku bita ku bita dasauri su muktasir suka miqe sukayo waje dan nemanta saidai fa ina duban duniya batanan.

Ita kuwa ummu tana fita abakin gate taji an rufe mata baki da tsumma haka ma Ummi cikin qarfi aka jawota zuwa dan dakin da ke qofar wajen tanata wutsil wutsil din so ta juya taga ko waye ina abu yaci tura..............

*Da yawa suna min test wasu nakan samu in amsa musu da wuri wasu kuma sai ya jima ina mai baku hakuri kan hakan dan bawai hakan na nufin wulaqanci bane saidai abubuwa sukamin yawa anman kusa aranku F.A.Ya'u mai san masoyanta ne ako ina suke*

*Ban cika qorafi kan readers ba koma ince ni ban taba ba saidai wani abu da yadan fara batan rai dasu shine insun ma magana kadan dauki time baka amsaba wani dan rashin kyautawa irin tasa sai yafara zagi ko faden maganganu marasa dadi hakan bayamin dadi danshi rubutun online sa kaine kawai bawai rashin abinyi ba sai sha'awaryi dan kawai ina rubutu online bashi yake nufin duk sanda kaso ko kika so zaki min magana in amsaba dan kuwa inada abubuwanyi da dama masu mahin manci arayuwata fiye da rubutun online*

*Readers kance writers basu da mutimci musanman na online sai dai kuma yawancin readers masu fadin haka asannu na gane sune marasa mutinci ta yadda suke zagewa su dinga cima mutun mutinci beji ba be gani ba.*

Ruwa Hajiya ta shafawa mahfuz a fuska ya farka a gigice yana fadin hajiya karki barta ta tafi dan Allah inban aureta ba bazan iya rayuwaba hankalinta yai matuqar tashi.

Malan ka ishemu da kuka da kasan kanasanta kai sana diyar barinta a gidan nan mansur ne ke fadin haka hajiya ce ta daka masa tsawa yai shiru yana dan qunquni.

Shiko nasir jin su muktasir sunce basuga su ummu ba hankalinsa ya tashi dan tazararsu da futarta beci ace har ta bacema ganinsu ba.

Miqewa yai zaiyi waje hajiya tace ina zaka mara san yan uwa dan uwanka na wani hali zaka fice yadawo jiki ba kwari ya zauna.

Mahfuz ne ya miqe hajiya bari kawai inje gidan da take in roqota hajiya ta zaunar dashi kayi haquri yanxu dare yayi gobe maje da sassafe inyaso sema mu tafi da masu daura muku aure inma acan zata zauna ita taji shidai Nasir abin duniya duk ya isheshi ji yake kamar qirjinsa zai tsage zuciyarsa ta fito tausayin ummu duk ya cika masa zuciya.

Gidan su Abbakar.

Gidan cike yake da farin ciki kana shiga zaka san tabbas yau suna cikin farin ciki shi kansa Abbakar wasai yake jin kansa bakamar kwanakin baya ba da zuciyarsa take cikin kunci duda farin cikin da suke ciki yanzu koya ya tuna da ummu da nahfuz sai gabansa ya fadi dan baijin zai iya rayuwa batare da ummu ba saidai baijin zai iya auren matar da Amininsa yake masifar so yanajin zai iya sadaukar da komi akan abokinsa ada duda zatonsa natana da aure yanajin wataran zai iya aurenta tunda yayi yayi ya cire santa ya kasa saidai tun lokacin da ya gano ita mahfuz yake so yasa ma ransa koda zai mutu ya haqura da ita.

Kamar kullin tun zuwan muktar hutu yau kwana hudu kenan gidan cika yake da yan zuwa sannu da zuwa dare yayi kowa ya miqe yai makwansa cikin shauqi da farin ciki haka shima Abbakar saidai yana tura qofar dakin ya nemi farin cikin ya rasa haka kullin yake dan da ya zauna shi daya shikenan tunanin ummu ne ke cika shi in bacci yake baccin cike yake da ummu

ya rasa yadda zaiyi addu'a kullin yake kan Allah ya temake shi ya cire masa ita aransa anman kamar addu'a yake Allah ya qara masa santa.

Juyi kawai yake akan gadon hawaye na bin fuskarsa yama kasa rufe idansa dan ko rufewa yai ita yake gani tana masa murmushinta me ratsa zuciya.

Gidan su mahfuz da sassafe ya farka dan be niyar komawa ba bayan yin asuba saidai bacci barawo yai gaba dashi ko wanka be ba yai dakin hajiya dan dama ya dade da dawowa bangarenta.

Qofar a bude take ya tura ya shiga ko taisheta beba tana zaune tana lazimi yace haji pls taso mu tafi ina tace yadan zaro ido kin mance gidan ummu taja tsaki kabari sai anjima dan ita dan kawai tana san mahfuz ne sosai shi yasa take iya haqurin jin sunan ummun dan batasan ransa ya baci anman a haqiqanin gaskiya ta tsani yarinyar sosai.

Hajiya inbazaki ba ni zani ta miqe muje suka fice sai da suka biya gidan malan habu suka daukoshi shida almajiransa guda hudu masu jire masa dalibai dan daura auren.

Bakwai dedai a gidan ta musu sunsha bugu kafin Farida tazo ta bude tana murza ido alamar bacci tana fadin ummu badai yanxu kika dawo ba sai dai ba ummu ta gani ba tadan zaro ido tana ja da baya.

Hajiya da mahfuz da sauran mutanen suka shigo suka tsaya hajiya na bin gidan da kallo ba lefi yana da kyau sosai da kuma dan girmansa.

Mahfuz ne ya daure yace ina ummulkairi pls Farida tace wallahi tun jiya da ta tafi dauko danta a gidansu bata dawo ba what ya fada pls karki mana qarya ta ce sabida me zan muku qarya.

To me yasa baki nemeta ba taja tsaki kaji malan taya zaka zo ka isheni da tambayoyi.

Nasir Hajiya ta kira tace ya sameta gidan ummu gin tana gidan da sassafiyar nan ya daga masa hankali hakan yasa yashararo mota ya tawo Allah ne kawai ya kawoshi lafiya.

Koda yazo ake fada masa ai tun jiya bata dawo gidanga hankalinsa ya kuma tashi cikin tsoro da rawar murya yake tambayar Farida.

Farida dan Allah ki fadan gaskiya da gaske bata dawo ba ta gyada kai cikin kwalla dan itama yanzu hankalinta ya tashi wallahi yaya bata dawo ba ta kirani bayan wajen awa uku da tafiyarta tace ai an dai daita komi yanxu dan haka a gidan zata kwana salati ya saka Farida me yasa baki kirani ba tace ai saida ta bani kai a waya ka tabbatar min hakane batunta innalillahi wa'inna ilaihirraji'un ni kuma Farida wallahi muryarka naji.

Aikuwa mahfuz yai kansa ya shaqeshi yana fadin wallahi saika fito min da masoyita mugu

kawai da sauri Nasir ya fuzfe wuyansa ya tankadashi baya kai malan bansan hauka kabarni inji da abinda ke damuna.

Ita kuwa Hajiya can kasan ranta dadi taji da batan Ummu dan gaskiya batasan ko kadan danta ya aureta dan kawai ta fuskanci in bai aureta ba komi zai iya faruwa zai iya mutuwa.

Wayarsa Nasir ya dauko ya fara kiran Aisha qawar ummu batare da la'akari da cewar ai safiya bace bugu uku ta dauka cikin muryar bacci tai sallama a gaggauce ya amsa bai jira tace komi ba yace Aisha ummu tazo gidanku kuwa ta gyada kai kamar tana gabansa tace a'a me ya faru fatan lafiya bai bata amsa ba ya katse ya fara kiran Fatima ita ma din haka ne duk wadda yake da number dinta ya kira ummu bataje ba.

Jiyai qafafunsa sun kasa daukansa ya tsugunna gami da dafe kai dan yadd yaji yana sara masa.

Duk inda suke saka ran ko ummu taje sunje ba ita ba dalilinta hankalinsu duk ya tashi sun rasa me zasuyi cigiya suka kai gidajen radio.

Hankalunsu bai qara tashi ba sai da police suka tsinci kayan Abbakar da wayarta a wani kango da ake zube shara hijabin ummi anan dan gaba da qofar gidansu mahfuz din.

Gidansu Abbakar

Muktar ke magana yaya wai me nayima Yaya mahfuz ne tunda na dawo baizo ba Abbakar yai dan murmushi kwana biyu bai cika jin dadi ba inajin jikin ne ka bari anjima maje mu gano ko lafiya to yaya yace.

Abi ne dan gidan zainab keta sukuwa kan muktar yanata wasansa ta sauko dauke da jaka Abbakar ya miqe ya amshi jakar qanwar an an gama shiryawa tai dariya bari yaya babansu Abi ne yace lallai lallai inshiryo in dawo gida nayi nayi yabari in sati biyu yaqi.

Yadan zaro ido sati biyu tab ai kwana biyar dinma yayi qoqari wallahi inni ne ai kwana daya ma sai ikon Allah zakiyi tadan zaro ido tab kaji yayan nan kace kulle zakayi yai dariya no ba haka bane kawai dai ni atsarina ba zuwa akwana ko kai dare tab matarka ta banu koda yake kai ko yar budurwar ma baka da ita gabansa ya fadi ya tuno da ummunsa yai saurin cire sa din yaha fadin ba tawa bace azahiri yai dariya haka nace miki bani da ita.

Ta zauna yawwa yayana nakaina fadamin ya miqe to sarkin san gulma bazan fada ba yai waje da kwatin nata dan kai mata mota.

Wajen biyar Abbakar da muktar suka fito dan zuwa gidansu mahfuz bayan tafiyar zainab.

Gidansu mahfuz.

Yadda Abbakar yaga mutanen fidan basa wani nishadi kamar da kana ganinsu kamar marasa lafiya yasa yasha jinin jikinsa kasan tuwarsa mutun bame san shiga sabgar kowa ba yasa ya basar yai bangaren hajiya.

Sun gaisa ba tabo ba fallasa ta fara tsokanar muktar a mutanen qasar waje haka ka girma jibeka kamar bakaine ka tafi kana dan tatsitsi sukai dariya gabaki daya.

Abbakar ne ya miqe yai dakin da yasan mahfux ya koma yabar yajiya da muktar suna ta fira.

Kwance ta taddashi yana kallon fanka sake faman wulwulawa wanda har Abbakar ya zauna mahfuz baiji shigowarsa ba.

Saida ya tabashi ya dawo dedai ya muqe zaune Aminin yaushe kashigo yaidan murmushi yanxinnan tunanin me kake cikin kwalla yace ummu gaban Abbakar ya fadi to me ya sameta.

Ummu ta bata what ya fada gami da miqewa yaushe me yasa baka fadanba cikin tashin hankali yake maganar mahfuz ya dafa shi kaima ka damu ko aminin nasani daman nasani Abbakar dina me damuwa da abinda na damu dashi ne.

Wai garin ya ta bace din nan mahfuz ya bashi labarin komi hankalinsa ya tashi jiyai jiri na dibarsa yai saurin zama gami da riqe kai shikenan an sace masa ummunsa wataqilma yan yankan kai suka tafi masa da ita.

Bai taba zato da tsanmanin haka yake san ummu ba irin tanzu yasan yanasanta da yawa anman yadda zuciyaraa ke bugawa hawaye na bin fuska bama yajin me mahfuz ke fadi yasa ya tabvatar indai ummu da gaske ta bace ansace ta komi zai iya faruwa gareshi.

Miqewa yai zaiyi waje jiri ya dibeshi dishi dishi yake gani yai karo da bango nan yayo baya luuuu yai qasa mahfuz ya miqe yayo gunsa yana kiran sunansa.........
[12/31/2020, 5:54 PM] 🅰️ " AXEEX✌🏼 D'🅱️🅾️Y😎: _POST BY GROUP OF HYPE HAUSA NOVELS BOOK WHATSAPP 08064400100_ 📚📚
[12/31/2020, 5:54 PM] 🅰️ " AXEEX✌🏼 D'🅱️🅾️Y😎: *ABBAKAR*

*100---110*

Cikin sauri ya dago shi mamaki ne ya kamashi ganin Abbakar na murmushi daurewa Abbakar din yai ya miqe sannu mahfuz take cewa kawai ya gyada kai badai kaji ciwo ba ko ya kuma yin murmushi haba yar wannan faduwar sukayi dariya duka Abbakar yai waje majfux na biye dashi.

Muktar ne ya miqe yaya har ka fito eh naga magariba ta kawo kai saida suka gaisa da mahfuz shima ya masa tsiyar girma da yayi suka fito dan barin gidan.

Tafiyama dagyar yake yinta dan qarfin hali kawai yai anman dishi dishi yakeji gashi har yanzu jirin be gama sakinsa ba.

Masallacin sake qarshen lokon yai bari in je masallaci kaje ka fadawa Hajiya nashiga masallaci kartaga mun dade inyaso sekayo alwala ka tawo to yaya yace yai gida.

Yana shiga masallacin ya zube ya dade riqe da kansa kafin ya iya kwantawa sai da ladan yafara kiran sallah ya miqe yana bin kiran sallah din yai waje danyin alwa.

Koda ya yayo alwala dinma komawa yai ya kwanta yama rasa meke damunsa dan ayanzu bazai iya cewa ga abinda ke damunsa ba shi dai yasan kawai baya da lafiya.

Ita kuwa ummu tana fitowa daga gidan rasa inda zata tayi tayi qofar gidan da gudu jin datai an kamota yasa ta kwalla qara jin qararta yasa aka rufe musu baki dakin me gadin gidan taga anyi dasu zullo kawai take tana qoqarin juyowa dan ganin waye ya riqeta ta kasa.

Muryar baba me gadi taji yana fadin zan bude miki baki anman dan Allah kar kiyi qara gyada kai ta shiga yi alamar to ya saki hannunsa kafin tace wani abu yace karku fito ina zuwa.

Gurin gadinsa ya koma ya zauna yana zama saiga su muktasir tambayarsa suka shiga yi koyaga ummu eh yace musu naganta sun hau wani adai dai ta sahu da yazo wuce oppps suka fada gami da komawa cikin gidan seda suka jima da komawa ya miqe yai dakinsa.

Ummu ce cikin kuka take tambayarsa me yasa ya kawosu nan yai shiru kafin yace inda na barku kun fice tabvas kuwa zasu ganku su kamoku kuma dolene ki auri mahfuz din tadan kalleshi da mamaki wato duk yasan me ke faruwa.

Kamar yasan abinda ke ranta yace tun wancan lokacin naso temakonki saidai bani da dama yanxu ki miqe zansa akaiku titi inyaso saiki koma inda kike da zama to tace masa gami da masa godiya yasa dansa yakaita har titi suka hau dan sahu zuwa gidan ta.

Koda suka koma gida farida ta rufe gidan han yasa tabaima ummi Abbakar ta bude gidan tace su jirata a farfajiya tai cikin gidan.

Ahankula ta ke tafiya hartai dakinta ta dauko ATM dinta da yan kayan Abbakar sai takardun secondary dinta da sauran takardunta masu mahin manci da kala uku na kayan ummi ko nata bata dauko ba takulle dakin tai waje.

Saida ta kulle gidan sannan ta amshi Abbakar ta goyashi ummi ta kalleta anti ina zamu qauyenku tace can zamu can zan koma ummi.

Shi ko Abbakar bayan an idar da sallah yaita roqon Allah yasa ummunsa tana da rai cikin qoshin lafiya ya bashi lafiya kodan yasamu damar nemota ganinta da jin tana cikin qoshin lafiya

koda bata matsayin matarsa ji yake yafiye masa wannan batan nata.

Sai isha ya koma gida bayan ya danji dadin jikinsa.

Abun duniya duk ya isheshi gashi ba sch balle ta tambayi qawayenta da ya saba ganin su tare gashi shi bashi da number din kowa.

Gidajen yada labaru washe gari ya kai cigiya gamida police stations yini daya tak duk yabi ya fada kana ganinsa kaga maras lafiya idanunsa duk yayi tsuru tsuru hankalin hayarsa gabaki daya ya gama tashi gashi tambayar duniya yaqi fada mata meke damunsa.

Inma ta tambayeshi sai dai yai dariya yace haba hajiya nifa wallahi gaskiya na fada miki ba abinda ke damuna kedai kawai kike ganin na fada anman garau nakeji na.

Mahfux ne zaune wani abu ne yabi ya tsaya masa arai ya kuma kasa gane dalili bakuma komi ke damunsa ba yadda yaga Abbakar gabaki daya ya kasa zaune yakasa tsaye yana wani nuna yafi shi jin zafin bacewar ummu yarasa dalilin Abbakar nayin haka.

Yanke shawara yai na yaje yasameshi ya fada masa me yasa yake abinda yake kan bacewar masoyiyarsa.

A qofar gida ya sami Abbakar yanajin radio ganin mahfuz yasa yasaki fuska gami da kashe radion sin gaisa gami da qara jajanta wa juna batan ummu.

Maganar da mahfuz yai ne tai mugun baima Abbakar mamaki cewa yai Wai Aminin mene naka nawani ishisshirewa wajen nemo ummu jibi yadda kabi kawani jeme wanda duk ni ya kamata inyi haka matsayina na masoyinta me shirin aurenta.

Dariya Abbakar yai masoyi manya ka mance ni kuma masoyinka ne aini me damuwa da abinda ka damu dashi ne mahfux ya washe baki hakane fa.

Kuma banda abinka mahfuz ka mance ummu frnd dina ce da muka shaqu achat ko ka mance aiko dan shaquwarmu na damu ko mahfuz ya daure fuska bai shiru ba ya qara da cewa kuma kamance ita student dina ce wadda ada nasota kamar raina naso aurenta.

Cikin fushi mahfuz ya miqe kai malan dakata bansan rashin mutunci haba dole ka damu mana tinda abar sanka ta bace Abbakar ya miqe gami da dafa mahfuz haba Aminin bakaji nace Ada ba yaje tsaki gami da ture hannun Abbakar din ya qara da cewa to tsaya kaji wallahi kama cire ta aranka inba haka ba zan rufe ido na cire amintar mu wallahi in cima mutinci kai barifa kaji akan ummu zan iya kawar da mutun wallahi.

Ido kawai Abbakar ya bishi dashi yakasa cewa komi ganin yadda mahfuz ya mance da shi waye dinsa kan mace yahau ci masa mutunci.

Atsaye ya barshi soro ro kawai yana kallon ikon Allah.

Ita ko ummu sun hau dan sahu kan yakaisu tasha suna cikin tafiya ummi ta dubi ummu tace auty zuwa qauyenmu da matsala ta dubi ummin me yasa.

Cikin kuka take magana wallahi in mukaje koro mu zasuyi me yasa sabida ummana bata gidan Abbana sai abinda umma rahane ta ce masa ita tasa aka kawoni ma aikatau shiru kawai ummu tai tama rasa abinda ke mata dadi.

Can ummi tace sai dai mutafi magarya inda ummana ke aure ummu batasan sanda ta rungume ummi ba ta farin ciki.

Me dan sahun har ciki yakaisu shi ummu ta roqa ta baima kudi ta kira farida ta bashi kan shine nasir kasantuwar tana bacci yasa bata dauki murya ba.

Dubu hudu ta bashi yaita godiya suka shiga motar da sukaji tana kiran babura magarya saura mutun biyu da sauri suka shiga.

Mota na shirin tashi tacema kwandas dan Allah ga dari biyar tukwici ga kakarbi wannan kasiyon sim da kati na sauran canjin ba shiri ya amsa ya tafi.

Bai jima ba ya dawo dauke da sim da kati ta amsa tana godiya gami da cire na kan wayarta tasa sabon.

Goma dedai motarsu ta tashi dan barin kano wani hawaye ne ya tawowa ummu dan gabaki daya bata taba zaton kwai rana irin wannan da zatazo mata ba ace wai ita take shirin guduwa tama koma wata qasar ba tare da sanin koma nata ba tunda magarya Niger ce wayyo ni ummu naga rayuwa...........

Sunyi nisa sosai a mota masu bacci nayi masu kalle kalle nayi cikin masu kalle kallen harda ummu gabaki daya ji take ranta babu dadi ji take kamar tasa motar ta tsaya ta sauka.

Duda kasantuwar garin yanayin sanyi gashi dare ne kukan tsin tsinye kawai kakeji gwanin dadi sai dai ita gun ummu ba abinda ke mata dadi baccin ma kwata kwata batajinsa juyawa gefenta tayi taga ummi nata sharar baccinta ta kalli hannunta inda danta ke maqale a qirjinta shima baccinsa yake har yana dan murmusawa akaro na biyu da tausayinsa ya cikata.

Tun randa aka miqo mata shi cikin zanin goyo randa ta haifeshi bata qara jin tausayinsa irin na yau ba aranta take qara tausaya masa koya zai tsinci rayuwa inya girma ko zai iya jure qalubalen dake gabansa wata kwalla ce ta zubo mata tai saurin gogeta duda kasantuwar motar da duhu ba wani zaiga hawayen ba.

A dai tashar babura suka yada zango inda da yawa a tashar zasu kwana dan daya tayi suma motarsu anan zata kwan kafin gobe ta tashi zuwa magarya.

Ba haka ummu taso ba taso cikin daren nan subar Nigeria sai dai ba yadda ta iya duda hankalinta bai yi zaton wani zaiyi tunanin suna jigawa ba balle azo babura nemansu hakan yasa ta dan samu damar yin bacci.

Da safe kafin mota ta tashi da yw na cikin motar tasu anan babura zasu sauka hakan yasa sai anyi lodi ummu barin ummi da Abbakar tayi ta fita dan nemo musu abinda zasu ci.

Sai da taje ta ciro rabin kudin account dinta ta sayo kaya kala hudu duda ba wasu masu kyau bane sai dai sun fi babu.

Sha daya dedai ta musu agarin seda suka hau mashin yaqarasa da su.

Yanayin garin ba qaramin firgida ummu yaiba qauye ne sosai ji take daqyar zata iya rayuwa a garin sedai babu damar komawa tunda ita bata da kowa wanda suke natan su sika fara gudarta.

Ai kuwa innar ummi tai murna sosai da ganinsu mijinta baya nan ya fice tun safe sai mahaifiyarsa sin gaisa cikin mutunci musan da ummu ta bata tsabar biredin da tayo musu tai ta godiya.

Malan tanimu shine sunan mijin innar ummi ko da ya dawo shima yai murna da ganin su ummun ba dan komi ba sai shima anbashi tsabar biredi harda madara yaita murna yana sa albarka duk ya mance da kishin da ya debo ana fada masa diyar matarsa ce tazo.

Yau satin su ummu biyu a gidan har sun fara sabawa da rayuwar garin dan hat ummu tai qawa me suna mero sun saba sosai dan mero mutince me san mutane kullin Abbakar na gunta hakan yasa ummu qara santa abinka da uwa kunsan ance in kanasan abin gurin uwa to kaso danta.

Yau malan tanimu mahaifiyarsa ta zugeshi tas hakan yasa ya fito yanata tafka bala'i yaha kiran ummu ita da ummi da gudu ummi ta fito riqe da Abbakar ahannu dan ummu bata nan mairo ce ta jata zuwa niyame dan canzo kudinta daga na nigeria zuwa na niger.

Kayan su yake watsowa waje ni na gaji da zamanku a gida tun ina kawaici na fiskanci baku fuskanta ba haka kawai bani nai cikin kiba ki dawo min gida da zama to wallahi bazai yiwu ba.

Kuka take tana roqonsa ya yadda ummu ta dawo yaqi ita kuma inna ta qi ko fitowa daga daki balle ta bashi haquri ya kyalesu azahiri ba qin fitowa tayi ba kasan tuwar ummi yar fari kuma da sanin halin mijin nata yasa taqi fitowa dan tasan in tai magana zai iya hadawa da ita ya kora.

Ummu ce tai sallama ta shiga ganin me ke faruwa yasa ta shiga da gudu aikuwa ya daka mata

tsawa cikin muryarsa ta buzaye dakata daga nan kubar min gida ynx ynxunnan durqusawa tayi tana kuka tana roqonsa kinga malama wallahi sai kun tafi kinjini ko.........

Nigeria

Yau watan ummu guda kenan da bata har sun koma sch inda zasu shiga level 4 su Aisha duk sun sauya kullin tunaninsu ko ummu na lafiya gashi sinyi sabo sosai da Abbakar dinta da sunga yaro sai suga kamar shi.

Zaune suke suna tattauna lecture din yau dan ta musu wuya wayar maryam tai qara ta dauka wata qara ta saki tana fadin ummu me yasa kika gujemu da sauri Fatima ta amshe wayar danjin wace ummun ce.

Ke banza wallahi wayarku bata da anfani inji ummu na dade ina kiranku ace akashe wallahi kin daga mana hankali sosai wallahi Aisha ta amshe wayar pls ummu ina kika shiga kin tafar mana da yaron mu wallahi munyi missing dinsa sosai eyye wato ma shi bani bako eh mn tunda ke haka kikaga ya fiye miki pls ina kuka tafi kedai bari kawai muna Niger what niger fa kika ce wa kika sani acan tai dariya mutanen azziki mana dil wayar ta katse kiran duniya taqi shiga sikai saving din number din gami da ci gaba da tattauna matsalar rayuwa sinma mance da lecture din yau din.

Yau littinin Abbakar ya yanke shawarar kiran qawayen ummu dan yaji ko zai sami labarin ta tinda yasan mata sau tari suna daukan abota da mahin mance sukan fadawa abokansu sirrinsu.

Ai kuwa yana gama lecture yace Fatima keda qawayenki su Aisha ku samen a office aikuwa hankalinsu ya tashi sosai dan tunda ya shigo suke surutunsu gashi kuma agaba suke zaune ko tsoeonsa basa ji jin abinda yace ne ya sa sukai zaton hukuncin surutu zai musu.

Sun jima a Bus stop sina jiran mota bata zoba gashi office dinsa a old side yake can physics department miqewa sukai danyin yellow bus stop ko zasu samu.

Mota ce ta tsaya gabansu dan rage musu hanya ganin me motar yasa hankalinsu ya tashi Abbakar ne tsuru tsuru sukai suka kasa shiga ya leqo kufa naje jira dasauri suka shige gabaki daya baya duk su shiga wata kan wata dariya suka bashi ya juyo ke Hafsa keda Aisha ku dawo gaba da sauri suka fito suka koma gaba jiki na rawa dan tsoronsa sukeji sosai dabashi bane banajin zasu shiga motar.

Adai dai gurin parker motocin staff ya fakar motar suka fito da sauri sukai gun office dinsa.

Sunfi minti goma a tsaye bezoba fatima da hafsa suka hau mita aiki kawai yazo ya shanya mutane a guri kamar bashi ya ce muzoba ya kuma daukomu.

Basu ankaraba sukaga yana bude office din suka hau kwalalo ido beko kallesu ba yai

shigewarsa ciki.

Kasa shiga sukai daqyar Halima da Amina suka fara shiga kafin daga bisani sauran su bi bayansu.

Yadda sukai zuru zuru ya bashi dariya duda ransa babu dadi.

Daman batun qawarku zan muku ko kun san inda take ko wacce tace bata saniba rabonsu da ita tun kan ai hutu bakomi kuje kawai suka fice sin sin dan har yanxu jikinsu da zuciyarsu be gama yadda da kan ummu ya kirasu ba.

Abbakar ne zaune a office dinsa abin duniya duk ya isheshi mahfuz ya dena shiga sabgarsa ga hajiyarsa ma kwata kwata fishi take dashi dan yaqi fada mata meke damunsa.

Alamun kwan kwasa kofar da yaji ne yasa shi dawowa daga dogon tunanin da ya tafi gami da fadin yes shigo aka shigo da sallama.

Captain din su ummu ne wanda ada kullin se yagansu tare da ummun sir daman assignment dinne an hada ya fada yana miqo masa ok ajiyesu nan.

Har yakai bakin qofa yaji ance Ahmad da sauri ya juyo dan yayi mamakin sanin sunansa da yayi danshi yasan kawai lazy yake cemasa ko a inane ko waya ya masa kan yasanar da yan class dinsu wani abu zaiji yace lazy ayi kaza da kaza.

Daman maganar qawar zanwa saida gabansa ya fadi wake nan Ummul khairi yadan zaro ido wadda ta bata eh ita pls badanni ba inkasan inda take dan Allah ka fadan.

Shiru yai na dan wani lokaci kafin yace jiya tamin waya dai sai dai ni bata fadan tana ina ba ya fada miqewa Abbakar yai what me tace ma to cewa tayi kawai ta bugo mu gaisa to muga number din sir ai unknown ce number din tayo hidden eh mugani kawai zanso gani ya fada yana miqo hannu jikin Ahmad ya hau rawa dan azahiri qarya yake bata boye number dinba ta kuma fada masa inda take rasa abin yi yai sai ji yai ya daka masa tsawa ba dakai nake bane baisan sanda yace tace min tana niger..........
[12/31/2020, 5:54 PM] 🅰️ " AXEEX✌🏼 D'🅱️🅾️Y😎: _POST BY GROUP OF HYPE HAUSA NOVELS BOOK WHATSAPP 08064400100_ 📚📚

[1/13, 4:16 PM] 🅰️ " AXEEX✌🏼 D'🅱️🅾️Y😎: *ABBAKAR*

*110---120*

Niger

Waje ya kora su ummu tana kuka ummi na kuka kayan da ta riqo a hannu kawai ta dauka

sukayi waje ya banko qofar kwanon langa langansa yai ciki yana ci gaba da mita da fada.

Sun dade a tsaye hankalin ummu atashe tama rasa abinda zatai gidansu mairo qawarta ta nufa.

Mairon na tsakar gida suna ganin kayan da ummu ta siya mata sai murna take shigowar ummu ta ja hankalinsu da sauri ta miqe tai gurin ummun tana tambayarta me yasa ta kuka.

Cikin kuka take musu bayani hankalin innar innar mairo ya tashi ita da kishiyarta can innar ta nisa mero ba kince tana da kudi ha eh inna to kinsan malan wato mijin innar ummi da san kudi taje ta bashi wani abin zai bari tazauna kinga nan daki biyu garemu daga nawa sai na antinki.

In munce zata zauna anan ba guri tunda kuma kullin cikin sauyin daki kuke ran kwana na ku koma daya dakin ran kwanan ta ku dawo nawa kuma duk atunkushe can din ne dai da guri shiru ummu tai kafin tace to inna kije ki masa bayani zaifi fuskantarki to shikenan muje.

Har sunkai bakin qofar gidan ummu taja ta tsaya Innar mero ta shiga aiko yana ganinta yayo kanta da fada inma kinzo dan ban haquri bazan haqura ba gida nawa dole su tafi.

Ni ba haquri nazo baka ba shawara ce kasan yarinyar da sukazo da yar matarka qawar mero na ce ko ya gyada kai alamar eh kafin yace to ni me yashafen da abotarsu eyye to ka tsaya kaji mana.

To mero ta sanar min yarinyar me kudi ce sosai dan yanzu ma daga niyame suke da suka fita tun safen nan sunje sun maku siyayya kuma ta fadawa meron nawa inta dawo zata baka yan wasu fam inaji fa sun kai dubu hamsim na garinsu Nigeriya ya zaro ido kai innar mero tai dan murmushi dan ta gane ta shawo kansa to ai ba kai daya tace zata baima ba har gwaggwo dije ta sayoma shadda sai alokacin gwaggwo tai magana wai to tn inane maza kije kice ta dawo in bazai bata daki ba ni sai inkaita gidan bala wato qaninsa da sauri yace kinji inna wane bala kuma daman ke kika sa na koresu.

Da sauri innar mero ta kira su ummu suka dawo ciki gwaggo ita da shi suka maida musu kaya aikuwa ta basu kayan da ta sayo musu shaddoji ne sai atamfa kala uku uku innar ummi kala biyar sukaita murna.

Ta zaro kudi ajakarta ta hannu ta baima malan jiki na rawa ya amsa yana lissafawa dan tun da yake bai taba riqe kudi masu yawan wadannan alokaci guda da sunan nasa bane gwaggo ma aka irgo aka miqa mata miqewa tai ta hau murna harda rawa.

To ke yar nan me yasa tun farko baki fada mana ke attajira bace tai murmushi ai gwaggwo lokacin da mukazo kudin Nigeria ne dani yau naje na samo canji kudin ku.

Innar ummi na jinsu hankalinta duk atashe sai dai suka shiga daki ta fito tai dakin su ummun.

Nigeria

Cikin farin ciki Abbakar ya zagayo ya dafa Ahmad yaushe ta kiraka tun wancan satin anman wallahi ni bata fadan wace unguwa take ba kuma inna kirata din bata shiga kwata kwata.

Ban number din ya tsaya qunquni zaka ban ko kuwa yai saurin daukowa ya miqa masa wayar nemomin number din ya dubo masa ita.

Tabas code din Niger ne wata +227 murmyshi ya saki aqallah yanxu yasan inda ummunsa take ya miqa masa wayarsa yace ka iya tafiya Ahmad ya fice cike da mamakin me malamin nasu zaiyi da number din ummunsa.

Sai da Ahmad ya fita Abbakar ya fara kiran number din sedai da gaske ne bata shiga hankalinsa atashe ya fara tunanin yadda zaiyi gobe ya ganshi a Niger.

Gashi farkon semester can ya yanke shawarar daukar hutu dan tun da ya fara aiki be dauka ba shaidar bashi da lafiya ya bada yana buqatar hutu dan neman lafiyarsa aranar ya bada komi zuwa gobe yake saka ran ayi signing.

Yai muguwar sa'a yasamu anyi masa komi aiko yai murna sosai tunanin me zai cewa hajiyarsu ya haushi dan yasan koya sha giyar wake be isa yace mata neman mace zai je gari har ya Niger.

Ko agida rasa me ke masa dadi yai yai uban taquri adaki iyakar tunaninsa ya kasa tunanowa ummi ce ta shigo dakin nasa riqe da littattafai tana kiransa yah kana ina ne kwata kwata bejita ba.

Ta shigo dakin yanayin da ta ganshi yasata yada books din ta qaraso gurin tana tambayarsa lafiya.

Hawayen fuskarsa ta hau goge masa jin haka ya dawo dashi daga tunanin da ya fada adan razane ya kalleta zatonsa hajiya ce.

Ummi lafiya naga kina kuka ta kalleshi yah tun dazu fa nashigo baka ganni ba kanata hawaye yai dariya na tuna da baba alhaji ne tai dan dariya yah pls yau daya ka fadan damuwar dan Allah ya kalleta tunda yake be taba ganin qanwar tasa ta zama serious irin yauba yai mamaki haka kawai yaji yana san fada mata.

Kimin alqawarin ko muktar bazaiji ba wato abokin taqwaitakarta. Dan shine amininta.

Allah yaya bazan fadawa ko hajiya ba ma yai murmushi kawai kafin ya bata labarin komi game da ummu har ya zuwa hutun da ya dauka.

Ta nisa cike da tausayin yayan nata yah kawai kacema hajiya a faculty dinku aka turaku maryam Abacca da ke Niger din dan yin wani research ai zata yadda be san sa'adda ya rungumeta yana murna ba that's my little sis shawarar ki tayi sosai wallahi ya dagata yana murna.

Itama dariya take ganin yayan nata cikin farin ciki.

Ya sauketa ta dauko books dinta yah pls aikinnan zaka koyan ya amsa ransa fal farin ciki ji yake kamar ma yaje yaga ummunsa sun dawo tare dan yaci alwashin inyaje tawo da ita zaiyi ya kawowa hajiyarsa ita.

Cikin jin dadi suke karatun sosai ummi take ganewa muktar ya shigo riqe da rake yabi littafin da kallo ke ynx wannan ne se an koya miki ta watsa masa harara ni sa'arkace yasa dariya to da sa'ar wace eyye.

Abbakar yace kai bansan rashin kunya fa bata girmeka bane ya kuma yin dariya da kwana biyun danma ta tureni ne ta fito ai da tuni ni zan fara fitowa Abbakar ya harareshi ko awa daya ne dole ka vata girma tunda ta girmeka dai bakaji kai hajiya ke cewa auta ba ummi ta saki qara kai yaya nicefa auta Muktar yai mata gwalo andai fi sona ta miqe ta bishi da gudu Abbakar yasa dariya yana san qannensa da yawa ya shuge toilet.

Hajiya na daki tana lazimi Abbakar ya shiga ya maya bayanin komi duda gabansa sai faduwa yake dan ba sabon sa hane qarye tsoronsa karta gane aikuwa yai sa'a bata fuskanta ba sai saka albarka take da addu'ar Allah ya sa adace ya kiyaye hanya.

Washe gari da sassafe a filin jirgi ta masa dan ta sama zai tafi tara dedai suka tashi .

Basu wani jima ba suka sauka a filin jirgi na Niger dake maradi Abbakar ji yake kamar atake yana saukowa daga jirgi zaiga Ummunsa.......

Niger

Waje ya kora su ummu tana kuka ummi na kuka kayan da ta riqo a hannu kawai ta dauka sukayi waje ya banko qofar kwanon langa langansa yai ciki yana ci gaba da mita da fada.

Sun dade a tsaye hankalin ummu atashe tama rasa abinda zatai gidansu mairo qawarta ta nufa.

Mairon na tsakar gida suna ganin kayan da ummu ta siya mata sai murna take shigowar ummu ta ja hankalinsu da sauri ta miqe tai gurin ummun tana tambayarta me yasa ta kuka.

Cikin kuka take musu bayani hankalin innar innar mairo ya tashi ita da kishiyarta can innar ta nisa mero ba kince tana da kudi ha eh inna to kinsan malan wato mijin innar ummi da san kudi taje ta bashi wani abin zai bari tazauna kinga nan daki biyu garemu daga nawa sai na antinki.

In munce zata zauna anan ba guri tunda kuma kullin cikin sauyin daki kuke ran kwana na ku koma daya dakin ran kwanan ta ku dawo nawa kuma duk atunkushe can din ne dai da guri shiru ummu tai kafin tace to inna kije ki masa bayani zaifi fuskantarki to shikenan muje.

Har sunkai bakin qofar gidan ummu taja ta tsaya Innar mero ta shiga aiko yana ganinta yayo kanta da fada inma kinzo dan ban haquri bazan haqura ba gida nawa dole su tafi.

Ni ba haquri nazo baka ba shawara ce kasan yarinyar da sukazo da yar matarka qawar mero na ce ko ya gyada kai alamar eh kafin yace to ni me yashafen da abotarsu eyye to ka tsaya kaji mana.

To mero ta sanar min yarinyar me kudi ce sosai dan yanzu ma daga niyame suke da suka fita tun safen nan sunje sun maku siyayya kuma ta fadawa meron nawa inta dawo zata baka yan wasu fam inaji fa sun kai dubu hamsim na garinsu Nigeriya ya zaro ido kai innar mero tai dan murmushi dan ta gane ta shawo kansa to ai ba kai daya tace zata baima ba har gwaggwo dije ta sayoma shadda sai alokacin gwaggwo tai magana wai to tn inane maza kije kice ta dawo in bazai bata daki ba ni sai inkaita gidan bala wato qaninsa da sauri yace kinji inna wane bala kuma daman ke kika sa na koresu.

Da sauri innar mero ta kira su ummu suka dawo ciki gwaggo ita da shi suka maida musu kaya aikuwa ta basu kayan da ta sayo musu shaddoji ne sai atamfa kala uku uku innar ummi kala biyar sukaita murna.

Ta zaro kudi ajakarta ta hannu ta baima malan jiki na rawa ya amsa yana lissafawa dan tun da yake bai taba riqe kudi masu yawan wadannan alokaci guda da sunan nasa bane gwaggo ma aka irgo aka miqa mata miqewa tai ta hau murna harda rawa.

To ke yar nan me yasa tun farko baki fada mana ke attajira bace tai murmushi ai gwaggwo lokacin da mukazo kudin Nigeria ne dani yau naje na samo canji kudin ku.

Innar ummi na jinsu hankalinta duk atashe sai dai suka shiga daki ta fito tai dakin su ummun.

Nigeria

Cikin farin ciki Abbakar ya zagayo ya dafa Ahmad yaushe ta kiraka tun wancan satin anman wallahi ni bata fadan wace unguwa take ba kuma inna kirata din bata shiga kwata kwata.

Ban number din ya tsaya qunquni zaka ban ko kuwa yai saurin daukowa ya miqa masa wayar nemomin number din ya dubo masa ita.

Tabas code din Niger ne wata +227 murmyshi ya saki aqallah yanxu yasan inda ummunsa take ya miqa masa wayarsa yace ka iya tafiya Ahmad ya fice cike da mamakin me malamin nasu

zaiyi da number din ummunsa.

Sai da Ahmad ya fita Abbakar ya fara kiran number din sedai da gaske ne bata shiga hankalinsa atashe ya fara tunanin yadda zaiyi gobe ya ganshi a Niger.

Gashi farkon semester can ya yanke shawarar daukar hutu dan tun da ya fara aiki be dauka ba shaidar bashi da lafiya ya bada yana buqatar hutu dan neman lafiyarsa aranar ya bada komi zuwa gobe yake saka ran ayi signing.

Yai muguwar sa'a yasamu anyi masa komi aiko yai murna sosai tunanin me zai cewa hajiyarsu ya haushi dan yasan koya sha giyar wake be isa yace mata neman mace zai je gari har ya Niger.

Ko agida rasa me ke masa dadi yai yai uban taquri adaki iyakar tunaninsa ya kasa tunanowa ummi ce ta shigo dakin nasa riqe da littattafai tana kiransa yah kana ina ne kwata kwata bejita ba.

Ta shigo dakin yanayin da ta ganshi yasata yada books din ta qaraso gurin tana tambayarsa lafiya.

Hawayen fuskarsa ta hau goge masa jin haka ya dawo dashi daga tunanin da ya fada adan razane ya kalleta zatonsa hajiya ce.

Ummi lafiya naga kina kuka ta kalleshi yah tun dazu fa nashigo baka ganni ba kanata hawaye yai dariya na tuna da baba alhaji ne tai dan dariya yah pls yau daya ka fadan damuwar dan Allah ya kalleta tunda yake be taba ganin qanwar tasa ta zama serious irin yauba yai mamaki haka kawai yaji yana san fada mata.

Kimin alqawarin ko muktar bazaiji ba wato abokin taqwaitakarta. Dan shine amininta.

Allah yaya bazan fadawa ko hajiya ba ma yai murmushi kawai kafin ya bata labarin komi game da ummu har ya zuwa hutun da ya dauka.

Ta nisa cike da tausayin yayan nata yah kawai kacema hajiya a faculty dinku aka turaku maryam Abacca da ke Niger din dan yin wani research ai zata yadda be san sa'adda ya rungumeta yana murna ba that's my little sis shawarar ki tayi sosai wallahi ya dagata yana murna.

Itama dariya take ganin yayan nata cikin farin ciki.

Ya sauketa ta dauko books dinta yah pls aikinnan zaka koyan ya amsa ransa fal farin ciki ji yake kamar ma yaje yaga ummunsa sun dawo tare dan yaci alwashin inyaje tawo da ita zaiyi ya kawowa hajiyarsa ita.

Cikin jin dadi suke karatun sosai ummi take ganewa muktar ya shigo riqe da rake yabi littafin da kallo ke ynx wannan ne se an koya miki ta watsa masa harara ni sa'arkace yasa dariya to da sa'ar wace eyye.

Abbakar yace kai bansan rashin kunya fa bata girmeka bane ya kuma yin dariya da kwana biyun danma ta tureni ne ta fito ai da tuni ni zan fara fitowa Abbakar ya harareshi ko awa daya ne dole ka vata girma tunda ta girmeka dai bakaji kai hajiya ke cewa auta ba ummi ta saki qara kai yaya nicefa auta Muktar yai mata gwalo andai fi sona ta miqe ta bishi da gudu Abbakar yasa dariya yana san qannensa da yawa ya shuge toilet.

Hajiya na daki tana lazimi Abbakar ya shiga ya maya bayanin komi duda gabansa sai faduwa yake dan ba sabon sa hane qarye tsoronsa karta gane aikuwa yai sa'a bata fuskanta ba sai saka albarka take da addu'ar Allah ya sa adace ya kiyaye hanya.

Washe gari da sassafe a filin jirgi ta masa dan ta sama zai tafi tara dedai suka tashi .

Basu wani jima ba suka sauka a filin jirgi na Niger dake maradi Abbakar ji yake kamar atake yana saukowa daga jirgi zaiga Ummunsa.......
[1/13, 4:16 PM] 🅰️ " AXEEX✌🏼 D'🅱️🅾️Y😎: _POST BY GROUP OF HYPE HAUSA NOVELS BOOK WHATSAPP 08064400100_ 📚📚
[1/13, 4:18 PM] 🅰️ " AXEEX✌🏼 D'🅱️🅾️Y😎: *ABBAKAR*

* PAGE 120---130*

Shima kansa me motar kasa tsayar da motar yai ko kauce min nidai tunda na daga ido na hangi motar ban qara sanin inda kaina yake ba.

Bu de ido kawai nai naganni a gadon asibiti da mamaki ne ya kama ni Yah Nasir na gani riqe da hannuna da alamu Bacci yake atsorace na fizge hannuna shima a tsoracen ya miqe yana dubana yana fadin sannu kin farka ki nutsu kinji daga masa kai kawai nake bawai dan na nutsun ba.

Sai da ya tabbatar na nutsu ya gyaran ruwan dake jikina kafin ya fara magana tun jiya ina kan hanyata ta dawowa na bugeki ganin kece da yanayin da naganki ko dankwali babu balle takalmi ya dagan hankali me yasa ki fitowa a haka.

Cikin kuka nake masa bayanin komi sai dai gabaki daya na kasa fada masa cewar ciki ne ya bayyanar min shi yasa suka koren sai tsintar kaina nayi da ce masa kawai dan munyi rikici da mahfuz ne suka koren shiru yai kafin yace ai shikeban ki cigaba da haquri hajiya mahaifiyata ce kinga bazan iya sata ko hanata ba.

Kawai dai nasani ina tausayinta da yawa banso ace lokacin da take neman afuwarki

bakyanan ko lokaci ya qure mata kallonsa nai da mamaki dan banji akwai time in da Hajiyarsu zatayi na dama harta roqen.

Miqewa yai zan turo wata ta zauna agunki ko gida banjeba tun jiya to kawai nace har ya fita ya dawo karki damu bazan fada musu na ganki ko nasan inda kike ba daga masa kai kawai nayi ya fice.

Ko agida ba wanda ya masa maganar ummu shima bema wani ba yadai kintsa yai dakinsa kawai.

Ummu na kwance wata matashiya ta shigo wadda batafi shekara ashirin da hudu ba ta zauna sannu ko yawwa nace mata tace baki sanni ba sunana Salma nice wadda Yah nasir ya turo to nace mata na cigaba da kwanciyata.

Kwana ba uku da Salma takanje ta dawo tazo ta ciga da zama dani ita din mutunce mai raha ga surutun tsiya dole na saba da ita muke fira sosai kai kace mun dade sosai da ita.

Aran na biyar aka sallameni hankalina ya tashi sosai inata tunanin yadda zanyi ko ina zani oho.

Yah Nasir ne  yazo ya tafi damu ji nake kamar intambayeshi ina zai kaini kawai dai nadaure nai shiru hirarsu suke da salma sosai har mamaki abin ke ban dan banyi zaton yana magana ko ta minti biyu ba nayi zaton daga eh sai a'a yafi fade saidai hard kwashewa da dariya.

Wani gida naga munyi parking a dedai shi Salma ta bude ta shiga shima futowa yai har ya je bakin qofar ya dawo futo mana na futo na bishi jiki ba kwari.

Gida ne qarami mai kyau dedai zaman amarya ko ince nace daya da yaranta ya birgeni gidan duda alokacin duk raina a bace yake.

Zaune muke a falo yah nasir yana min bayani nan ne gidan da zaki zauna wannan sunanta salma yar Kaduna ce tana karatunta anan Buk so batasan zaman hostel sai ta kama haya na roqeta ne kan ku zauna tare ta kuma yadda murna nai sosai nagode mata aqallah yanzu ina da gurin zama.

Washe gari duk wasu kayan da mace kamata ke anfani dasu yah nasir ya sayon sai dai kayan sawa ne kawai duk dogayen riguna ne nai masa godiya ya tafi.

Ko zuwa yai gaisuwa kawai ke hadamu sai dai suyi ta firarsu da salma tun inta sani bana shiga har nafara sakewa dashi sai gashi ko batanan yakan zauna muyi fira har ya tambayen yan matsalolina.

A hankula yake kawon yan abu buwa na masu mahinmanci dake gida kaya ne dai yace inyi

haquri dasu ahankula zai dinka wasu banji komi ba nace to.

Yau kam murna nake sosai dan yau yah nasir ya kawon wayata kullun da ita nake kwana nake tashi inata so ince ya daukon sai dai ina jin nauyinsa sai gashi ya kawon agida ba wanda yake da number ta dan haka baice in canza layi ba kawai dai ya amshi number ta ya ajiye a wayarsa.

Tunda ya fita naje nasata a caji 10% kawai tayi na kunna ta kamar yadda na zata message din Abokina ne ya fara shigowa bansanshi bantaba ganinsa ba anman azahirin gaskiya mun shaqu dashi sosai achat kawai muka hadu tun ina SS 1 muke chat dashi a Facebook.

Farkon haduwa ta dashi in ban mance bashine lokacin da Baba mahmood yai tafiya wato yayan mahaifina tsaraba shine waya da ipad sai yan sauran tarkace nai murna sosai duda ni bansan me zan dasu ba.

Washe gari na gama komi na kinkimi kayan tsaraba a jaka nai gidansu Walida wata Aminiyata yanxu tana Malaysia tana karatu tun bayan candy dinmu, ta tayani murna sosai kafin ta bude kwalinsu ta saka su a caji muka ci gaba da firarmu.

Wayar ce ta fara cika ta kunna mun muka sha selfie kafin ta dauko tata wayar dan ita tun muna Jss 3 take da waya ta ciro sim daya kin ga wannan sabo ne jiyama na siyoshi nai masa sub na 2month bari in bude miki email account ta budemin sannan aka buden Facebook da WhatsApp lokacin shima bai cika gari ba duk yawanci 2go mutane sai facebook din nai mata godiya ta rakoni gida dan maqota muke nai gida ta koma gidansu.

Da daddare bayan naci abinci na gama aikina kawai na dauko wayata na kunna data banbi takan WhatsApp na shiga Facebook nafara duba posting din mutane na dariya in dariya na tsaki inyi tsaki.

Tun budemin account da Walida tayi kullin sena hau facebook sai dai ba na magana da kowa banma taba shifa inbox dina ba, kusan kullin sena duba posting din mutumin har yazame min jiki dan posting dinsa masu ma'ana ne ko joke yai inka duba sosai sai kaga abin anfana.

Nakanyi commenting sosai aduk post dinsa wanda na rasa abin cewa kuma nakanyi liking.

Yau ina zaune bani da data kawai dai inabin previous post ne na mutane ina kallo sai dai nai nai gabaki daya suyi loading sunqi iya goman farko ne kafin Data ta ta qare kawai inbox na shiga inda ban taba gwada shiga ba sai yau tsawon wata biyu da fara chat dina.

Duba mutanen da suka min magana na shiga yi kamar me naga nashi manar sai dai nai nai ya bude yaqi hakan yasa na gane rashin data ne kudi na ciro daga account dina ta waya na kira walida.

Pls ya zanyi ne insai data tawa ta qare tai dariya eyye ai dayake data ce yau kin kirani tunda kikai waya baki taba kirana ba nai dariya to ni kirana kike eyye nan ta basar ta fadan yadda zanyi.

Kashe wayar nayi na sai Data din dan ganin saqon nasa sallama ce afarko sai qanwata shine kikaqi karbar request dina ko dan murmushi nayi duda kuwa bansan me yasani ba sauri nayi naje nai accepting dinsa.

Na koma nace amsoryy yanxu naga saqon sai dai me naita jiran replay shiru.

Sai da aka kwana uku sannan ya turo tun daga time din muka saba sosai harta kai ga ya amshi wayata dan yace shi yana japan yana karatu mukan gaisa hakan yaqara qarfafa shaquwarmu saidai abu daya ke hadani dashi in yace yazo hutu yaushe zamu hadu saima inkashe wayar indena hawa online gabaki daya sai na dedaici ya koma.

Yauma din tambaya ce qanwata kwanaki da yawa kin dena hawa online inna kira ki bata shiga ko dannace miki na dawo kenan nai murmushi kawai dan bani da amsa din bashi.

Bai cika tambayata abinda ya shafi personal life dina ba duda shi yakan dan fadan wani abun da ya shafeshi duda ban cika cewa komi kaiba.

Online na hau na bashi haquri mukasha firarmu.

Zaman gidan Salma ya fara gundurata gashi inaso inma yah nasir magana kan karatuna dan alissafina yanxu shine dedai lokacin da ya dace ace an fara admission duda nasan ba lallai insamu jami'a ba tunda nasan banyi post UTME ba sai dai nakasa.

Yau aunty Salma suke final paper murna take sosai duk yan nima ina tayata ji nake dama nice ita da sassafe taimin salma ta tafi makaranta.

Sai yamma liqis ta dawo daga makaranta ina zaune ina sana'ar chat dina ta shigo ta fada kaina tayani murna little sis exam tayi dadi kai anman nayi murna fatan Allah yasa adace tace amin kamin tace kuma Allah yasa afara asa'a nakalleta kawai bance komi ba.

Washe gari Tace in shirya zamu unguwa na shirya cikin doguwar riga yah nasir yazo ya tafi damu tafiya muke sosai mamaki na shiga yi ganinmu a BUK Aunty salma ta juyo ta kalleni kina mamaki ko nai saqare ina kallonta ta miqon takarda surprise na karba ina bude emblem din admission letter ce tawa bansan sa'adda na saki qara ba inamasu godiya.

Screening Mukaje ranar kam munna ba'a magana kowa yaganni yasan ina cikin farin ciki nan naqara san yayan nawa ashe shima yasan abinda nakeso wato in zama engineer godiya har gajiya yai da yimasa.

Bayan convocation dinsu anty salma ta koma gida qanwarta da batafi sa'a ta ba tazo itama tare zamu fara karatu inda ita zatayi MBBS su suna tsohon makaranta mu muna sabuwa.

Watanmu daya da fara lectures akayi bikin aunty Salma sai yanzu na gane alaqarsu da yaya Nasir ashe budurwar Amininsa ce da shi yake can university of ibadan yana koyarwa shi yasa yah nasir kular masa da ita har kaduna mukaje gurin bikin tai ko murna sosai.

Akan hanyarmu ta dawowa be naita sheqa amai ga zazzabi lokacin cikina watansa uku da wasu kwanakin hankalin yah nasir shida farida ya tashi sosai asubuti mukaje inda aka bashi tabbacin ai ciki gareni hankalinsa ya tashi danni ban fada masa ba agida kuma baiji ba dan bai taba tambayar inda nake ba.

Zuwa yai ya titsiyeni in fada masa gaskiya wayamin nan nafada masa ai dalilin korata da akai kena yaita fada me yasa tun farko ban fada masa ba ai da tuni ya zubar nidai nai shiru dan daman zubarwar ne banaso ayi.

Da muka koma gida yai yai inyadda azubar naqi ya haqura ya qyaleni kawai.

Shine ya dauko min ummi diyarki dan min akace akace tunda ga ciki ga karatu ita kuma farida itama ba zama ta cikayiba tunda tare yawanci ma muke fita nakanma rigata dawowa wataran aiki duk yabi yamin yawa.

Karatu yana zuwa mn da sauqi dan ba qarya ina gane abu indai an koyan gashi kuma yah nasir na iya qoqarinsa na koyamin.

Lokacin da muka fara lectures na rage chat cikina bai fito ba sai dai yana dan ban wahala haka nake jurewa akwai wani malaminmu maisuna Abbakar tun gani na dashi na farko naji inasansa sai dai shi din irin malaman nanne da ko dariya baya yi magana ma kamar siye yake sai yaga dama yakeyi ni kadai nasan me ke damuna game dashi.

Ko gaisheshi nayi sai yaga dama yake amsawa kallo ban isheshi ba balle insa ran zai soni inna koma gida bani da aiki sai kuka in dare yayi musanman duk lokacin dan cikina ya motsa na tuno da malaminmu sai kukana da tsanar yah mahfuz ta cikan rai dan nasan babu tayadda za'ai yasoni balle ya aureni tunda masu mutunci da basuyi cikin shege bama suna nuna masa so abanza.

Lokacin da na haihu yah Nasir yasama yaron mahfuz ni kuma azahiri na tsani me sunan shi yasa nace da nawane ni Abbakar nasa masa bai ce komi ba yadai qi kiransa da Abbakar sai mahfuz yace in yaro ya girma ta zabi sunan da yake so.

Sati biyu da haihuwar Abbakar yah nasir ya kawon takardar gidan da muke ciki ya bani yace yanzu yazama nawa watansa guda da siye so dama yake sai na haihu nai nai ya karbi abinsa

yace ina inya mutu kuma ina zani nai murmushi kawai dan baisan inada kudi da yawa ba.

Koda yake lokacin da mahaifinsa ya bani ATM dina yace kudadena suna ciki in ina buqata ba wanda ya sani dan yasan halin matarsa ko sauran yan uwansa bai fadawa ba.

Yadai min kwatance inda wani abokinsa yake yace sauran abubuwa na da inda zan sami mahaifiya duk innaje zan samu dai dai ni ban taba bi takan hakan ba dan ban dauki abin da mahinmanci ba.

Lokacin da nahaihu ne Abokina Abbakar ha facebook ya takura sai mun hadu dole na nemi izinin yah nasir ya yadda dan daman yasanshi dan har gausawa sun tabayi munyi dashi zaizo inbashi shawara dan nasaba bashi shawara yaji dadinta sai dai yace alokacin yafiso muhadu face to face dan matsalarsa babbace.

Lokacin da na fita dan ganinsa sai ganinsa nai da yah mahfux wanda daman yace min da amininsa zaizo dan yasha fadamin kusancinsa dashi abu nagaba da ya tsoratani shine ashe shine lecturer dinmu danake masifarso.

Koda na koma daki na shige nakira tah nasir na fada masa komi yazo ya kori yah mahfux da Abbakar matsayin besansu ba duda dakewa kawai yai.

Lokacin da rikicin yah mahfux yai qarfine kan waini masoyiyarsa ce yasa yah nasir samo wani amatsayin mijina  kanni bani bace ummun da yasani dole hajiyarsa ta yadda yasamu tabuwa.

Ganin rikicin mahfux yai yawa yasa yah nasir yanke shawarar aurena duda cewar yasan da nasan irin san da yakema Farida fada mata ne kawai beba danni ya tambaya kan yanake gani nace ai sun dace sosai yace kar in fada mata sai yagama nazari kanta saidai kawai ya bijiromin da batun aurensa.

Naqi yadda danni harga Allah matsayin yaya na daukeshi saidai shawarar da qawayena suka ban na amince zan aureshi dan na yadda bazasu ban shawara mara kyauba  dan tun farkon fara karatuna na basu labarina duka sun tausayamin bakuma su sauyamin ba bankuma tabajin sun fadawa kowa va hakan yasa na yadda dasu sosai.

Sai dai mahaifiyar yah Nasir taqi yadda qarshema sai cewa tayi ina ita ai aure dole in auri Mahfuz ni kuma ganin haka yasa cikin daren na baro kano ummi tace muzo nan.

Innar Ummi ta nisa gami da share hawaye kiyi haquri Na zargeki kan abinda baki aikata ba ummu tai dariya bakomi inna ai hakan shi ke nufin ke uwa ta gari ce inna tai murmushi kawai.

Wasa wasa Abbakar ya gama karade maradi da yawo yau kwana uku anman ko alamun ummu babu gashi ko hotonta bashi dashi hausar yan garin ba cika ganeta yayi ba gashi su basa jin turanci ma sai France suke ji abin duniya duk yabi ya ishe shi hankan yasa yau ya yanke

shawarar barin maradi zuwa wani garin

Kasuwar grand marshé ya fara shiga dake nan maradin danyin siyayya yan abinda ba'a rasa ba ya siya abinka da namiji bai wata iya siyayya ba ya fito ya koma unguwar da ya sauka mai suna kawo acan yabar duk kayansa sai abinda ba'a rasa ba ya dauka ya tambayi kwatancen tasha yai can.

Mota ya hau da yaji ana kiran niyame niyame bai wata tambaya ba yai shigewarsa shidai burinsa bai wuce yaga ummu ba yakusa minti talatin cikin motar kafin ta cika su yi gaba.

Ita ko ummu inna ce ta dafa ta tace to yanxu ummu zuwanku nan kina ganin shine dadai ummu ta gyada kai to anman me yasa baki nemi wanda mahaifinki yace ki nema ba ada ban niyar nemansa ba to lokacin da naso nemansa sai na tuna da abinda Abbansu mahfuz yace min.

Mutumin lauyansa ne yakuma fada masa duk sanda na nemishi hakan na nufin da wata matsala to ko gidan da su yah Nasir suke ne asaida dan cireni daga matsalar dan gida nawa ne to ni kuma tun kanma ahaifen suke cikin gida tayaya zance injanyo abinda zaisa subar gidan.

Inna ta gyada kai ai da sai kije kimasa bayani ba matsala bace kinaso ne kawai yakaiki gun mahaifiyarki ummu ta share hawaye kamin tace innar ummi ada inaso inje gunta da burina kullin bai wuce inyi candy inje inganta ba dan Baba mahmud wanda yake ayanxu babba agidanmu yasha fadamin zai kaini Jordan innai candy kafin ashiga tsakani na da duk yayun babana yakai yakawo cikinsu ba wanda yasan da zamana ko ya damu dani.

Inaso inga ummata duda ita bata damu dani ba tunda tun randa ta tafi tabarni kafin ta yaye ni bata kuma nemana ba saidai inna banasan inje in tada mata da hankali inna kinsar ba uwadda zata so ace yau diyarta ta haihu dan ya girma kuma bada aure ba inna ta rausayar da kai haka ne ummu.

Amma ga shawara kinsan kudi duk yawansu ana anfani dasu dole su qare kuma in sun qare baki da na baima mijina da sirikata zasu koreku ne ni kuma bazanso haka ba mai zai hana kuje cikin zender ku sassaro kaya inyaso sai kizo kike saidawa irinsu mai magi gishi fulawa dasauransu ki dinga sai dawa tiya tiya rabin tiya kai har gwangwani.

Ummu tai murmushi nagode inna da kika fahince ni kika yadda in cigaba da zama daku gobe sai muje nida meron inna ta miqe ni bari inje in dora sanwa.

Washe gari da wurwuri ummu suka fita su gwaggwo harda bada sauti alhalin ko ficika vata bada ba.

Siyayya sosai ummu tai suka hawo qurqura ta dawo dasu sai yamma liqis suka shigo unguwarsu mai suna unwala, daki gwaggo ta baima ummu wanda zata zuba kayan nata bayan ta vata tsarabar da tayo mata.

Zaman ummu gidan babu wata matsala dan sau da dama ma ita take bada abinda za'a dafa hakan yasa kakejinsu shiru ko fada malan musa ya dena dan zatonsa karyayi ummu ta tattara tabar gidan.

Shi ko Abbakar duk yabi ya gaji tun yana baza ido yaga anzo har ya gaji yai bacci sunyi azahar ahanya anman har lokacin basu isa niyame ba.

Awarsu goma sha biyu a tafe kafin sukai niyame garin ya birgeshi dan yafi maradi kyau da girma da anan tasha aka saukesu kafin ya fito daga motar.

Sai da ya fito daga motar sannan hankalinsa yadan tashi sai alokacin yafa tuna bashi da masauki ga gajiyar da yai sosai shi ba abin ya koma maradi ba wannan uwattafiya haka.

Can ya hango me shayi tafe irin buzayennan yai saurin kiranshi sai da yasha shayin wajen kofi hudu dayake irin qananun kofunanne sannan yadanji dadi ya bashi kudinsa shi kuma yai gaba inda yaga taron matasa gurin wani me saida kasa kasai.

Sai da aka dan watse ya masa salma sun gausa kafin mutumin yace anman dai ke daga nigeriya kike ko Abbakar yai murmushi eh mutumin yai dariya haba koda naji ai daga jin maganarki na huskanta yanzu ina anki zuwa hakanna na cikin almuru.

Abbakar ya nisa nazo neman qanwata ne da tazo nan sedai bansan inda zan sameta ba gashi na gaji da yawa wallahi kuma bani da masauki.

Mutumin yai dariya ayya ayya seki jirani in kammala sai muje can gidana na in baki masauki Abbakar ya washe baki aiko da na gode sosai.

Anan sukai sallah kafin mutumin ya goya Abvakar a mashin dinsa sukai unguwar francophonie wadda nanne mazaunin mutumin me suna muntari.

A gofar gida ya saukeshi ya shiga gida yafi minti biyar sai ga yaro da tabarma ya shimfida masa ya sauna kafin mutumin ya fito da kwanuka a hannu tuwone na gero da miyar kadi ba lefi tuwon da dadi gashi da zafinsa hakan yasa Abbakar yaci ya qoshi.

Adakin zaure inda qanin mutimin ke kwana anan aka sauki Abbakar din.

Kwanar Abbakar biyar agarin nan yaje dik inda zaije sai dai ya rasa gano ummu hankalinsa duk ya tashi sai yanzu yagane bawai zuwa niger dinne wahala ba face gano inda take gashi kusan kullin sai ya kira wayarta wadda Ahmad ya bashi anman akashe.

Sun saba sosai da muntari da kuma qaninsa Basiru yau suna zaune suna fira  duk hirar ummu ce basiru yace anman me yasa baki zuwa zender nemanta tunda naga lokacin da zani fara zuwa nijeriya tacan mukabi ta magarya kuma abokina yace min duk yawanci masu zuwa Niger ta mota tacan suke bi.

Miqewa Abbakar yai ai sai in tafi ma yanzu muntari ya ruqoshi ki bari gobe maje gyada kai kawai yai ya koma ya zauna.

Adaki kuwa ji yake kamar gari bazai waye ba shi ji yake kamar yaga ummu ya gama.

Da sassafe ya kintsa suka rakashi tasha ya hau motar maradi dan sai anje can kafin ya hau motar da zata sadashi da zender sai da ya shiga mota ya leqo yana qara musu godiya sai da motarsa ta tashi sannan suka bar tashar shi kuma muntari yai gurin sana'arsa wato saida fina finai danshi har kano yasani dan yana zuwa sayen fin qofar wanbai.

Kusan irin tafiyar da sukai kafun su zo niyame sukai yanzu ma sai dai yanzu awa goma sha daya sukai.

Nasaukinsa yai inda yabar kayansa dake maradi nan unguwar kawo dan yagaji sosai.

Washe gari ya hau haramar yin zender duk ya bi ya rame abinka da wanda bai saba wahala sosai ba.

Ita ko ummu sana'a ta karbu dan yawancin unguwanni dake nan magarya sun san da zamanta dan ita din kayanta da sauqi sosai ko akasuwa dake birni inkahe yadda take saidawa zaka samu dan ita ba ta riba take ba ta kawai juya kudin take.

Yanxu takai takawo daga unguwar
Ghana, Sabon gari , tudin wada , un franco,mayanka , gawo  da  gamdji, gawon kolliia, château, kai inma akace duk garin magarya ba'ai qarya ba..inka anbaci sunan gidan malan musa da ake sai da komi sai ankawoka har gidan.

Yau wasu kayayyakin sun qare hakan yasa mero da ummi zuwa zender sayowa inda ummu da ummi suka shirya dan zuwa can niyame sayen kaya dan inna tace niyame anfi samunsu da arha sai dai nisa kawai.

Gurin innar mero ummu tabar Abbakar dan yaba musu quya kuma komi yana ci.

Amaradi su ummu suka fara sauka anan tasha.

Abbakar yana cikin mota inda kwandasta ya shiga gami da bugun motar alamar muje fara tafiyar mota kamar ance ya dago ya hanqi wata kamar ummu ita dince ya fada sai dai cikin

mota yagansu motarsu taja da gudu rasa abinda ke masa dadi yai  shi ba abin yace asaukeshi ba anya kai ba ita bace abinda keta kai kawo aransa kenan.

Sunyi wajen awa bakwai a hanya kafin su isa zender nanma agajiye suka isa dagyar yasamu hotel yakama anan din yau kwanansa takwas gashi ko alamun ummu babu gashi sati biyu yacema hajiyarsa zaiyi kawai.

Sai da ya huta atashar da yake basu da nisa da kasuwar dole can ya nufa dan ko zai sami abinda zai ci dan wani irin hotel ya sauka basa baima mutun abinci.

Acan kasuwar ya rasa mai zaici can ya hango wani mai shayi yai gurin yana kurbar shayin da yake da zafi sosai.

Ya dago kenan suka zo wucewa ta gabansa indai ba gizo idansa ke masa ba wannan yarinyar itace mai ma ummu raino tabbas itace kenan yar niger ce kome ya fada gami da miqewa, buzun ya ruqoshi kudina malan ya ciro ya miqa masa.

Saurin shan gabansu yai har yana dan haki sukai saurin tsayawa cikin fada mero ke fadin malan lafiya ummi ce ta dan firgita dan tasanshi azatonta ma shine Mahfuz dan vatasan mahfuz din ba.

Yi haquri baiwar Allah ya fada gami da kallo ummi ina ummu take ta hade rai ni bansanta ba yadan kuma kallonta kafin ya basu hanya su shige.......

Zanci gaba insha Allah
[1/13, 4:18 PM] 🅰️ " AXEEX✌🏻 D'🅱️🅾️Y😎: _POST BY GROUP OF HYPE HAUSA NOVELS BOOK WHATSAPP 08064400100_ 📚📚
[1/13, 4:19 PM] 🅰️ " AXEEX✌🏻 D'🅱️🅾️Y😎: *ABBAKAR*

*PAGE 130---140*

Sai da sukai dan nisa ummi ta dubi mero wannan shine wanda antina ta baki labari ta gwalo ido to me yake anan bakiji yana cewa ina take ba nemanta yaso yi mun shiga uku mero tace kafin tace kinga zo muje mucewa dan bala ya kawo mana kayan gida zo mu tafi.

Abinda basu bani ba Abbakar buye yake dasu har sanda suka gama yima dan bala bayani sukayi hanyar futa daga kasuwar.

Gun dan bala ya koma suka gaisa kafin yace yanaso yakaishi inda zai kai musu kayan dan bala bai kawo komi aransa ba zatonsa ko irin masu sayen kayan da ummun ke sai dawa ne.

Suna tafe a mota dan bala na masa surutun kaima kaima kaji labarin sauqin hajiya ko shi dai eh kawai yake cemasa har suka iso qauyen magarya.

Su kuwa su ummu acan suka yanke kwana dan basu suka gama siyayya ba sai dare jafin su taso suzo maradi ma dare yayi sannan daga nan qara wata uwattafiyar zuwa zender dole sika yanke shawarar kwana gidan wani qanin malan habu mijin inna dake nan unguwar lazare dake nan niyame din.

An shisshigar da kayan dan bala yaja mota yai gaba ummi sin rigasu isowa tama dan jima agida dan harta dora girki danshi Abbakar kan su tawo saida Dan bala ya qarasa sayayyar.

Wata yarinya ce ta fito daga daya gidan dake kallon inda aka shisshigar da kayan riqe da Abbakar ahannunta duda magariba tayi sai da ya ganeshi dan akwai nefa saidai irin jan kwannance bakuma ta cika haske ba.

Zo yace mata tai sauri taje ya amshi yaron dan tabbatarwa ta miqa masa ba musu ya sunansa yace tace Abbakar yadan rungume taron yaiko lif ajikinsa ya miqa matashi jeki ki kiramin ummamsa tai dariya ai batanan tun safe suka tafi niyame sai gobe zata dawo.

Tausayin yaron ya cika shi ace yaro dan qarami haka babarsa ta tafi tabarshi harta iya kwana.

Ganin baice komi ba yasa yarinyar shiga gidan sai dagowa yai yaga bata nan yaci gaba da zamansa a qofar gidan har malan musu ya dawo.

Sai alokacin ya tsaidashi suka gaisa kafin Abbakar ya dora daman nine mahaifin Abbakar dan da suke zaune a gidanka malan musa yadan waro ido da gaske eh yace yajashi cikin gida to me yasa suka barka anan biyoni ciki ba musu ya bishi ciki suka shige.

Kai tsaye dakin inna malan musa yai ya fada mata komi itama ta hau murna ai wai tunda matarsa take da kudi ai sai yama fita kudi sukam karensu ne ya yanke sa'a.

Ummi najinsu ta kuma leqo ta ganshi hankalinta inyai dubu ya tashi ta rasa meke mata dadi ta kuma kasa fitowa duda futsarin da ya matseta.

Gwaggo ce ta je ta dauko Abbakar ta dangashi ahannun Abbakar babba tana fadin Allah sarki dan albarka ashe da uba nasa muke wadin shege ne dan kawai uwatasa nada kudi yasanya bamu wadi gabanata Abbakar yai dan yaqe kawai tausayin yaron da mahaifiyarsa na cikashi.

Washe gari wajen goma na safe gwaggo tai tabi gidaje tana cewa azo aga baban dan ummu aikuwa akaita zuwa.

Su kuwa su ummu basu suka dawo ba sai wajen biyar na yamma duk a gajiye suke daga ita har inna sai da aka gama shigo musu da kayan kafin su shigo gwaggo na zaune ummi a gefenta tana mata tsifa.

Anan suma suna zauna ummi da gwaggo na musu sannu da isowa sai da suka ci abinci sukayi la'asar kafin gwaggo tacewa ummu jiya mijinki yazo atsorace ummu ta ce mijina eh gwaggwo tace yanxu yana ina inji ummu yadan fita shi da dansa.

Dansa kuma eh danki mana ummu ta miqe badai Abbakar nawa ba eh shi kenan nashiga uku an gama dani hankakin inna ma ya tashi to wazaizo har yace shi ne mijin ummun harya dauke mata yaro komdai masu garkuwa da mutanene tunda kowa yasan uwar yaron nada kudi.

Sallamar da sukaji yasa ummu saurin juyawa danko mafarki take intaji muryannan tasan me ita zata kuma iya gane muryarsa cikin maza dari.

Shi dinne riqe da Abbakar dinta akafada da alamu ma yayi bacci tasaki ajiyar zuciya gami da fadin Malan kaine ya akai kazo nan waya fada ma ina Niger ya akai ka gano gidannan duk lokaci guda take maganar yayin da shi kuma ke binta kawai da kallo cike da mamaki.

Nigeria

Tun bayan bacewar da yan kwanaki mahfuz ya ware ya ciba da sabgoginsa inka dauke da daddare da yake kasa bacci dan ko ya rufe idanunsa ita kawai yake gani azahiri inka ganshi zakayi zaton ta ya mance da ita sai dai shi kadai yasan me yakeji aransa daurewa kawai yake yayin da yasaka ido sosai akan yayansa nasir dan yace yanxu ma shi ya boyeta.

Shiko bangaren Nasir hankalunsa yafi na kowa tashi har yau bai dena nemanta ba yabi ya rame yai baqi daman shi ba wani jikin qiba ke gareshi ba.

Gidansu Abbakar.

Ummi ce qanwar Abbakar wadda ita daya kawai tasan me yakai yayanta niger zaune take suna waya dashi yana fada mata irin wahalar da yasha tana ta jimami har ya fada mata ai yau yagano gidan da ummum take sai dai basa nan ta hau murna kai anman yaya nayi murna yaushe zaka dawo.

Ya nisa kinsam damuwata kenan jibi sati biyun da na fadawa hajiya zai cika gashi banma shawo kan ummum ba balle ta yadda ta biyoni.

Ummi tai dariya kai yaya kana ban mamaki kawai ka kira hajiya kace aiki zai iya kaiku irin wani satin yasaki dariya kai wannan yarinyar da wayo kike ta dan turo baki kamar tana gabansa kai yaya nidince yarinya ka manta shekaruna yai dariya kawai sukai sallama.

Gaban ummi ne ya fadi tai saurin miqewa tana fadin hajiya yaushe kika shigo ta watsa mata wani kallo bansani ba wato ummi harkinyi girman da zaki boyen wani abu ko inshi yayan naki

yana ganin yai girman da zai boyen abu ke harkin san ki hada masa qarya ya fadan ko.

Wallahi hajiya ha haka bane ta fada wayar ta dauka ta hau kiran Abbakar gami da barin dakin ummi ta diro daga gadon gami da bin bayan ta.

Niger

Maganar Abbakar ce ta baima ummu mamaki wato murmushi yasaki gami da fadin haba tawan mene hakan daga mun sami yar matsala saiki baro gida ki tawo gari harya Niger kina ganin kin kyauta kenan kinsan yadda nakesan yaronmu jitai qafafunta basa son daukanta taja ta zauna.

Duban inna tayi taga itama din kallonta take alamun tana buqatar amsa tai saurin kawai da kai gami da miqewa ta suri danta dake cinyar Abbakar din tai dakinsu.

Inna ta miqe ta bita aba tana shiga tahau tambayarta ummu daman qarya kike min kinada miji ko ta ce wallahi inna ba miji na bane shine Abvakar dun da nake baki mamaki ni wallahi banmu ma taba maganar soyayya dashi ba gyada kai inna tayi tai waje kawai.

Washe gari masu siyayya sunata zuwa inna ta kira Abbakar dakinta yana riqe da takwaransa yana masa wasa.

Bawan Allah kadubi girman Allah ka fadan gaskiya ummu ta ban labarinta tas ni tacemin danta baida uba bata taba aure kai kuma kazo ka tubure kai mijinta ne ka fadan gaskiya.

Ya kalli yaron dake ta faman bangala masa dariya tausayinsa ya cika shi kafin ya fadawa inna gaskiyar komi ta gyada kai alamar yadda to kai yanzu da ka biyota nan me kake nufi kenan kazo ka dauketa ne ka kaima abokinka ya aura ko kuwa.

Ya karkada kai alamun a'a nazone nan inta yadda zata aureni adaura mana aure a matsayin ada na mata saki dayane aka maida mana da abunmu kodan ruwar mutuncinta anan garin naku da basu san komi game damu ba inna tai shiru shikenam kaje ka sameta kome tace inyaso se inji.

Ko da yaje tana ta hada hadar bada fulawa da za'a siya rasa me zaice mata yayi bama tasan yazo kusa da ita ba yadaure ya matsa kusa da ita dan da kunnenta yai maga ahankula wanda ita kadai zata ji yace ummulkairi inasanki da yawa zaki aureni......

Nigeria

Ita ko Hajiyar Abbakar ko da ta amshi wayar agurin ummi kiran Abbakar ta shiga yi sai dai taqi shiga hakan yasanya ta cillowa ummi wayarta harsai da ta fashe  ummi bata bi takan wayar ba tai gun hajiyar.

Kuka tasa ma Hajiya sai tana roqonta tayi haquri daqyar ta haqura nan ta bata labarin ummun da yake hajiyan tasan ummun sai dai ba wanda yasan inda ta tafi ba dan dayawa suna zaton ko anmaidata gurin mum dinta ne.

Ta tausayama rayuwar ummu sosai sai dai vata nunama ummi sosai ba kawai dai ta haqura da mitar da take.

Muktar ne ya fito ganin idanun ummi ya kumbura yai jane yasa dariya towo ke kuma keda wa ta watsa masa harara ni sa'arka ce eyye shima harararta yai gami da zama kusa da hajiyarsu yakalli hajiya ummata dan Allah me yasa kika ce wannan yarinyar ce ta rigani zuwa duniya.

Hajiya tai dariya to shi kenan inka yadda to ita ta zama auta dun in dena cema auta ummi tasa dariya aikuwa na yadda ya miqe cab ni ban yadda ba wallahi yai waje hajiya ta miqe itama tana dariya tai dakinta.

Ummi ta dauko wayarta duk ta fashe wani hawaye ya zubo mata dan daqyar yah babba ta siya mata iPhone dinnan yanxu ko wata batayi ba ace ta yi raqa raqa haka haushi kamar me.

Yau muktar zai koma dagyar yasamu wayar yah Abbakar sukai salama daqyar Abbakar yasha kanshi ya haqura danshi cewa yai sai yazo sunyi sallama.

Yau ummi tana da test tun safe ta tafi taso sosai ace da ita za'ai rakiyar dan biyun nata har kuka tayi shi kuma sai dariya yake mata duda daurewa yake dan yanajin dadin zaman gidansu musanman rayuwarsu da yar biyun nasa.

Sai da ta tafi ya tuna da suprise din da yai niyar bata hakan yasanya ya faki idon hajiya da yayyensa da zasu rakashi yai makarantar su ummi din.

Sun shiga test gashi sai sunyi awa daya shi kuma qarfe goma zasu tashi ya rasa ya zaiyi kawai yai kasadar shiga ajin.

Cikin sa'a yaya yaya Nasir ne wato yayan mahduz ya kuma sanshi.

yana ganinsa ya danzo bakin qofa yace muktar lafiya ya gaisheshi gami da miqa masa ledar yace yah pls ka baima ummi ina sauri zamu tafi ne ok yace dashi gami da komawa ajin.

Muktar ya daga mata hannu tai murmushi kawai ta ci gaba da rubutunta.

Sauri tayi ta gama duk a burinta na taje taga tafiyar dan uwan nata.

Taxo fita Nasir yace ummi ki jirani anan waje ina zuwa yo tace masa taja ta tsaya kawayenta nata tsokanarta waiko dai ko dai dan ba tun yau sika fara ba tace musu yayanta ne shi yasa

yake sakar mata fiska sunqi yadda dan shi din bama ko yaushe yake dariya ba.

Sai da ya gama karbar papers dinsa tas sannan ya fito haushi duk ya ishi ummi ya miqa mata ledar da muktar ya bashi gashi inji yayanki muktar ta turo baki kai yaya Nasir qanina dai yai dariya shima to gyanbo sarkin san girma yai gaba abinsa, zainab tace oh wow Allah ummi mutumin nan yayi naso nice muke wasa dashi haka tuni zansa masa sona suka saka mata dariya gabaki daya.

Niger

Ita ko ummu daki ta shige da sauri jin magan ganun Abbakar inna ta gani ta zube kan gado tana haki kai kace wadda tai wani uban gudu inna tace ummu lafiya kike irin wannan haki haka.

Cikin rawar murya take magana inna wai malan ne yace zan aureshi inna tai murmushi to me kika ce masa bakomi to kije ki tambaye shi ko dagaske yake inyace eh inaga ki yadda kawai.

Waje ta fice ta ci gaba da aikinta yana kallonta ganin bazata masa magana bane yasa yai waje abinsa riqe da takwaransa.

Sai da ta kammala komi itama tai waje yana can nesa da gidansu yana wasa da Abbakar dinta ta qarasa inda yake din tai sallama ya amsa a ciki ta jima  tsaye baiko dago ya kalleta ba ya ci gaba da abinda yake.

Ganin tsaiwar bazata mata bane yasata zama dan nesa kadan dashi tace malan ina kwana bai amsa ba bakuma kalleta ba taji zafin abinda ya mata ta dai daure ta kuma cewa.

Yah dazu me kace ya dago ya kalleta au bakiji ba eh tace ok kiban amsa tace ai banji me kace ba dan Allah ka maimaita, kinga malama inzaki ban amsa kiban mamaki ne ya kamata lallai mutumin da nuna isa yake.

To taya zan baka amsa banji me kace ba to koma mene nidai amsa kawai nake jira kiban dan Allah ka maimaita wallahi bazan maimaita ba.

To dagaske ne zaka auren ya dago karaf suka hada ido wani yar yaji har cikin kansa yai saurin kau da kai au ashe kinji me nace ta sunkuyar da kai.

To tunda muke dake na taba miki wasa eyye tai shiru kawai kiban amsa zaki aureni to aini na kasa yadda ko da gaske kake yai dan murmushi da bako yaushe yake ba  kin taba ganin anyi maganar aure da wasa.

Tai shiru kamin tace ai naga nidin bakowa zai yadda ya auren ba ya dago ido ya kalleta sabida me ya ta nuna masa Abbakar dake hannunsa yanata wasa yai murmushi kamin yace to ai ni babansa ne kin taba ganin inda mutun yaqi uwaddansa tai shiru can tace to family dinka fa yai

dariya kice dama can su kike tsoro kawai ta sun kuyar da kai basu da matsala yace inma suna da ita ai dani zaki zauna bada suba ko.

Kin amince zaki aureni shiru tai kamin ta miqe tai ciki kawai.

Duk yadda sukai dashi ta fadawa inna ita kuma tace zata fadawa mijinta.

Kwanansu biyu da yin maganar ummu bata ce masa komi ba hankalinsa duk yabi ya tashi to ko bata yadda bane hakan yasa yau yai niyar saminta intaqi amincewa ya koma gida ya kawo Hajiyarsa ta roqar masa ita.

Yana zaune yana cin tuwon da gwaggo tamai dan baya iya shan koko suna ta fira dan sun saba sosai malan musa tazo ya zauna aka ci gaba da firar dashi.

Sai da Abbakar ya kammala kafin malan musa ya fara magana jiya Halima tamin bayani kan kanaso in zama waliyin matarka kan amaida muku da armenku haka ne.

Abbakar yai saurin cewa eh haka ne sabida inasan kawai mukoma Nigeria da aurenmu yai murmushi hakanma yayi kyau Abbakar ya ciro kudi ya baima malan musa ya amshe yana godiya.

Da Azahar malan musa yama liman bayanin komi aka sanar a masallaci kan da la'asar za'a daura auren.

Ilai ana yin la'asar mutane da dama suka shaida daurin auren ummulkairi da mijinta Abbakar aiko angon sai washe baki yake duda ba kowa yasani a garin ba yaci kwalliyarsa takwaransa ma ammasa wanka yana zaune dashi a qofar gida.

Kwana uku da daurin auren  Abbakar da qyar yasha kan ummu ta amince ta biyoshi Nigeria sai da suka biya maradi ya dauko kayansa acanma sun kwana biyu kamin su mamo hanya da yaso yima su ummu visa abin yaci tura dole suka biyo mota bawai dan yaso ba.

Sun iso kano lafiya yakan yasa suka dauki taxi har gida.

Hankalin ummu bai tashi ba saida ta gansu a unguwarsu wato gidansu babanta gidan da ta girma bata qara shiga rudani ba saida ta gansu a lokon cikin tsoro ta kalli Abbakar ya daga mata gira ganin a farkon layin suka tsaya yasa ta gane ba can gidansu suka zo  ba sai alokacin tadanji dadi kadan.

A gidan su Abbakar hajiyarsa ta amshi ummu sosai da mutunci ummu taji dadi sosai sai dai can qasan ranta fal tsoro ne dan tanjin kamar in hajiyar taji Abbakar ya aureta zata tsaneta ganin har dare yayi an nuna mata inda zata kwanta ita da danta Abbakar baicema hajiya ita matarsa bace yasa ta fara tunanin kenan shima yana tsoron abinda zata ce ne.

Sai da ummu ta hau sama yaje ya tabbatar tayi bacci sannan ya sauko yai gun hajiyarsa da tun tashin ummu ta wani hade rai ta fara cika tana batsewa.

Yana saukowa ta haushi da fada ta inda ta shiga bata nan take fita ba yanxu Abbakar yaushe ka koyi qarya haka shi dai hakuri yaita bata hartayi shiru.

Saida tayi shiru kafin ya dora Hajiya wannan ita ce wadda naje nema din kuma na aureta miqewa tayi tana tafa hannaye wato Abbakar harkayi girman da zakai aure bada sani na bako aqallah yaji dan sanyi cikin ransa dan baiyi zaton abinda zata ce kenan ba ya dauka cewa zatai me yasa ya auri ummu nan yaita qaqalo bayani dan shawo kan hajiyar har ya samu ta dan sakko kamin tace shikenan alasa albarka ka tashi kaje anman kasani ni bazan ma kawunnanka bayani ba kasan me zaka fada musu ya sunkuya yana godiya yai bangarensa.

Washe gari gidansu mahfuz yaje da yah Nasir suka fara haduwa sun dan taba fira kafin Nasir din kwana biyu bana ganinka a sch na jejje faculty dinku office dinka arufe.

Abbakar ya sosa qeya na dauki hutu ne nakuma yi tafiya towo ina kaje haka kai da nasani indai ba abu me mahinmanci ba kana baima aikinka time inka eh wallahi yah naje neman ummulkairi ne.

Nasir ya zaro ido wacce ummu ya sosa qeya ummu dai taka kuma ma naganta Nasir ya miqe tana ina a'ina ka ganta.

Naganta a Niger kuma kamin mu tawo an dauran aure da ita yanzu tana gidanmu shaqo Abbakar da akaine ta baya yasa Nasir saurin juyawa Mahfuz ne ashe duk yana sauraronsu.

Cikin fada da masifa yake zagin Abbakar kan yaci Amanarsa yaci amanar abota kan mene zai auri wadda yake so da qyar Nasir ya fincike Abbakar yace ya tafi kamin haniyarsu ta fito da sauri Abbakar ya bar gidan.

Shima kwace kansa yai yabi Abbakar din kan yaje har yashige gida shima gidansu Abbakar din yai dan ba baqonsa bane me gadi yasanshi bai bi ba'asin zuwansa ba.

Yana shiga ya fara kwalawa Abbakar din kira kai Abbakar kana ina ne kafito munafi maci amanar abota ka bani matata Hajita ta fito tace lafiya kake mana ihuu haka yace ni mamata nazo karba.

Hajiya tace wace mata ai matar Habu ce sai dai ko kazo kwace masa matana kawai wallahi Hajiya ummu tawa ce ni daya dan da take goyo nawane in ba tawa bace taya zata haifar min yaro tsawa hajiya ta daka masa futarmin a gida in qwayar ta sakeka ka dawo.

Ya juya zai fuce dan yanajin nauyin hajiyar Abbakar sosai sai dai jirin da ya debeshi yasa shi

dawowa da baya luuuu ya fadi.

Da sauri Abbakar da tun da mahfuz ya shigo yake tsaye ya kasa magana yazo yana dagashi yana kiran sunansa sai dak kamar babu hakan yasa ya miqe ya kira me gadi ya temaka masa suka kaishi mota baibi takan hajiyarsa ba ya asibiti.

Sai da ya tabbatar likitoci sun duqufa kan mahfuz ya koma gida ya dauko Hajiyarsa da ummu shi kadaj yasan me yake rayawa aransa.

Ya bugawa Nasir abinda ake ciki kan ya fadawa hajiyarsu kafin wani lokaci sun iso Asibiti hajiyar mahfuz sai bala'i take.

Sai yanma liqis mahfuz ya koma normal yana ganin hajiyarsa yasa mata kuka Abbakar na shigowa dakin ya fincikd drip din da aka saka masa ya daga drip stand din ya wulla masa fita mugu kawai yana kuka da badan Abbakar ya sunkuya ba da sai yaji masa ciwo.

Da sauri Abbakar yazo ya riqe hannun mahfuz yana kuka haba aminin mene haka yazaka bari mace ta shiga tsakaninmu ya miqe yai inda ummu ke tsaye ya shigo da ita dakin gurin mahfuz ya nufo.

Kamo hannunsa yai yasa na ummu ana mahfux kamin ya share hawayen da ya tawo masa yace ni inasan abokina bakuma zan bari soyayyar mace ta bata mana abotarmu in dai ummu ce ni Abbakar nasaketa saki daya daman ban dora mata idda ba ko yanzu ne a daura muku aure yana kai nan yai hanyar fita yabar ummu tsaye kamar gunki yayin da mahfux ke bin hannunsu da kallo........

Zan cigaba insha Allah
[1/13, 4:19 PM] 🅰️ " AXEEX✌🏻 D'🅱️🅾️Y😎: _POST BY GROUP OF HYPE HAUSA NOVELS BOOK WHATSAPP 08064400100_ 📚📚
[1/13, 4:20 PM] 🅰️ " AXEEX✌🏻 D'🅱️🅾️Y😎: *ABBAKAR*

*140---150*

Fun cike hannunta ummu tayi cikin kuka take magana wallahi banasansa ba kuma zan aureshi ba ko gawata bazata zauna dashi ba yayin da Abbakar cikin qunar rai yai waje danshi kadai yasan mai yakeji aransa ji yake kamar girjinsa ya tsage zuciyarsa ta fado.

Hajiyarsa ce ta matsa inda ummu take dan tun dazu da Abbakar in ya kamo ummu ta biyosu dakin takuma ji komi.

Dafa ummun tai tace ki dena kuka kimki indai ina raye ba zaki kuma maraicin uwaba indai ina raye ba wanda ya isa ya aura miki mahfux duda shima dana ne anman kema yatace.

Tace cikin murya mai kaushi Habu dakata yaja ya tsaya taje ta juyo dashi yana kallonta tana kallonsa tace indai ni na haifeka inaso yanzu ka maida ummu amatsayin matarka ya kalleta zai yi magana tace karka cemin komi wannan umarni ne nake baka bawai shawara ba dan haka kayi abinda nace.

Cikin rawar murya yake magana na maida mata ta ummu hajiya ta saki ajiyar zuciya kamin tace kuma wallahi ko bayan raina kasaki ummulkairi kan Mahfuz bazan yafe maka ba zan iya maka afuwa in kan wani dalili ne.

Ta juya ta kalli hajiyar mahfuz kamar zatai magana kawai taja hannun Abbakar da ummu sukai waje sai kace qananun yara.

Suna fita Mahfuz ya muqe zai bisu hajiyarsa ta gyada masa kai alamar a'a kar yaje ya dawo ya zauna gami da rushewa da kuka yana fadin wannan wacce irin jarrabar so ne nake miki ummu hajiya ki temaka ki ko ragen santa ne dan Allah ta dora kansa a qirjinta tana lallashi kamar wani yaro.

Sai da su Abbakar suka isa gida hajiya ta ja ummu sukai daki suka bar Abbakar nan tsaye yana kallonsu sai yanzu ya gane kuskurensa lallai ya tafka kuskure yasan ko zai hadiyi laya ummu bazata yadda yanasanta ba zatayi zaton tafi san abokinsa kanta bacin ba haka bane yasan duniya bayan hajiyaraa it yakeso bema san me yasa ya ce yabarma mahfuz din ita ba can wani bari na zuciyarsa yace sabida kaima kanasan kyautatama aboki ka koda sau daya ne.

An sallami mahfuz dan ba wani serious abu bane, agida mahfuz mahfux duk yabi ya tashi hankalinsa ji yake kamar ya kashe kansa ya wuta dan dai kawai yana tsoron jahannama ne ya daure anman ji yake gabaki daya duniyar ta masa zafi.

Kwance yake akan gadonsa yana kallon fanka da take ta faman kadawa idanunsa na zubda kwalla ji yake kamar yaje ya sato ummu ayanzu ma azuciyarsa tunani yake tayi inda zai satota ina zai kaita santa ne ita da danta keta ruruwa aransa.

Hajiyaraa ta shigo ganin yana kukan ne yasa tai saurin yin gurin tana fadin subhanallahi haba mahfuz mene haka karka kashe kanka kan wata banza dan Allah, ya dago a fusace hajiya ummu ba banza bace masoyiyata ce to naji me yasa ka kuka.

Cikin shessheqar kuka yake fadin hajiya yarona inasansa wallahi in na rasa ummu bazan iya jure rashin dana ba hajiya ta dafe qirji wane yaro kuma kaida ba mata ba.

Hajita dan gurin ummu wallahi yarona ne ni nayi cikinsa tai saurin rufe bakinsa kul yi shiru vaka da wani da Allah ya rufa mana asiri shine kakesan tonawa indai yaro kakeso zanma aure sai matar ta haifa maka wani abin da yasa hajiya bata damuba da jin kalaman Mahfuz kan dan ummu sabida tasan halinsa tun futowar cikin tasan shi yayi da gaske din tsanar ummu da tai da san zuciya yasa taqi yadda.

Shiru yai kamin yace wallahi ni shi nakeso inasan dana nasan na cuce shi nasa an haifeshi bada aureba anman wallahi yanxu inasansa inasan riqeshi matsayin nawa.

Yace wallahi hajiya inasan yarona nasan ko yara dari zan haifa bazan dena sansa ba inasan amsoshi in nuna masa gata in sauya masa suna daga Abbakar zuwa mahfuz dan Allah ki yadda.

Da qyar tasha kansa ya yadda zai aure bawai san dagaske ya haqura da yaron nasa ba .

A can gidansu Abbakar na dai babu dadi sosai dan hajiya ta rage shiga sabgarsa zaman faloma ba cikayi tayo ba kusan ko yaushe tana daki ita da jikanta Abbakar qarami inyaje tayi kicin kicin tace me ya kawoshi, ummumma kullin idanunsa cikin sam ganinta suke sai dai baya ganinta inma yaganta daga ina kwana, barka da rana ko barka da dare shi kenan sai tayi dakinta.

Yakan kwan uku bai ma ganta ba abubuwa kawai yinsu yake babu dadi.

Yau Abbakar baya nan ya tafi aiki dan sun koma mid semister yanaso yai qoqari ya qarasa ma dalibai lectures insu da tunda ya tafi hutu malamin da aka sauya musu ba wani zuwa yake ba basuyi wani abin kirki ba.

Ummu na zaune suna kallo dan ita din ba me yawan magana bace hajiyan ma haka hakan yasa basu cika fira ba Abbakar qarami ne kan hajiya yanata dab dalarsa.

Su Aisha kabir ne suka shigo da gudu ummu ta miqe tai gunsu ta fada jikinsu Fatima ta tureta dalla ni mataa bakisan haushinki nakeji ba baki daukemu aminai ba lokacin da kika shirya guduwa kika daqa mana hankali tai gurin hajiya suma suka tureta sukai gun hajiya ta tatsaya tana kallonsu kawai kafin itama tai gurin.

Sun gaisa da Hajiya ummu ta mata bayaninsu kafin tajasu zuwa dakinta suna shiga ta shiga musu kuka dagar tai shiru sun rasa kukan me take.

Cikin kuka ta basu labarin komi har aurenta da Abbakar sukai ta murna to mene na kuka ai naga shi din mutumin kirki ne, kukan asarar sch dina danai nake yanzu fa sai na sake jamb fa na kuma jira, Aisha ta miqe af kin ganmu ko munata fira da baqo fa mukazo wakenan ba gurinki yazo ba tai waje ummu ta bita da kallo kawai.

Gurin Hajiya tai tace hajiya mun mance da baqo mukazo yanasan ganinki hajita tace towo baqo kuma waye kenan.

Eh muda Yah Nasir ne hajita tace Nasir kuma wanne Yah nasir dai na ummu na gidansu mahfuz........

Hajiya ta danyi shiru kamin ta nisa tace to me yasa be shigo ba banda a abin Nasiru da dayake shigowa ai ba wani ke masa iso ba kosan zainab mutuniyar tasa bata nan.

Wato zainab qanwar Abbakar duda kasancewar Abbakar ya girme mata anman tanasan yayan nata sosai fiye da kowa agidan dan haka duk girmanka in ka tabashi ka banu abinda ke hadata da Nasir kenan indai ya daki Abbakar sai tazo qofar gida ta labe indai nasir ya zo wucewa ta jefeshi ta gudu ya biyota har gida ya daddaketa.

Lokacin da ya qara girmane batafi shekaru goma ya dena dukanta sai dai in yaganta yace ke tsattsewala tasa kuka duda har yanxu in abu ya hadashi da Abbakar ya daddakeshi sai ta masa rashin kunya.

Data girma mutunci ya shiga tsakaninsu karatu ma da Abbakar ya tafi waje karatu shi yake koya mata dan basa shiri da mahfuz ko kadan dan ta ganshi yanashan taba ita kuma indai kanashan taba ta dena ganin girmanka yayin da mahfux mutun ne me dan banzan san girma.

Jeki kice ya shigo tai waje suka shigo tare Aisha ta dauki qaramin Abbakar sukai cikin dakin ummu Nasir ya zauna yana sun sun da kai.

Sun gaisa kafin hajiya tace yanxu Nasiru dan zaka shigo gidannan shi ne sai anma iso da wani kema yadan sosa qeya yana murmushi yayi kyau   yanzu yaushe rabonka da gidannan ina zaton tin haihuwar zainab ta farko da tazo wankan gida ya sosa kanshi gami da sun kuyar da kai wallahi abubuwa sukamin yawa.

Eh haka ne shi yasa ai kake iya zuwa katsina ziyara yai dariya ni kuma ga hanci ga baki baka iya zuwa sabida abubuw sun maka yawa  can dinma saifa aiki yakaini uhum tace ai shikenan. Tinda yanzu na dauko qanwarka ai dole in ganka Allah hajiya ba haka bane Nadiru kenan ta fada gami dayin shiru.

Daman magana nazo muyi to inajinka kan mene kan karatun ummulkairi ne ok inajinka.

Kinga tayi nisa yanzu ace saita sake jamb ta jira admission kamar abin beba shi ne naga tunda anyi sa'a ta dawo ba'ayi exam ba mai zaisa ta koma ko co tasamu ta gyara nan gaba.

Haka ne kayi magana zanma mijin nata magana yawwa yace wasuma sunyi test anman na roqesu zataje su mata inyaso inta koma sai taje din abinda bata ganeba sai shi Abbakar din ta koya mata bama sai ya koya mata ba in qawayenta sun kasa in yaso saita kiraka to yace gami da miqewa ya dire handouts din da ya shigo dasu gashi sai abata wadanda ta siya kan hutune sai wasu kuma wanda malamansu suka bada ne na sayo mata godiya hajita tai yai waje ransa fal farin ciki danshi daman burinsa ummu tasamu inda ake santa.

Sai yanma su Aisha suka tafi tunda ansan da zuwansu daga gidajensu.

Koda ummu taji batin komawarta makaranta tai ta murna tanama Yayanta addu'a nasir koma ince uba dan ita aranta jinsa take yafi qarfin matsayin yaya gareta saidai uwa da uba.

Washe gari sai gasu Hafsa ita da Ahmad Ahmad ummu tai murna sosai suka sha firarsu anan su ummu suka tafi suka barshi dan zai koya mata wasu abubuwan da bata ganeba cikin wanda taga yah nasir ya rubuta mata zatai test.

Ummi (me aikin ummu) dan tun dawowarsu Abbakar ya maida ita sch duda kafin su gudu ma Nasir yasata dan basu barta a niger ba shigowa tayi sanye da kayan islamiyya ta qaraso inda suke karatun tana washe fuska da yake tasan Ahmad sosai lokacin suna zuwa buk namata namatansu ummu kenan kullun yana cikinsu baifi sa'ansu ba ko su ya girme musu da kadam shine kuma captain dinsu.

Mutuncinsu da ummu ya fara tun wata rana baya zama a baya suma su ummu haka saidai suk qawayenta sun gudu gida kan bazasu ji GSP ba tace ita kota koma gida ba kowa zamanta zatai.

Ta shigo theatre din inda ta aje jakarta sai dai ya sauke yai dare dare kan kujerar aikuwa cikin fada ta qarasa sai dai ganin captain ne yasa tadan sassauta captain pls tashi kaban gurina yai banza da ita ga malami a ajin ko tsoronsa bataji ba ta kuma magana katashi nace yace bazan tashi va wani yace ki fuce eyye yana murguda baki dan ya iya abubuwan mata da yawa.

Malamin yace dakai da ita duk kuyi waje ta jiyo anman malan yimum shiru nace kuyi waje ya miqe pls sir harsun kai waje malamin yace ku dawo ga kujera can abaya guda biyu kuje ku zauna ya nuna baya.

Ummu tai can gefe yace madan guri guda nakesan kuzauna ta dawo tana turo baki Ahmad na hararta sai dai kamin atashi har fada ya koma fira dan Ahmad surutunsa yai yawa ko sati ba'aiba duk insa ya gansu sai yaje yana tsokanarta wai ta fiye fada har suka saba sosai ya zama amininta bama aboki ba tun qawayenta na tsokanarta mai aboki namiji kodai kodai har suma din ya zama abokinsu dan shi din mai saurin sabo ne kasantuwarsa duk yan uwansa mata yasa baijin komi dan yana cikinsu.

Ummi ta dan durkusa ta gaidashi ya amsa yana murmushi maman Abbakar andawo tai dariya eh to sannu da zuwa ina tsarabar guduwa ta rufe fuska abinka da yarinta batafi goma sha biyu ba zan kawo maka ai na dauka bazaka zoba yai dariya to gashi na baki mamaki tai ciki tana dariya.

Sun ci gaba da karatunsu ummi ta dawo riqe da kaya irin na yan niger gashi tace ya amsa yana dariya duk wannan eh tace to na gode tai ciki abinta.

Ya kalli ummu Allah diyar nan taki tayi kinga da ace na isa aure ai bada nan ba ummu tasa dariya kaifa shaqiyancinka baya kadan.

Allah da gaske nake to banda abinka kana shekara sha takwas wazaima aure yadan hade rai ashirin dai au haka ne kaka tsoho kawai ki dinga ragen shekaru da girmana da mutuncina sukai dariya baki daya kinga fa dagaske nake ya za'ayi ina ciki fa to kabari ka qara hankali in naga zanbaka sai inba eyye wato yanzu bani da hankali suka saka dariya baki daya.

Hakan yai dedai da shigowar Abbakar a mota aikuwa idanunsa kan ummu dake faman sheqa dariya wani malolon takaici yazo masa wuya gami da kishi afusace ya bude motar yai gunsu shi kansa baisan me zai yimusu ba in yaje anman yasan tabvas bazasuji da dadi ba....
[1/13, 4:20 PM] 🅰️ " AXEEX✌🏼 D'🅱️🅾️Y😎: _POST BY GROUP OF HYPE HAUSA NOVELS BOOK WHATSAPP 08064400100_ 📚📚
[1/13, 4:21 PM] 🅰️ " AXEEX✌🏼 D'🅱️🅾️Y😎: *ABBAKAR*

*150---160*

Ransa duk a bace yayo gurrin baiyi shi kansa baisan yana da kishi irin haka ba sai yanxu ganin ummu da wani da daga nesa bai gano ko wane ba.

Sai da yazo dan kunya ta kamashi ganin Ahmad dan yasanshi abokin su ummun ne qoqari yai ya qaqaro murmushi kamin ya qarasa din, Ahmad na ganinsa yai saurin sauko daka kan kujera yana fadin lah sir sannu da zuwa Abbakar yadan saki murmushi kamim yace ah Ahmad yau kaine a gidan namu yai dariya eh tun daxu muka zo dasu Hafsat su sun tafi nima nakusa muna dan yin abunda zatai test ne ok yayi kyau yace.

Ya maida kallonsa ga ummu yace shine baki fadan zaki fito farfajiya ba ko tai masa banza ince dai baki tafi yawo ba da sunan raka qawaye hawa mota ta juyar da kai tana fadin to sabida me zan fada maka qasa qasa take maganar eyyi me kika ce tace cewa nayi ai naga na fadawa hajiya ok ya miki kyau ya koma gurin motarsa.

Ahmad ya dubeta ashe daman kinsanshi baki taba fadanba tai dariya bansanshi ba kawai dai ashe shine frnd dina da nake fadama na facebook kai dan Allah kice chat ya hadaku tai q wayasan masa baifa taba ganina va time in muna chat kai da gasqke ka mance su haka nefa.

Bama kasan wani abu ba ya kalleta yana fadin mefa wai nan mijina ne wai mijina ne ya tafa hannu gami da riqe haba kai dan Allah tai dariya Allah ya shiryeka ka dinga abu sai kace mace.

Nan ta bsshi labarin komi har aurensu tunda daman tuni yasan tarihinta ya kuma tafa hannu ai mukam kice A abagas zamu sameta a course dinsa tai dariya ai seku dena karatu shima yai dariya.

Ko da Abbakar ya shiga ciki Hajiya ta masa maganar batun Nasir yace ina sam shi yadda ba tunda ummu matarsa ce ba wani karatu da zata ci gaba wanda tayima ya wadatar.

Aikuwa hajiya binsa kawai tai da ido ganin ta miqe zai tafi dakinsa ne tace Habu zonan ya dawo ya zauna .

To bari kaji wallahi kayi kadan ka hana yarinyar nan karatu dan zalunci inma kana ganin kudine bazaka iya biya mata ba ni zan dauki nauyinta balle kuma tanada yaya wanda zai dauka yai shiru.

Maganar aurenka in dan kana aurenta ne kake ganin bazaka barta tayi karatu ba to hanya mafi sauqi ka sawwaqe mata Inada wanda zan bata yai saurin kallinta a'a hajiya bama sai ankai ga haka ba tai tsaki gami da yin dakinta.

Acan kuwa gidansu maganar aurensa tai nisa dan tuni hajiyarsa ta gama magana da aminiyarta zasu hada auren zumunci tsakaninsu badan komi yasa aminiyar amincewa ba sai dan sanin halin diyarta.

Duda cewar tasan halin mahfux sai dai tasan da cewar yafi yarta nutsuwa nesa ba kusa ba.

Dan yarinyar tata takai matuka wajen rashin mutunci dan in iskancin ta da rashin mutuncinta ya motsa har gida take kawo qato inko ta bar gidansu sai anganta.

Bakomi yasa salma yadda da aurenba sai dan daman tun da tana san mahfuz dan yana cikin mazan da take so shi yasa koda mum din ta tazo mata da tanaso tai aure ta fara fada jin wazata aura yasa ta hau murna ta rungume mum dinta gaskiya mum kin gama mun komi da kika neman auransa.

Mum din tata tasa dariya cike da farin ciki yawwa yar gari.

Kinga kafin ai aurannan sai mun gama dashi dan tuni na gama da uwassa so nake kiyi zaman farinciki gidan aurenki dan haka dole musan yadda mukai sai abinda kika ce masa suka tafa kai kace ba uwa da 'ya bane.

Shiko mahfuz ko kadan baya wani farin ciki da auren kawai dai yana dan shassharewa ne dan kar hajiyarsa ta gane.

Shi kadai yasan me yake shiryawa dan ya qudiri aniyar kwato dansa kota yaya ne.

Zaune yake shida lauya dinsa yace wai mansur yaushe zamu fara zaman kotunnan ne wallahi na qagu inga yarona jikina nafiso da ya fara magana ya fara da kirana baba ba wani qaton kawai ba mansur yai dariya yanzu mahfuz aminin nakane qaton kawai yaja tsaki kaga gyara maganarka ba amini na bane.

Ya dafashi da zanbaka shawara kabi da kadaure ka janye qarar nan inaganin in yana gun Abbakar ai kamar yana gunka ne mahfuz ya daga masa hannu kaga malan in bazaka iya kareni

bane ka fadan in canja lauya a'a ni ai shawara na baka ba komi.

To yanxu yaushe zamu fara shiga kotun mansur yace eh yau dai akace za'a kai mata san masu ok ai gwara ayi ayi.

Hajiya na zaune Badaru ya shigo hajiya anada baqo to jeka kace ana zuwa ta dubu Abbakar jeka kaji waye ya miqe yai waje.

Mutumin yace daga kotu nake ina san ganinmatar gidan towo kotu lafiya dai ko lafiya kalau kirata.

Ya dawo yama hajiya bani ta fito yace hajiya kece ummulkairi tace eh nice to gashi ya miqa mata takarda ta mece inkin duba zaki gani.

Abbakar ya amsa ya duba sammaci ne ankai ummu qara kan ta riqema Mahfuz yaro ta baima wani ya dafe kai oh my God ya fada hajiya tace mene ya miqa mata takardar ta karba jiki na bari.

Ganin meke ciki ne yasa ta saka salati yanxu abinda mahfuz zai mana kenan sika koma ciki hankali tashe ganin ummu ta tawo dan basa son tamasan me ake ciki

*Amina-yarzazzau Oumyasmin AeshaKabir  Safiyya kabir da Fatima Ahmad wannan page in naku ne kunfi kowa san wannan littafin ina godiya sosai Abbakar ma na godiya, Ummu tace itama a miqo mata saqon tata godiyar gareki, Mahfuz kam cewa yayi agaisheku da kyau dakyau, Nasir kam tsabar Farin cikin yadda kuke san littafin murmushi ya hanashi yin bayanin saqonsa*

Ciki sukai kowa da tunanin abinyi Hajiya ce tace Habu miqon wayata yai saurin miqa mata sunan Babbar yaya ta hau kira bugu biyu aka dauka.

Tsohuwa barka da rana aka fada daga daya bangaren tai dariya wadda inkana kusa da ita kana kallonta kasan yaqe take dan ranta duk a cakule yake.

Dan rikishi miqama uwarka wayar Sudai yasaki qara kai Hajiya zagina fa kikai itama tai dariya ai nima kasan ba tsohuwa bace ko, Sudais kenan jikan Hajiya na biyu, maza ni kai mata inasan magana da ita jitai ance Hajiya na karba ok sai da ta gaida Umman tasu kamin ta ce umma kiyi Hakuri nayi nayi subar daukan wayata in ankirani anman indai sukaga kece sai sun dauka.

Hajiya bata bata amsa ba tace in Abbansu ya dawo inasan ganinku baki daya to umma fatan lafiya, lafiya qalau kamar yaushe kenan kike san muzo yau ko gobe da sassafe to insha Allah zamu zo mu duka kike san gani ko mu biyu a'a banda yara tam se munzo sukai sallama.

Hankalin Babbar yaya duk ya tashi dan Hajiya bata musu neman gaggawa haka kawai, Hakan

yasanya ta kammala komi da wuri mijinta kawai take jira.

Koda ya dawo abinci kawai yaci dan ita bama taci ba saida ta tabbatar ya qoshi yana shirin zama kallo kamar ko yaushe tazo ta masa bayanin kiran hajiya yako hau fada kinsan da kiran tun dazu da na dawo baki fadanma yanxuma nasan ta gaji da jiranmu ita dai tai shiru kawai.

Maza dauko gyalenki muje ta miqe tana qwalaw Nurat babbar yarsu kira ta fito da gudu mum gani daukon gyalena a daki ta kawo mata tana sanyawa tana mata bayani.

Nurat ki kula da qannenki bankuma san duka kinji ko zamu fita bazamu dade ba gidan hajiya zamu in 10 tayi kuje ku kwanta to mum Dady yace zansa tijjani in 11 tayi ya kashe gen to kai sudais kazo muna futa ka rufe qofar shigowa nan shima to yace.

Sai kun Dawo Nurat tace gami da komawa kujera tai kwanciyarta tana ci gaba da karatun littafin da take na Aisha Kabir a wattpad mai suna Step mother ( Aziza's Story) danma writer din tana bata haushi bata cika update da wuri ba anman duk sanda tayi sai tasa ta mance da haushin da takeji dan zata kawo chapter mai dadi data fi ta da.

Yaya babba ce zaune ita da mijinta gaban hajiya suna kwasar gaisuwa ganinta lafiya qalau gasu maryam duk zaune suna fira yasa yaya Babba samun kwanciyar hankali.

Bayan sun gaisa ne Hajiya ta kuma kai dubanta ga ummu tace wannan itace Bilkisu babbar yayar su Habu wannan mijinta ne ummu ta kuma durkusawa ta kwashi gaisuwa duda dazun ta gaidasu, Hajiya ce ta baima su maryam harda ummu umarnin su koma daki zata gana da diyarta.

Maryam ce takaima Abbakar qarami sura zata daukeshi yana kan Cinyar hajiya yako sa kuka shi bazai bitaba Hajiya tace qyaleshi maryan ta watsa masa harara gobe kace zaka bini ko kallonka bazanba sukai mata dariya baki daya.

Idon hajiya nakansu ummu sai da tada sun haye sama ta dawo da idonta kan su bilkisu nan ta musu bayanin komi gami da basu takardar sanmacin.

Mubarak kai nakesan ka zama lauya dinmu inso samune banasan ko kadan yarinyar nan taje kotu tam shikenan hajiya anman inaga kamar zuwanta zai iya zama dole anman dai bari muga kamun ludayin shari'ar.

Yaya babba tace anman dai mahfuz bai kyauta ba zan je in sameshi gobe ko zai janye shari'ar Abbakar da tun dazu yake sauraronsu baice komi ba sai yanxu ai yaya dama kin gyaleshi wallahi ta watsa masa harara kai ba abin kunya bane wasu sujiku a kotu dashi to aishina ya rufe idanunsa ya mance da alaqarmu, daquwa ta watsa masa ungo nan inshi san zuciya ya rufe masa ido sai kaima ya rufema.

Gobe zanje insha Allah ai kowa nasan sulhu yawwa kije in inji Hajiya dan wallahi inajin tausayin yarinyar tana cikin matsaloli da yawa tayi qanqanta dudu batafi sekara sha tara ba yan biyu inzan iya tunawa sun girme mata.

Washe gari da wuri Yaya babba tazo gida anan ta aje motarta tai gidansu mahfuz tai sa'a alokacin zai fita yana ganinta ya washe fuska kai kace ba abinda ya shiga tsakaninsu da qaninta itama ta saki fuska suka gaisa bayan futowarsa daga mota.

Tace Allah ya temaken ban daki gurbi ba gurinka nazo towo to mushiga ciki a'a namma ya isa zatonta ko hajiyarsa tasa shi kai qarar dan bataso ta hanashi janyewa basshi namma ta isa taja ta zauna a teburin me gadin su.

Yanzu mahfuz abinda kai ka kyauta kenan ya kalleta da mamaki kamar ba abinda yai yace ni kuma me nayi ta kalleshi sosai kamin tace yanzu bakasan me kayi ba eh wallahi yayi kyau tace.

To Bari in fada maka daka kai amininka kotu mana ya dafe qirji ni kuma me yamin zan kaishi kotu ta kalleshi da mamakin yadda yake maganar kamar besan yayi ba.

Ka mance kace ya riqe maka yaro oh ya fada haka yace miki shi nakai ni wallahi bashi nakai ba ai komai yamun ya wuce in kaishi qara tai dan murmushi ai kamar shi kakai tunda ka kai matarsa yai shiru kamin yace ni wallahi bashi nakaiba ko sunansa babu cikin qarata.

Ok naji bashi kakaiba kayi haquri ka janye qarar in yaso inkayi aure sai yaron ya dinga zuwan maka hutu kaga yanxu ko yayeshi batai ba.

Ina wallahi baxan janyeba ace nida yarona sai dai yadinga zuwa min hutu to ni so nake in amshi yarona tun kan ayayeshi inasan jinsa kusa dani ajikina akullin inasan ya taso da qaunata.

Yaya Babba ta gyada kai ai shikenan se aje kotun inga me baka yaron yanajin nauyinta hakan yasa cikin qunquni yace ai kota yaya ne sai na amshi abina.

Bataji mai yace ba tai gaba kawai.....

Waye Abbakar

Alhaji ukashat Fadal shine sunan mahaifin Abbakar haifaffen garin kano ne unguwar yakasai komi nasa yayi shi ne agarin kano wato girma karatu duk a kano yayi su.

Yayi karatun likitancinsa inda ya fara aiki anan Muhammad Abbdullahi wase hospital, Fiddausi daliba ce cikin daliban sch of nursing kano practical ya kaisu asibitin sannu a hankali shaquwa ta shiga tsakaninsu da da Dr Ukashat har ta kai su ga aure.

Shekararsu guda da aure ta sami ciki ita din mutunce me laulayin tsiya hakan yasa da kanta ta

ajiye aikin da take dan tuni ta kammala school of nursing in.

Sai dai tun haihuwar diyarsu ta fari basu qara haihuwa ba san duniya suka dorawa Bilkisu tun basa damuwa har suka fara damuwa.

Bilkisu na primary 1 suka kuma haihuwar namji yaci sunansa Abbakar yayarsa ke kiransa da Habu sai dai yaro nada shekara uku bilkisu na primary 4 yaro ya koma tai ta kuka cikin ikon Allah fiddausi ta kuma samun ciki lokacin da ta haihune Aka maida masa da sunan marigayi Abbakar.

Abbakar nada shekara biyu fiddausi ta kuma haihuwar mace ta ci sunanta zainab.

Abbakar nada shekara hudu zainab biyu bilkisu sha biyu tana Jss one yanzu kam arziqi sosai ya zaunawa Ukashat dan asibitinsa ya bunqasa sosai gami da shahara a ko ina a nigeria dan tuni yai asibitinsa mai zaman kansa inda kwararrun likitoci ke aiki cikinsa, makarantar koyon jinya ma tuni ya kammala gininta kawai jira yake amasa register ta fara aiki.

Su Abbakar basa futa sai dai in Bilkisu zata makaranta ta tafi dashi ajinsu daya da Muktar yayan mahfuz shima yakanzo da Mahfuz Nasir na aji daya sai dai su mahfuz basa zama a ajin yara sai gurin yayyensu zamansu aji daya su kadai ne sa'anni yasanya shaquwa ta sosai tsakanin Mahfux da Abbakar.

Hartakai in ba islamiyya mahfuz zaita kuka sai ankawoshi gidansu Abvakar danshi Abbakar bayasan zuwa gidansu mahfuz danshi mahfuz irin yarannanne inyaga agidansu ne yaita dukan yaro inko agidansu Abbakar ne sai dai suyi ta wasa.

Lokacin da suka isa shiga sch baban mahfuz yakaisu makaranta tare aji daya Mahaifin Abbakar yaso cire Abvakar Fiddausi tace ya kyaleshi kar baban mahfux yaji ba dadi.

Abbakar da mahfuz abokaine sosai sai dai hakinsu ya vanbanta dan shi mahfuz ya cika rawar kai duk yan iskan aji da sch insu abokansa ne.

Suna jss 3 aka haifi maryam su Abbakar murna kamar me.

Tuni makarantar mahaifinsu ta fara aiki kudi sun qara zauna musu sai dai ko kadan Abbakar ba irin yarannan bane masu nuna su wasu ne.

Da suka shiga SS ne ya zabi science mahfuz art yakeso sai dak bayasan rabuwa da Abbakar hakan yasa ya haqura da art din ya shiga science.

Bilkisu babanta ta gada dan medicine take tana lecel 4 aka mata aure .

Zainab na Jss 3 Abbakar Ss3 yayin da maryam primary 1 Hajiya nada wani tsohon cikin Alhaji

ukashat yai hadari kan hanyarsa ta dawo wa gida daga kaduna sai gawarsa aka kawo gida kuka gurinsu kamarme.

Kwana uku da rasuwar Hajiya Fiddausi ta haifi yaranta guda biyu macen ta fara haifa da kwana biyu wank ciwon ya taso dan agida ta haihu ko asibiti basu je ba ta kuma haihuwat namiji.

Abbakar ko kadan bayasan yayi medicine math yake so ko engineering hakan yasa da suka fara medicine aka tafi yajin aiki yasa kawonsa ya masa komi na tafiya japan karatu yai sa'a dagyar Hajiyarsu ta yadda.

Lokacin da ya samu mahfux da batu ya yadda shima zashi sai dai daya fadawa wani abokin shaye shayensa yace kar yaje haba Baba kaima kazama mutumin kanka mana ace kullin sai abinda guy dincan yace zakayi yaita zigashi har ya yadda....shi kuwa salim badan komi yake zugar ba dan sanin in Mahfuz ya tafi babu mai siya masa kota yar lasa ce wato kwaya.

Samun Abbakar yai ya fafada masa Hajiyarsa taqi yadda Abbakar yace zai sameta yace kar yaje nima inasan koda sau daya ne inma mahaifiyata biyayya Abbakar yaji dadi dan zatonsa shiriya tasamu abokin nasa.

Duda Abbakar basa tare da mahfuz anman komi yai sai ya fada masa lokacin Abbakar ya kirashi tayashi murnar kammala masters insa ne Yakr fada masa abinda yai ma ummu batare dajin komi ba zatonsa Abbakar ma bazaiji komi ba kamar su salim da sukai ta sara masa.

Saidai Abbakar fada yai ta masa har saida mahfuz yai danasanin fada masa.

Yaya Babba da zainab ke kula da Dukiyar mahaifinsu asibiti da makaranta sai dai lokacin da zainab ta samu miji tai aure a katsina abubuwa suka dawo kan yaya babba duka hakan yasa Hajiya tilastawa Muktar auta yin karatun likita tunda shi namiji ne tashi Abbakar yaqi.

Koda ya kammala secondary ya tafi india yin medicine ummi tagwai insa take law maryam pharmacy.

Ci gaban labari

Ranar da aka saka za'a zauna a kotu yazo ta kuwa cika ba lefi duda bakowa yasan da qarar ba.

Lauyoyi sun bayyana kansu inda maga takarda ya karanto bayanin qara kamin shari'a ta fara gudana.

Bayan bugawa da lauyoyi sukai tsakaninsu aka daga qara zuwa sati biyu ba tare da tabbacin wazai nasara ba cikinsu dan ko wanne kwararrene.

Yaya Babba ce tazo gida tana fadawa Hajiya abinda mijinta yace dole sai sun kai ummu kotu da

ita da Nasir dan sune shaidun fyade ya mata dagyar hajiya ta aminta.

Bikin mahfux kam yai nisa dan gobe ake saka ran daurin aure yayin da shi tuni ya mance dan hankalinsa gabaki daya ya tashi ganin kamar bazasuyi nasara ba.

Yau akai za'ai zaman kotu dagyar Nasir ya yadda zaije sai da ummu da hajiya Hajiya da yaya babba sukai ta roqonsa ya yadda yaje.

Bayan saurarun shedu da DNA da akai aka tabbatar yaro na Mahfuz ne alqaliya tai gyaran murya kotu tai tsit kowa nasan jin me zata zartar.

Tace ina mahfux ya miqe ina yaron da ake qarar kansa shima ummu ta miqe gashi ranki ya dade ina uwattasa tace nice.

Miqa masa shi ummu ta kalli alqaliyar alamar in miqa masa kamar yaya tace nace ki miqa masa shi ko ummu ta qara qanqame yaronta police mace ce ta amshi yaron ta miqawa mahfuz dake faman washe baki ummu ta zube gurin tana kuka.......
[1/13, 4:21 PM] 🅰️ " AXEEX✌🏼 D'🅱️🅾️Y😎: _POST BY GROUP OF HYPE HAUSA NOVELS BOOK WHATSAPP 08064400100_ 📚📚
[1/13, 4:22 PM] 🅰️ " AXEEX✌🏼 D'🅱️🅾️Y😎: *ABBAKAR*

*PAGE 160---170*

Mahfuz yakai hannu ya amshi yaron tuni kotu ta hargitse da hayani kowa na fadin albarkacin bakinsa domin yau kotun ta cika sosai da yawa cikin mutanen kotun abu daya suke fade yake kuma basu mamaki wato wannan wace irin alqaliya ce wannan zalunci ne.

Maganar da alqaliyar ta fara ne yasanya kotun fara yin shuru kafin daga bisani kuma tai shiru.

Yanzu daman innace ka amshi yaron nan saika amsa ya kalli alqaliyar da mamaki, ina kai musulmi ne ko baka da labarin in mace ta haifi yaro a muslunci batare da aure ba yaron nata ne bana wanda yai cikinba.

Kai wane irin azzalumi ne da har zaka ma yarinya fyade ta haihu kakuma zo ka kawota qara ko dan ita batasan haqqinta ba ta gaza kawoka qara.

Wato kazo nan aqwace yaro abaka ko kai gaka uwa da uba na doka ko to abaka shi kamasa me ka kasheshi ko yai saurin kallonta da mamaki fiye da dazu eh mana kanasan karbar sa ka kasheshi dan karya girma ya zargeka da rashin kawoshi ta hanya dedai.

Mahfux cikin fishi yake magana Haba malama wannan ai bayi bane zaki dunga mun sharri kawai dan kina alqaliya tsawa ta daka masa kai malan kasan a inda kake kotu ba sa'ar wasan ka bace.

Sakamakon samun wanda yake qara da rashin ta ido da kotu saka makon haka kotu ta bada dama a sakaya shi nanda wata guda sannan yaro na mahaifiyarsa ne kotu ta masa katanga da yaron indai ba mahaifiyarsa ta yarje yaje gunsa ba.

Duk yadda yan uwan mahfuz sukaso kar yai firxin na wata guda abin yaci tura dan alqaliyar iya wuya yazo tace da a qyaleshi gwara ta bar aiki.

Har gida alqaliyar mai suna Salma tazo ta sami ummu tasamu karba ta mutunci sun gaisa da hajiya kamin ta fara bayaninta.

Indai kun amince ni zan tsawa ummulkairi ta kai yaroncan qara kan cin zarafinta da yai na keta mata haddi tunda duk wata shedu munadasu na zaman kotun da mukai.

Kafin hajiya tace wani abu ummu ta dora a'a ni zaman yarona agurina wallahi ya fiyemun komi na riga nakai shi qara gurin sarkin da baya zalinci nakuma san ko aduniya ko alahira zai saka min nagode sosai aunty sukai sallama ta tafi.

Hankalin hajiyar mahfuz yafi na kowa tashi gashi gobe daurin aurensa abin haushi dik gidajen radio da tv sun nuna shi sakamakon rashin mutuncin da yai akotu balle tace ko tafiya yai.

Ban garen gidansu amarya basu wani ji komi ba dansu burinsu kawai su aurar da salma gama ko wane ko sa samu su huta da halinta, itama bangaren Amarya bataji komi ba saima murna da tayi na rashin bashi shegen dansa dan mum dinta ta fada mata irin son da yake masa shi yasa tun kan tashiga gidan kishin duniya ta dora kan yaron, na biyu kuwa ta samu abinyi in ya mata gori zata rama da cewar ai gwara ita bata taba bursinba.

Mahfuz duniya ta masa zafi ba abinda yake tunawa sai sa'adda police suka saka masa ankwa Abbakar yasa hannu ya amshe takwaransa dake hanunsa ya miqawa ummu.

Gabaki daya yai baqi ya rame danshi mutunne da bai saba da wahala ba bakuma yasanta ji yake wata guda dinma taqi qarewa  ji yake kamar shekara ce zaiyi ba wata ba.

Sanye taje cikin baqar abayarta mai adon ja ta nada mayafin abayar akanta sai yar jaka mai dauke da littafanta gudu uku kacal ita ma jace sai dan duwatsun baqi jikinsu takalminta mai sauqin nauyi tai kyau sosai.

Ummu kenan wadda ko wacce kwalliya tai tana mata kyau musanman a idan Abbakar wanda yanzunma tunda take saukowa ita da ummi qanwarsa yake binta da kallo gashidai shiga iri daya sukai anman gani yake ina ummu ai babu ya ita.

Ummu doguwa ce bacan ba komi nata me kyau ne ita din bata cikin fararen fata bakuma za'a kirata baqa can ba tanada dai duhu irin na yan Nigeria wato duhunta me kyaune fatarta ma me kyauce idanunta yan madai daita wanda hancinta da baqinta sun dace da yanayin fuskarta kana kallonta zaka san ta hada jinsi da larabawa ko ka kirata irin fulanin asalin nan kamarta daya sa babarta saidai ita batayo hasken babar tata ba.

Sai da suka zo dab ummi ta tabashi yah munata gaisheka bakaji ba ya dake irin karsu gane ita yake kallo yayin da tuni hajiya ta rafkoshi yace oh banji ba inadanjin bacci ne, ina zuwa haka zamu sch ne ok to ku jira in kaiku ya fada gami da miqewa.

Ajikin motar suka tsaya yazo ya bude duk suka shige baya shima yai zamansa agaban motar yaci gaba da daddana wayarsa yayinda lokaci lokaci yake satar kallon ummu.

Ganin bazai tafi bane yasa ummi qanwarsa cewa yaya muje ko ya juyo ya watsa musu harara baki dayansu muje ina? sch mana kai kace zaka kaimu ai, nace dai zan rage muku hanya ko suka kalli juna ita da ummu shi kuma ya ci gaba da danna wayarsa.

Ganin da gaske bazai tafiba yasa ummu daurewa tace pls sir karmu makara asanyaye tai maganar yadan kalleta watoma agidanma kallom wancan lecturer din nasu na thermodynamic take masa yace au ai nazaci baku shirya tafiya ba ummu aranta tace lallai mutumin nan dan rainin hankali ne bamu shirya tafiya inba zamu shiga mota ummi ta miqe daga bayan ta koma gaba.

Ko rufe qofar taiba ya tada mota ta jawota suka tafi, ummi ya fara saukewa a old campus dan zatai wani abu yaja yai tsawarsa ganin yana bata mata lokaci yasa tace pls dan Allah sir mu tafi.

Ya leqo gidan bayan ni direbanki ne ya fada yadda yai yamata kwarjini hakan yasa ta fito ta shiga gidan gaba yaja suka tafi.

Adai dai faculty insu ya paker ta bude kamin ta sauka ta juyo tace thank you sir ya ruqo hannunta da sauri ya juyo ta kalleshi ba sunana Sir ba, nakuma sanda kinsan da hakan dan haka akiyaye ya saketa tai waje dasauri.

Su Aisha ta gani can gefe suna sheqa dariya harda tafi iyye kaga masoya wato abin har yakaiga adinga kawoki inkuma ankawoki a zauna a mota a kwashi love ta turo baki to 'yan sa ido masu zuwa lahira da qoqom danbu anayi kuna irgawa to ya ranku.

Ahmad yace ransu fes birgesu kikai shi tasa suka kasa shiru Hafsat takai masa duka da littafinta kaifa dan is ne ah kinga yarinya dena iskantani da mutunci na har yanzu suka saka dariya baki daya.

Yau kwanan mahfuz uku kenan da fitowa duk yai baqi abinci ma ba wani da dinsa yakeji ba

kawai dai yana daurewa ya cine dan kan abin ya masa yawa ga yunwa ga rashin dansa.

Ganin ya kwan uku ne bai maganar matarsa ba hajiyarsa ta sameshi adakinsa yana kwance da alamu tinani yake tace mahfuz magana nazo muyi ta Fahinta ya dago gami da jin gina da gadon to hajiya inajinki.

Maganar matarka ce Naga tunda ka dawo bakamin maganarta ba adan razane ya kalleta mata kuma hajiya eh matarka danshi a zahirin gaskiya yama mance dawai za'a daura masa aure balle yasan an daura.

Haba hajiya da wanne zanji da auramin wadda banaso ko kuwa da kwacen yarona da akai ta daga masa hannu kaga ni yimun shiru kai inbanda butulci naka yarinyar duda sanin kana da yaro shege ta yadda ta aureka kace aura maka ita tashin adalcine kai inbanda amincin dake tsakanina da uwatta aikasan kamin kasamu me aurenka saika shirya.

Dan haka ina baka umarni kayi maza ka hada naka yanaka ka koma gidanka na court road dan can nasa aka kaima ita idanunsa sunyi jawur rannan abace ya miqe ya hau dibar kayansa.

Ko sallama baima Hajiya ba ya fice daga gidan danshi yanzi haushinta yakeji gani yake ita ta cuceshi data sangarta shi ta nuna masa komi yayi dedai ne gashinan tasa yaje yai abinda sakayyarsa ke neman haukatashi.

Gidansu Abbakar

Yau shirye shirye suke sosai dan har su Nurat sunzo aunty zainab ce zatazo dan ganin amaryar yayan nata dan ita batasanta ba.

Lokacin da tazone aunty zee tasha mamaki qanwarmu ashe kece amaryar tamu ummu ma ta mamaki aunty zee daman ke yar nance eh aure yakaini katsina kowa yai mamakin sanin juna da sukai.

Aunty zee ta dubu Hajiya umma ai nasanta qanwar Yah Nasir ce kuma qawar Farida qanwar salma wato qannen mijinta Hajiya tace ikon Allah.

Da yake duk gida daya suka zauna da su salman yanzu ma tare suke ra Farida ummu tai dariya kawai Abbakar yace a'a yanzu ta dawo nan daiko suka saka masa dariya baki daya.

Zainab ta dubi ummu waiko in tambayeki ummu ta zuba mata ido alamar inajinki, Yah nasir kuwa ya fadawa Farida yana santa ummu tadan dubeta wato itama tasan yanasan Faridan a'a tace.

Kai yaya Nasir da zurfin ciki yake wallahi tun yarinyar nan fa na Jss yake fama da santa yasha fadan yadda yakejin santa aransa anman ya kasa fada ai shikenan nasan me zan masa.

Suna gama cin abinci ta kira Nasir din awaya Yaya na nafazo garin naku eyye watoma garinmu ko to ganinan zuwa gidan naku.

Sun sha fira kamin zainab tace daman jaje zanma bikin Farida ya gabato sauran wata uku what ya fada yana miqe ina wallahi bazai yiwuba farida tawa ce ni daya.

Yai waje zainab ta bishi a baya sedai kamin tazo ya fice a motarsa ita dai hankalinta duk atashe kar yaje yai wata baran baramar.

Kai tsaye gidan Farida ya wuce ya dade baije ba dan yanzu ita kadaice hakan yasa gudun shedan ya rage zuwa duda ta ce masa qannenta uku sunzo mata hutu baida niyar zuwa.

Kullin cikin kiransa take awaya ko a sch nunawa yake baisanta ba yama hanata zuwa office dinsa gabaki daya.

Kai tsaye gidan ya shige yana kwala mata kira Basira na shanya tasanshi hakan yasa bata tsorata ba se ce masa datai tana ciki.

Da gudu Farida ta fito yah lafiya kuwa cikin kwalla yake magana yanxu Farida kin kyauta min kenan kinsan da ke daya nakeso a duniya shine zakiyi aure ki barni ta kalleshi yah ban gane me kake magana akaiba yaushe muka taba maganar soyayya dakai.

Ko kuwa nace inasanka ne what eh bakice kinasona ba anman aikin nuna ta zaro ido ni wallahi a'a kawai irin kulawa da wa da qanwarsa ce .

Oho ke kika sani ni kawai abinda nasani ke din matata ce kuma dole koma wazaki aura a fasa ayi dani cikin dan murya me qarfi take magana wai yaya wane aure kake magana yaushe nace ma zanyi aure.

Wayarsa da tun dazu ke ringing ya daga bema duba ko waye ba ya amsa muryar zainab ce cikin muryar kuka take fadin yah wallahi da wasa nake tsokanar ka kawai fa nake ba wani aurenta da aka saka.

Kunya duk ta kamashi sun sun ya fice yabar gidan Farida na kiransa yai gaba ita dai tasan yaya nasir baya shaye shaye dasai tace ko ita ta fada masa qarya.

Gidansu zainab ya koma anman kin gama dani kinsa nayi abinda banniya ba tasa dariya to ai kaga na temakeka kaidinne inata ka tsaya katsaya kai gaba ummu tai dariya ke kuwa aunty zee yaji zuciyarsa zata tafi gidan wani yace eyye kema harda ke ko suka saka dariya Abbakar mamaki yake daman tana magana da dariya haka.

Gidan Mahfuz

Duk ransa abace ya shiga gidan sai dai me yana shiga yaji yamanta komi ba abinda yake sai burin ganin matarsa ko rufe murfin motar baiba yai ciki ita kuwa gwanar daman su suka tunzuro Hajiyarsa ta koroshi dan tuni ko wanne aiki da bokansu ya basu sun kammala.

A tsaye ya hangeta da wata arniyar shigarta suna hada ido wanda yaci kwallin boka yaji ya kasa koda motswa zuwa tai taja hannunsa sukai ciki gurin dinning area ta kaishi ta zuba masa lemon abarba da yasha magani ta miqa masa ya amsa ya hausha saida ya shanye ta zuba masa abinci yaci yai nak.

Komi ya tafi yadda suke so dan basu wani sha wuyaba asirunsu ya kama mahfuz dan shi din ba gwanin ibada bane .

Mahfuz ya zama kamar wani sauna sai abinda matarsa ta fada masa yake ta zama kamar itace mijin shi kuwa irin baiwar matarnan danma bazamu kirashi matarso ba.

Rabonsa da gidansu tun randa ya baro sati biyu kenan ko wayoyinsa matarsa ta kashe cewarta ita bata gama cin amarcinta da angonta ba aiki ma dan dole take bari ya fita shima sai yasha kashedin in ya dade ko ya kula wata shi da ita ne gabaki daya tsoronta ya gama rufe zuciyarsa.

Gidansu Abbakar

Zainab ce tsaye suna magana da Hajiyarsu umma wai yaushe ne Amaryar zata tare nama yaya magana yamin shiru Hajiya tace se randa ya shirya inkuma be wasa ba wallahi sawa zan yasakar min ita tunda naga baya santa inyaso na bata sulaiman kai hajiya kema kinsan yah nasanta sulaiman da tunda ya taso yake qasar waje ai bazai yadda da auren dole ba au haka kika ce zakusha mamaki tai dariya kawai sikai sallama suka tafi.

Soyayya tsakanin Farida da Nasir kamar sa hadiye junansu ko yaushe suna maqale awaya ko yana gidansu Abbakar dan tuni Farida ta dawo gidan da zama.

Magana tai nisa aure saura wata guda duda farida taso sai tana level five yace shikam ya gaji da yaquri tanaji tana kallo ya mata fun qarfi.

Rana bata qarya yau laraba ake kamun Farida su ummu ne manyan biki duda kuwa gogon nata baisan budirin da take ba dan ko ta kanta baya bi qarqari yazo ya dauki takwaransa girin hajiya su fice yawo dan yaron ya saba dashi sosai.

Yau zasu wuce kaduna dan acan za'ai bikin dagyar hajiya ta barsu sun fito da akwatu suna zubawa a bayan mota ya shigo da motarsa idanunsa kansu yai parking ya qaraso.

Ku ina zakune haka kuke jidar kaya cikin sauri ummi tace yah ka mance bikim yah Nasir to

nan nan din sekun dibi kaya kai yah Kaduna fa zamu.

Me kaduna ku ai yan uwan angone ba inda zaku munfa tambayi hajiya ya doka mata harara zaki matsa ko sai nai ciki dake tai cikin gida da gudu tana kuka ummu ta huro baki gami da qamewa wajen.

Eyye sannu mara mutunci wayo ke bazaki bar gurinba ko tai masa banza wallahi ki kiyayeni ta kiyayeka ko kai ka kiyayeni.

Hajiya ta fada suna fitowa da ummi kuma biki ne se sunje haba hajiya dan Allah nifa mijin tane anman kin hanani matata kuma kina nunan iko kanta ai inzata fita ya kamata ta tambayeni.

Haba hajiya ta riqe iyye sannu me mata kai inkana da kunya kace matarka ce ka taba bata kwayar shinkafa eyye.

To anman hajiya ai baki kawota gidana kinga na kasa ba me kace yace bakomi cewa nayi se sun dawo yai ciki hajiya tace dan nema ashe rashin kunyar qarya kake.
[1/13, 4:22 PM] 🅰 " AXEEX✌🏼 D'🅱🅾Y😎: _POST BY GROUP OF HYPE HAUSA NOVELS BOOK WHATSAPP 08064400100_ 📚📚
[1/13, 4:24 PM] 🅰 " AXEEX✌🏼 D'🅱🅾Y😎: *ABBAKAR*

*PAGE 170---180*

Duda ummu taji dadin shigar mata da hajiya tayi can qasan ranta bata ji dadin zatayi tafiya me nisa ba tare da izinin mijinta ba duda shi din bai nuna wata kulawa na shi din mijin ta ne.

Yau take daurin aure cikin wadanda sukazo kaduna har da Abbakar tunda suka iso yake baza idanu ko zaiga ummu amma bai ganta ba ko ya manta da mata basa fitowa gurin daurin aure oho.

Su ummu se hotuna ake sha da angwaye wadanda suka shigo cikin gida bama tasan da zuwan Abbakar ba tai kyau sosai kai kace itama din amarya ce.

Ummi qanwar Abbakar taxo ta riqota madan yaya fa zai tafi baku ko gaisa ba balle kuyi hoto ta dube ta wane yayan, Yah Abbakar au yazo ta fada eh to shida yazo be nememu ba se mu zamu nemeshi, ta dan dafata haba tawan ki daure badanshi ba danni to kije kisa ya shigo se muyi photon pls ummu ki temaka danni kije ki kirashi ummu tai jim kamin tace amman ummi..... Bata qarasa ba ummi tace pls harda dan rissinawa.

Sai da ummi ta rakata har zaure ta tabbatar ta fita farfajiyar gidan sannan ta juya cikin gida.

Ware idanunta ummu ta shiga yi dan su bata ikon hango ko gani Abbakar cikin dan dazon

mazan da ke gurin.

Baba mahmud da wasu yayun babanta ta hanga da sauri cikin murna tayi wajensu ta durqusa har qas ta gaidasu babu wanda ya ganota dan an riga da anmusu asirin farraqu nasu mance da ita da shafinta.

Baba mahmud ne yaso ganota sai dai ya rasa inda yasanta kawai dai yanaji ajikinsa kamar ita din jininsa ce sosai suka gaisa taji dadi dan zatonta sun ganeta Baba mahmud harda zaro kudi ya miqa mata gashi a qara a hidimar biki ta amsa tana godiya duda bataji dadin rashin tambayarta ina take ba ko me yasa tabar gida.

Shiko gogon nata kamar ance ya kalli qofar gidan idanunsa akanta kishi ne ya rufeshi ji yake kamar duk gurin kalle masa ita suke yayin da ya kasa dauke idanunsa akanta.

Jikinta ya bata ana akallonta hakan yasa ta maida idanunta inda take zaton tanan ake kallontan hangensa tai jikin motarsa shida wasu su uku tai saurin qarasawa.

Batasan me yasa ba lokacin da taje daf dashi ta tsinci kanta da yi masa murmushi, shima din ganin murmushinta da in ba daga nesa ba tanaima wasu bazaice ta taba masa ba ji yai kamar su kadaine awajen ya hau mata murmushi duk ya nemi fadan ya rasa.

Yah barka da safiya tace barkanki dai daman naga baka shigo bane shine nazo in kiraka kazo muyi hoto da angwayen.

Hoto kuma eh a'a ni gaskiya ban iya hoto ba balle cikin mata pls yah tarihine tai maganar cikin wani salo dama batasan tayi ba yayin da shi kuma baima sanda yace muje ba, tana gaba yana biye mata baya har suka isa gidan.

Sunyi hotuna sosai wasu shida ita dasu ummi da su Nasir din ji yake dama ranar aurensu ce shida ummunsa da yafi kowa jin dadi har ya juya zai fita ummi ta tawo da gudu riqe da Abbakar qarami yah bakuyi dashi ba tace ya amsheshi ya tsaya za'a daukesu su biyu ummi ta tura ummu kuyi tare tarihine, su uku me hoton ya dauka ita Abbakar da takwaransa sunyi kyau sosai.

Duk yadda akai da Nasir ango ya yafi yaqi yace ina shifa sai an bashi amaryarsa dole dole ya tsayar da Abbakar kan ya bari zuwa qarfe uku sai su tawo in andauko amarya.

Su hudu ne cikin motar Abbakar keja ummu agaba azaune sai ango da amarya, Hirar ummu da Yah nasir da Amarya kawai kakeji yayin da Abbakar tuqinsa kawai yake dan bashi da ta cewa sai in Nasir ya sako shi ciki ne yake dan tofa tasa.

An kawo amarya gidansu Nasir aka fara kaita ummu bata shiga ba a aqofar gida ta tsaya cikin

motar Abbakar yai yai da ita kan tazo su tafi gida taita roqonsa ya bari ta kai amarya shi kansa mamakin kansa yake me yasa komi tace yake amin cewa uhum Abbakar kenan wato bakasan power of love ba kadan ma kenan.

Su Farida se wani kuka take tun shugarsu har fitowarsu se kace ba ita ce dazun suketa kwasar fira a mota ba.

Sun shiga kamar dazu ummu a gaba ita abaya sedai angon be shigo ba shima Abbakar yana daga waje ummu ta leqo ke mu dallah ki mana shiru ai kin fito daga gidan sirikan da kukan naki zai yau dara, Farida ta daqa mayafin gami da dan shan mur.

Ke nice dallah din maza ki nitsu yanzu ni yayarki ce tunda ina auran wanki ummu tace ayi haquri aunty gyanbo sarkin san girma suka saka dariya baki daya, Ummi ta leqo ta taga anti Farida pls ki dena surutu ko yaya Nasir yazo kinga in kina magana ai bazamu samu kudin siyan baki ba kidan daure kiyi shiru awa daya ne kawai munje mun tafi, Farida ta kai mata duka ta jikin taga tasa dariya tai gefe.

A mota ma da Nasir ya shiga kuka ta cigaba da yi abinta shiko yahau rarrshinta haba tawan ki daure kiyi shiru kar nima kisani kuka ko kunyar su ummu baya ji harda wani jawota jikinsa yana lallashe ita kuma taqi magana se shessheqar qarya take tana kuma lafkewa, ummu tai gyaran murya gami da daga waya tana fadin ummi albishirinki anbi umarninki ki shirya karbar masu kauri Farida tace to mugaye ce miki akai.....bata qarasa ba ummu tasa dariya maza ki tonawa kanki asiri itama tasa dariya.

Ankai amarya da yake ba wani qawayen azo agani take da ba su ummu ne sai wata aminiyarta da suke buk tare su ummi sarkin san kudi tun aqofa ake radawa Farida kartayi magana intayi kuwa gidanta bazata dinga zuwa ba, ansamu abinda akeso dan dubu hamsin Abbakar ya lale ya bada dan Nasir din tun safe abokanansa sun tafi sai Abbakar din din da mansur duda duk qannene ga Nasir din.

Duk masu rako amarya na kaduna wato yan uwanta a gidansu Nasir zasu kwana hakan yasa su Abbakar na fita ya dubi ummi yace to lashe money se a yunqura ayi gaba ko tace lah yah kora yace wah ni ban koreku ba kawai dai ta miqe bari to muje kar akoremun da dai yafi inji farida ta kamo kunnenta ta fada mata kai aunty Farida.

Nace su Yah Nasir seda safe su farida uwar rawar kai kuma uhum to ba wani abin zance ba ita ma din seda safe ne asha amarci lafiya.

Zaton ummu yah Abbakar ya tafi sai dai tsaye ta ganshi jikin motarsa ummi tai kamar bata ganshi ba ta shige motar mansur ita da wasu qannensa.

Ummu ma tazo shiga taga ta cika ta dawo gurin Abbakar din bai ce mata komi ba ta bude ta shiga gami da kwantar da Abbakar dinta a baya.

A dedai inda zai kaika ga bangaren da zai kaiga bangaren hajiya ya parker kagaba kadan ummu ta da juya ta dauko Abbakar qarami dake bacci ta riqe qofa zata bude yai locking din motar gabaki daya gami da ruqo hannunta tai saurin kallonsa a tsorace cikin sanyin murya yake magana kai kace bashine wannan Abbakar din data sani ba me fada da tsare gida .

Ummulkairi dan Allah su yaya Nasir basu birgeki ba tai shiru be damu da shirunta ba ya kuma Fadin yaushe zamu tare muma anamu gidan ta kalleshi gida eh gidanmu........

Gidansu mahfuz

Hankalin hajiyar mahfuz ya gama tashi musanman ganin anyi bikin Nasir an gama babu Mahfuz babu labarinsa tun tana tsanmaninsa harta dena hakan yasa ta kira number din matarsa danshi ko ankirashi akashe take.

Bugu hudu ta qari ringing dinta baza'a dauka ba sai ana biyar dinne aka daga cikin tsiwa take fadin wai waye haka ya isheni da kira na tsani irin haka ka kira sau daya sau biyu ba'a daga ba basaika haqura ba.

Eyye sannu maras mutunci to uwar mijinki ce taja tsaki in uwar mijina ce ai ba ita ke aurena ba sannu salma yanxu rashin mutuncin naki har ya kawo kaina aiko ba mahfuz kike aure ba na fice rashin mutunci gurinki balle duk asirin da muka rufa miki, wa kul hajiya kima dena cewa kun rufan asiri ai in bazaki ce na rufa muku asiriba na auren dan iskan yaronku zaifi kyau kice mun rufawa juna asiri tunda kinsan duk iskanci na banyi dan shege ba, ban kuma yi zaman prison ba.

Yanzu salma ni kike fadawa haka ai kedin ce naga kina neman kawo qabli da ba'adi yayi kyau daman ai gado kikai ni ban dana inaso muyi magana tsaki taja mai qara mtttwwwww gami da fadin au baki da number dinsa in da tana kunne aikinsan babu ta yadda za'ai in kiraki ko.

To yanzu yana hutawa ne banasan atakura masa zaki iya kiransa anjima bata jira cewar hajiyar ba ta kashe wayar.

Bin wayar da kallo hajiya tai ranta na quna wato rashin mutuncin salma har kanta.

Wayar Batulu ta kira bugu daya ta daga aminiyar ya akaine cikin fada hajiyar mahfuz ke magana ba wata amininyar yanzu batulu rashin mutunci da asirinki har kan yarona vatulu ta riqe ha6a kai kace tana gabanta tace haba Aminiyar me yafaru haka ai kema kinsan babu ta yadda za'ai inma mahfuz asiri to mene ribata ai dashi da salma ni duk daya ne me ya faru ne kike irin wannan batun.

Nan ta kwashe komi ta fadawa Hajiya batulu itako sai salati da tafa hannu na munafirci take haba Aminiyar sai kace bakisan halin salma ba aikinsan rashin mutuncinta harni ma yiwa take

batun kuma mahfuz ai kinsan se ahankali zai huce balle yaga kinqi goya masa baya ya daukaka qara ya amso yaronsa shiru hajiya tai kamin tace kumafa haka ne.

Kiyi hakuri zan kirata zan mata fada bazata sake ba suka taba fira kamin suyi salama.

Hajiya Batulu ce ta hau kiran diyar tata bugu daya ta daga suka ta6a fira duk kan asire asirensu ne kamin hajiya batulu ta dora.

Dazun muka gama da mutuniyarki ta fadan duk yadda kukai sedai inasan ki kirata ki bata haquri ki kuma barmata yaro yana zuwa gunta.

Kai infa basshi kika ce eh kema kinsan ita din ba daga nanba duda ni nasata ahanya anman kinsan sau da dama dan koyo yakan iya fun malaminsa nafiso se itama an kama mana ita ta dena zaton asiri muka nasa in ba haka ba kuwa zata iya ruguza mana komi.

Allah momey ina kishin inganshi da mace to ai ita uwassa ce kuma banda abinki mun riga mun musu farraqu abunda zai dunga mata na rashin mutunci sai tafiso kar yazo Allah umma kishi nake, tsaki hajiya batulu taja tace ke wace irin mutunce kima rasa kishin wa zakiyi sai uwassa to umma ita ba mace bace.

Kinga nace ki kirata ki bata haquri inba so kike in cire hannuna akanki ba to zan kira ta kashe sukai sallama.

Mahfuz na zaune yana musu gugar kaya ta shigo tana fadin honey ka kuwa kira hajiya ya dago yana sakar musu murmushi eh mana jiyafa munyi waya tadan hade rai kasan wace hajiyar nake nufi.

Akwai wata hajiya da na ke kira da ya wuce hajiyarki tadan saki rai kadan a'a hajiyar ka nake nufi ya hade rai in kirata in mata mene.

Haba nawan mahaifiya ce fa kadai daure ko sau daya ne ka dinga kiranta ta miqo masa wayar pls call her ya amsa yana wani shasshan qamshi shi kenan zan kirata dan ke tai murshin jin dadi.

Bugu daya ta daga haba mahfuz yanzu ka kyauta gabaki daya ka gujemu kofa bikin Nasir bakazo ba bakuma ka turo matarka ba sai anan ya samu damar magana, a'a hajiya ni ne ya dace nazo ban kuma ga damar zuwa ba matata adena samin ita cikin matsal tsalun gida ni kika haifa ba ita ba ya kashe wayar.

Rashin mutuncin Mahfuz kullun yawa yake yayin da matarsa kullin cikin sake shiri take ganin dagaske za'a kwace mata yaronta yasanta hajiyar mahfuz ko ta kan mahaifiyar salma abokiyar zuwa gurin bokayenta ba tai zamfara gurin hatsabibin bokanta.

Qarya da gaskiya bokan ya fadawa wa hajiya tahau tazauna daram komi ya hada mata kai tsaye gida ta koma.

Washe gari gidan mahfuz tai dan ai watar sa aikinta baya nan ta shiga ciki daman haka taso dan tasan ahalin yanzu yafi ma matar tasa rashin mutunci.

Sai dai me shiru falon kamar ba kowa cikin kujera ta tusa daya cikin asirin nata bata taba zuwa gidanba tun kawo salma sai dai tasan gidan sosai hakan yasa ta miqe tai dakin da ke kallonta kai kanta ke da wuya ta dawo da baya abin ya mugun daga mata hankali bata gazgata abinda ta gani hakan yasata qara komawa sai dai me abinda ta gani gaske ne.

Bawai gizo bane Salma ta gani da wani qato ba mijinta ba wato mahfuz suna sa6ama Allah hankalinta yai matuqar tashi sosai.

Dakin ta fada hankali tashe ganinta yasa mutumin yin waje dasauri salma ta bishi ta ruqoshi haba Darling mene haka atsorace yake ka kintsa se ka fita ba abinda zata iya mana.

Mamaki ya cika hajiya ai ku shi dai tuni ya fice hajiya ta kwadawa salma mari gami da jawota waje ashe iskancinki ba iya fatar baki bane haba salma da aurenki aka.

Anan falo hajiya keta surfa bala'inta tama mance da me yakawota gidan dan nata.

Ai kuwa Mahfuz na dawowa Salma ta miqe cikin kuka ta fada jikinsa tana fadin hajiya tazo ta mata duka abinka da aikin asiri tuni ya hau ya zauna hajiya me ya kawoki gidana nan hajiya ta hau masa bayani komi har halin da ta tsinci salma budar bakinsa sai cewa yai yanxu hajiya dan kawai kinajin haushi na shine sai kinma mata ta sharri.

Hajiya ta hau rantse rantse dan ya yadda da gaske take yace pls hajiya kije gida ganinki na qaran takaici wallahi dan kece kawai anman babu wanda zai daki salma in raga masa kema inkika ci gaba da zama zan iya sauya ra'ayi.

Ba shiri hajiya tabar gidan ranta bace har wani jiri take ji.

Gidansu Abbakar

Ummu tace gidanmu kuma bayan wannan da muke ciki yai dan murmushi kamin yace ai kinsan ba wannan gidan nake nufi ba namu mu uku nida ke da takwara na ko shima yasamu qanne ta sunkuyar da kai ganin ya bata kunya yasa shi sauya maganar da fadin.

Wai me yasa bakya hawa facebook account dinki tace haka kawai kuma inna kira number din dana sanki da ita bata shiga tace ai ta bata tun kan na tafi Niger, to da wacce kike anfani babu tace.

Miqo masa ta hannunsa yai ungo kafin in siyo maki wata ta kalleshi yamata kwarjinin da bazata iya cewa a'a ba ta amsa.

Tace ka buden se kin amsan tambayata wacce tambaya ta tambaya yaushe zamu tare anamu gidan tai dan murmushi kamin tace sai randa hajiya ta yadda.

Ya kuma mai maitawa haka kika ce ko tai shiru yadan dubeta kadan kamin yace waini yaushe qanwata ta facebook me magana, fira da barkwanci ta koma miskila ne tai dariya ai daman ko waya muke ni kasan ba magana na cika ba basshi achat din yai dariya wato haka ne ta gyada kai nasan me zanyi ya dauki Takwaransa dake kan cinyarta ya bude qofar sukai cikin gida.
[1/13, 4:24 PM] 🅰 " AXEEX✌🏻 D'🅱🅾Y😎: _POST BY GROUP OF HYPE HAUSA NOVELS BOOK WHATSAPP 08064400100_ 📚📚
[1/13, 4:25 PM] 🅰 " AXEEX✌🏻 D'🅱🅾Y😎: *ABBAKAR*

*PAGE 180---190*

*Pls kusani a addu'a wallahi bani da lafiya sosai ni kadai nasan me nakeji dakyar ma nayi muku wannan zaku iya jina shiru kwana biyu*

Abun duniya duk ya ishi Abbakar gashi dai yanajin haushin mahfuz sakamakon abinda yai tayi bacin mugun kishinsa da yake ji sai dai kunsan in akace abotar gaskiya wacce take ta tsakani da Allah ko me mutun ya maka wannan san sabida Allah kullin yana nanne.

Gabaki daya ya damu musanman ganin anyi bikin Yah nasir ba Amininsa ya kuma tambaya yah Nasir yace masa wayasan masa tun lokacin yakesan zuwa gidansu sai dai yana tsoron jarrabar Hajiyarsa dan inta mahfuz ne daman sun saba suyi su shirya.

Yanke shawarar zama abakin lokonsu yai ko zaiga aqallah wucewar Aminin nasa dan tabbacin lafiya yake sedai yau kwana hudu babushi bare labarinsa.

Zaune yake gaban hajiyar Mahfuz duk ta rame tai baqi yadda ta amshe shi ya bashi mamaki dan yayi zaton da fada ne sai wani nan nan take dashi.

Sun gaisa yake tambayarta mutumin me makon ta bashi amsa kawai sai ta fashe da kuka yai yai tai shiru taqi sai da tai me isarta cikin shessheqa take fadin Habu haqqine ke cina nakuma san bana kowa bane saina ummulkhairi da iyayenta.

Shi dai da ya samu tai shiru ya danji dadi kadan duda zuciyarsa cike take fal da tunanin me yasamu Aminin nasa "nace uhum Abbakar kenan Allah ya baka zuciya me kyau"

Hajiyar mahfuz bata boye komi game da halin da mahfuz ke ciki ba harda wanda data je gidan ta tadda matarsa, sai dai bata fada masa zuwa gurin bokan da taiba da dalilin zuwa Hankalin Abbakar ya tashi yasan mahfuz yana shaye shaye dan baya boye masa komi anman

baya bin mata shi yasa lokacin ya fada masa game da ummu yaita masa fada yanzu tsoronsa daya kar matarsa ta saka masa cutar wannan zamanin.

Nan yaita lallashin hajiyar yana bata haquri yasamu ta dan dawo nutsuwarta kamin ya dora yanzu addu'o'i yakamata ayi tayi masa zansa a masallatai da makarantu ki yawaita masa sadaka da niyar Allah ya karya koma mene taji dadi sosai dan ita tama mance da batun addu'a din.

Kai tsaye gidan Nasir Abbakar ya nufa ya sanar dashi duk yadda sukai da hajiya shima hankalinsa ya tashi ya yadda da shawarar Abbakar tun daga lokacin su ka duqufa sosai ko sallah ce ta kai Abbakar masallaci sai ya roqi asa abokinsa a addu'a.

Sannu a hankali farraqun da aka masa da hajiyarsa yaji ya tsani zuwa gurinta ya kau dan yanzu yana zuwa sosai fiye da da, duda har yanzu cike yake da tsoron matarsa gidan nasu ma aboye yake zuwa.

Da zuwan da yake ne Babban wansu muktar yai anfani tofin da yake masa azam zam ya hada da dabinon ajuwa indai yazo se yasha in yaqi dole suke masa.

Awayo a wayo yayan nasa yake nusar dashi sallah dare in addu'o'i kamin kwanciya bacci da neman tsari dan shi din ba daga nan bane yasan illimin addini sosai kawai dai irin ansani ne bashi da anfani tunda ba'a aiki dashi.

Sannu ahankula tsoron matarsa ya fara barinsa har mamaki yake in yaga tazo ta tsaya masa aka tana bashi umarni kawai kallonta yake sedai ya kasa daukan mataki.

Hankalin Salma da hajiyarta yai mugun tashi ba kadan ba ganin har Niger sun kai sunan mahfuz gurin hatsabibin bokansu wanda duk wanda suka kai ya gama yawo anman kulin abubuwa qara tabarbarewa suke.

Yau sunyi da matarsa zaiyi tafiya zuwa university of ibadan dan yin wani abu murna take sosai dan ta gaji dashi sosai gashi tsoro ya hanata kawo kowa dan daya fita yake dawowa.

Wanda zasuyi tafiyar tare ke fada masa su bari se gobe hakan yasa ya wuce gidansu suka taisa da hajiya sukai yar fira kafin suyi sallama ya wuce gidansa.

Da ace nasan mahfuz yasan me zai tadda da tabbas da bazaiyi sha'awar zuwa gida ba hankalinsa yai matuqar tashi idanunsa duk ya rife bema san me ya rarumo ba yai kansu.

Duka kawai yake babu qaqqautawa ganin zai ita kashesu yasa kwarton yin ta maza yai waje a miliyan ya koma kan salma dake gefe a rakube tama kasa motsawa duka kawai yake tai mata lilis dagyar ta rarumi zanin gado ta arta aguce.

Biyota yai yana ci gaba da duka yana fadi Allah ya isa tsakani na dake na sake ki saki uku har farfajiyar gidan dagyar me gadi da driver suka riqeshi ita dai data samu tai waje adai daita ta hau se gidan ubanta.

Agurin Mahfuz ya zibe yana kwasar kuka shi kadai yasan abinda yakeji yanzu ransa bai taba yadda cewar inkayi zina da wata mace se anyi da wacce take mallakinka ba sai tau matarsa ta sunna kuka kam yayi shi bakadanba tausayin yaransa mata ya kamashi innalillahi wa'innailaihi raji'un yake fade kawai Allah ka temake ni katsayarmin iya nan wallahi nayi nadama ya Allah karka dorawa yarana abinda ni nayi sanbatu kawai yake.

Gidan ji yake gabaki daya ya zame masa kurku ku ba abinda yake gani sai matarsa da wani gidanma gabaki daya ya bari yai gidansu.

Cikin kuka yake fadawa hajiyarsu komi baima qarasa ba suka jiyo masifa a waje da sauri hajiya ta miqe tai waje Hajiya Batulu ke ta sirfa masifa salma na bayanta.

Fadi take ina Karimar take wallahi dukan da dan iskan yaronki yama yarinyata akanki zan rama mata ganin hajiyar yasa tai kanta gadan gadan aikan daga hannu tai zata zuba mata wayar dake hannunta aiko muktasir yako riqeta kul bazai yiwu kizo mana gida dan rashin mutunci kice zaki dakar mana uwa ba kinyi kadan.

Kamin ya qarasa tasakarma Hajiyar tasu nari itama taji kuwa an dauketa dashi wa zata gani mahfux ne namfa yaran suka mata lilis ita da salma sai da hajiya taga zasuyi kisa tasa baki suka kyalesu.

Hajiya batulu fadi take wallahi, Wallahi sai kinyi danasanin ni kika ma haka kinsan da cewar gabaki daya a tafin hannuna kike shirya karbar sakamakonki, hankalin hajiyar mahfuz ya tashi dan tasan me take nufi su kuwa yaran ina suka sani fadi suke abar mana gida yayanmu ya rabu da bunsurar yarinyarki ya wuta da kuda.

Kai tsaye maqabartar dan dole ta nufa daga gidansu mahfuz din yaron da ta baima aikin binne binne tace duk ya je ya haqo mata ya kawo mata yace an gama.

Inda ta sa aka kai na tsohuwar rijiya ma duk aka ciro ta tara shirgin asiri tim gabanta ta zuba musu kalanzir gami da kunna ashana tuni suka hau ci da wuta.

Tasaki wata dariya Wallahi hajiya karima dani kike zancen kin riga kinyi sake da kika bari ni nasan sirrin komi naki waike uwar san jiki sedai ki bada kudi ni inje miki gun boka inkuka miki aikin yadda nasa aka binne na haqesu yadda naje nayi miki kike rayuwar fantamawa kike mulkar kowa gidanki to kuwa kinyi kadan.

Tun safe hankalin Hajiyarsu mahfuz yai mugun tashi ganin Baba tijjani da baba usman matsayinsu na qannen mijinta me rasuwa da sukazo gaidata suke tambayarta ina Ummulkairi

ne basu ga tazo gaidasu ba wato tunaninsu game da yar qanin nasu ya dawo yanzu in mahmudu ya dawo me zata ce masa wato wanda yake me matsayin babba gidan yanzu.

Tasan ko mijinta be kaishi san diyar qanin nasa ba.

Ilai kuwa yana dawowa yaran kowa yaje ya masa barka da dawowa yana ta zuba idon ganin diyar tasu sedai shiru bayan yai wanka yaci abinci ya debo tsarabarta yayo bangarensu wato bangarensu Hajiya karima tunda anan yasan take tun rasuwar mahaifiyarsu.

Dakinta ya shiga sai dai yadda yaga dakin ya tabbatar babu mutun aciki duk yayi qura yai cudun cudin.

Tun yayansa nada rai basu cika shiri da karima ba hakan yasa take shaskarsa afusace ya futo yake kwala mata kira ta fito da sauri ina kuka maida yarinyar nan cikin rawar murya take tambaya wace yarinya fa.

Cikin fada yake magana zan tambayi wata yarinya bayan ummulkairi ta gurin Yasir hankalunta yai mugun tashi tama rasa amsar bashi dan gabaki daya ta gama rudewa.

Nasir ne ya shigo jin rikicin da ake hankalinsa ya tashi daqyar ya samu kawun nasa yai shiru ya zauna ya masa bayanin komi game da ummu har aurenta yanzu sedai bai fada masa wata aura dinba.

Hankalinsa yai qololuwar tashi yanzu duk yaushe hakan ta faru bamu sani ba yama akai haka cikin kuka hajiya ke fadin abin duk tayi ya miqe yana salati wallahi karima kinban mamaki ashe zaki iya haka nasan duk bazai wuce kan wannan gidan ba da yake mallakinta to gabaki daya kinja muku kowa gobe zai bar gidan daman ai ba namu bane muna zaune dan iyayenmu ne yanxu tunda suma basa raye se abarma me gida gidanta.

Gidansu Abbakar

Sabo sosai da shaquwa me qarfi ta shiga tsakanin Abbakar da ummu kullin suna farfajiya tare duda yawanci da maryam ko ummi ake karatun anman kallonsu kawai kai kasan da masoya ne masu san junansu iya so.

Duk yadda Abbakar yai yayi da hajita tace ina itafa babu zancen tarewa yanxu dole se ummu ta gama katatu ganin da gaske take yasa zuwa ya sami kawunta ya rattaba masa komi.

Aikam yasha fada kanyin aure bada saninsu ba yaita bashi haquri yace zaije ya sameta yaje ya fadowa nasa kawunnan yace to.

Gidan qaramin kawunsa yaje ya fada masa dan yasan inyaje gidan wan babansa dukansa ne kawai bazai ba dan mutumin kwai fada.

Shima kawu Barau din da bai cika fada ba yau ya ta6a dakyar Abbakar yai ta bashi haquri har ya yadda zaije ya fadawa wan nasu.

Aiko dakyar yasha kan yayyen nasu suka yadda zasu saka baki akan auren dan nasu.

Hajiya ta yadda ummu zata tare da sharadin dole aje dangin ummu su san da batun auren ba musu suka amince.

Gidansu Mahfuz

Washe gari da sassafe Baba mahmud ya tara qannensa ya fada musu komi harda hukuncin da ya yanke sun yadda kan jibi iyanzu sun bar gidan agurin ma wasu cikinsu suka fara kiran motar da zata kwasar musu kaya.

Ba wanda bai jin jina halin da ummu ta shiga ba da tausayinta agurin suka yanke shawarar sanya cigiyarta dan nasir bai fadi inda take ba zatonsu ta bace yanxu, hankalinsu bai qara tashi ba sai jin abinda mahfuz yai wasunsu ma ji suke kamar su dakeshi tada kam yashashi harda masu cewa basu bashi tunda ya rasa wanda zai ci mutunci sai yar uwarsa.

Abbakar ne yazo gidan kan kawunnansa nason zuwa ganin su baba mahmud yai mamakin ganinsu gabaki daya mahfuz nafaman kuka.

Ada baba mahmud yace sedai in wani satin anman jin yace kan ummulkhairi ne yace su zo yau da yanma kawai.

Tarba sosai suka samu duda gidan a hargitse yake kowa na qoqarin hade kayansa ne sosai hankalin su Baba mahmud ya tashi kanjin har wani aure akama ummu bama da saninsu ba.

Budar bakin Baba mahmud se cewa yai ai ina maganar tarewa bai taso ba yadda akayi mata dole barin gidan nan ina da tabbacin dole aka mata aka mata aure dan haka kawai kuce ya bata takardar ta yarinyar mu nada gata in ta sami wanda take so to lokacin zamu aurar da ita.

Komi suka ma Abbakar bayani game da yadda sukai da iyayen ummulkairi aikam hankalinsa ya tashi sosai da kansa yaje yasamu baba Mahmud aikan rufe ido yai kamar be sanshi yahau yazauna sakin ummu dole gida Abbakar ya dawo ya sanar da hajiyarsa.

Itama hankalinta ya tashi taje har gida ta sami baba mahmud sun gaisa cikin mutunci ta masa bayanin komi yai murmushi fiddausi kenan nasan kun mana da kuka riqe mana yarinyar nan anman hakan baya nufin zamu biya ku tukwici da yima yarinya auren dole dan kawai danku nasanta.

Duk yadda hajiya taso ya fahinta ya kasa fahinta haka ta tawo gida rai babu dadi.

Ganin yayi duk yadda zaiyi ne kan sakin ummu Abbakar yaqi yasa yanke shawarar zuwa har gidansu Abbakar din ya dauko ummu  ya kuma sanar musu tabbas qara zai shigar indai nanda kwana uku bai kawo sakinba.

A gidansu Abbakar tabar yaron nata Abbakar gurin hajiya dan ta yaye mata shi.

Ummu tai mamakin ganin gidan da ya kaita can unguwar karkasara me makom nan naqotansu Abbakar bata tambayi dalili ba dan ranta duk babu dadi bataso barin gidansu Abbakar ba tayi sabo sosai dasu bana wasa ba tanajinsu aranta anman batasan nunawa kawun nata iyakarsa.

Komi sabo aka saka mata adakinta ita da Abbakar dinta ahankula tadan fara sabawa da zaman gidan babu inda take zuwa dan anyi hutun sch balle tasa masoyinta a idanunta ko bacci basosai take ba cikin tunaninsa take.

Bata taba zaton tanasansa haka ba sai yanzu dan ada tana qoqarin yakice shi zatonta bazai taba santa ba anman yanzu da ta riga ta saba dashi ta saba fira dashi ya koya mata sansa ji take raba ta dashi kamar ta'addanci ne babba sedai ita batasan me zatai ba.

Satinta biyu gidan baba mahmud yaje ya amso Abbakar qarami dan ganin ummu taqi sakewa zatonsa ko rashin yaronta ne tunda Nasir yasanar masa tanasan dan dayawa.

Kwana biyu yaron ya saba da kowa dan baida rikici musanman gidan da yake da yara sunzo hutu jikokin gidan sai warkajaminsa yake abinsa.

Tunda ummu tazo gidan bata ta6a farin ciki irin na yauba taji dadi sosai  Baba mahmud ne yazo yafada mata ta shirya zasu Jordan can gurin ummanta tai murna ba kadan ba.

Nan ta shiga hada musu komi dan gobe ne tafiyar ita da Abbakar dan su uku zasu tafi daga ita sai danta sai baba mahmud.

Yanzu abu daya ke damun ummu rashin masoyinta Habunta anman indai fannin iyayene duk cikin yayun babanta kowa nan nan yake da ita danma taqi sakewa dasu kamar da.

Sun shiga mota ta tuno ta dauki wayarta ta turawa Abbakar saqo pls izini zamu jordan a samu a addu'a afadawa hajiya.

Baba mahmud na kallonta tai kamar be ganta ba yace kawo yaron jeki kice ma kadija ta baki saqona tace tota miqa masa yaron tai ciki ya dauki wayar yana duba saqon.

Har ya turo amsa Allah yasaukeku lpy abar sona dan Allah kiyi wani abu kar a rabamu pls ajiye wayar kawai yai ganin ta tawo.

A Jordan

Bayan sun sauka mota ta daukesu sai gidansu ummanta kowa yaji dadin ganinsu musanman kakanninta sai washe gari aka dibesu zuwa gidan umman nata.

Tunda ta shiga falon ummun nata kishi ya rufeta ummanta ce jikin bango a hoto sai yara suma larabawa uku manne jikinta mijinta gefe tai saurin dauke idanunta daga hoton duk inda ta duba sune.

Yan matan biyu masu kama da ita suka fito dan ganin su waye ganinsu yasa komawa ciki da gudu dan kiran momy dinsu suka fito tare har namijin wanda da gani shine qarami befi 9years ba kishi ya rufe idon ummu hawaye ya fara kai kawo aidonta.

Wato ummanta ta ma mance da tana da yarinya a Nigeria tayi aure ta samu wasu ita ta badda marainiya ba uwa ba uba tunda ta yayeta ta tafi bata kuma nemanta ba.

Danta ta sura taja baba mahmud mu tafi nafasa banasan ganinta muje Kawai take fada tana kuka ganin bazai tafi bane yasa sakinsa tai gaba.

Dasauri umman nata tai gunta dan tana dan fahintar hausa ba sosai ba ta ruqota gami da dorata a kafadarta tana lallashi dakyar tai shiru.

Haba ummu kin taba ganin inda uwa ta mance da danta kina raina babu yadda zanyi ne.

Yaran sukaita kawo mata abu buwa wasu duk hotunan tane jiki tana qarama sunata murnan ganinta seda ta kula sosai taga ashe hoton farko ma kana shigowa shi zaka gani kamin nasu dukansu itace rungume jikin umman nata da alamu ma ranar da zasu rabu ne tadan share hawayenta kamin tace cikin harshen turanci dan larabcinta be kwari sosaiba.

Anman mum me yasa haki kuma wai wayata ba.

Ummu babu ce tasa tun bayan dawowata daga qasarku babana yai rashin lafiya sosai duk abinda muke dashi dana gadona duk ya qare gurin jinya  har bashi muka dinga amsa qarshe ya rasu.

Shekara daya da rasuwarsa na auri babansu Nasrin shi ba wani me arziqi bane da zai iya daukan nauyi na inzo nageria albashi nama haka muke hadawa gurin kula da yaranmu da iyayenmu dan da nasa iyayen da nawa duk suna buqatar temakonmu.

Ummu ta kuma rungume ummanta tana qara bata haqurin fahintarta bai bai.

Koda Dahir ya dawo bakowa falon sai ummu yana ganinta ya ganeta dan yasan basu da dan uwa baqar fata sai diyar matarsa bayan mugun kama da sukai da matar tasa.

Da sauri ya qaraso ya rungumeta yana fadin ummulkhairi ya kuma dubon fuskarta dadi ya cika ummu tabbas ummanta bata mance da ita ba tunda har mijinta da akasan larabawa da kishi yasan da ita.

Watanta guda cif taji dadin zama dasu sosai soyayyar uwa kam se yanzu tasan me ake nufi da ita dabadan tanasan mijinta ba babu yadda za'ai ta yadda tabi baba mahmud Nigeria.

Sunyi shawara dashi kan tanasan kudinta na account dinta ya cire mata zata baima ummanta dan ta fusksnci suna wani hali tunda ita ba abinda take dasu ya amince.

Aikam tasha albarka dakyarma umman nata ta yadda suka amshi kudin haka ummu ta tawo suna kewar juna.

Nigeria

Ummu ce biye da Abbakar yana ihu shi baza'a masa wanka ba ya 6oye jikin baba mahmud yai saurin dagoshi mutumin lafiya dai kake yawo ba wando se nasa anma kaciya ko baisan kaciya ba yasa dariya baban ya nuna masa gurin nan zansa a yanke ya tsanyara kuka ummu taja ta tsaya turus ganin abinda ke faruwa.

Hajiyar mahfuz ce tsaye tana kuka tana roqon baba mahmud ya batta taga ummu zata nemi afuwa, ganin ummu tayo gurin zata zube qas ummu ta dagota tana girgiza kai alamun a'a.

Umma ni na yafe miki karki durkusa min ha juma da mancewa da komi hajiya taita godiya harda daukan Abvakar taita masa wasa.

Tun daga lokacin ba'a sati sai hajiya tazo gidan se alokacin ummu tajiashe kowa yabar gidan taje taita roqon baba mahmud dakyar ya amince kowa ya koma gidan tace ita indai gida nata ne to kowa ta bar masa bangaren da yake bangaren Abbanta kawai takeso da kakarta.

Farin ciki ya dawo gidan kowa nasan ummu Abbakar qarami haka kowa nasansa ko yaushe yana gun hajiyar mahfuz.

Mutun daya ne ko kallonsa ummu batayi shine mahfuz dan sosai ta tsaneshi danma yanzu yana yawan shiga sabgar danta komi ya samu sai ya kawo masa yaron shima bini bini uncle mahfuz a bakinsa abinda kedan rage mata haushinsa kenan.

Ummu zaune gaban baba mahmud daman zancen rabuwar aurenki ne nayi shiru da batun zuwa ki dawo daga jordan wani satin zamu fara zaman kotun.

Tama rasa me zata ce hankalinta ya mugun tashi ko bakiji bane to kawu Allah ya kaimu ta miqe tana tangadi dan jin jiri na qoqarin kwasarta tana shiga daki ta fashe da kuka.

Yau aka dawo da Abbakar daga gidansu Abbakar babba daqyar ya dawo danshi in ya je guri dagyar yake yadda ya dawo sabida sabo seda Abbakar babba yai masa dabara ya tafi yanata kuka.

Baba mahmud ya bita da kallo kamin ya miqe yai cikin gida dan dauko Abbakar za'a masa kaciya dan sanyi yazo.

Kai tsaye gurin ummu yai da yaron ya tsaya abakin qofa jeka ka kiramin ummanka ya shiga da gudu yana fadin mome tizo mamu afi anguwa tai saurin goge hawayenta ta dubi yaron.

Ya mata kyau sosai jitai kamar tace abar kaciyar se ya kuma girma tadai daure muje to yasa kuka auke shi wai ta daukeshi tai dariya dan rikici gami da daukansa.

Har mota ta kaishi gami da shafo kansa suka fice yana daga mata hannu.

Yara da yawa an musu kaciyar a idansa yaga suna  fitowa yadda yake ganinsu yasa shi fara kuka.

Hankalin masu kaciyar yai mugun tashi ganin yadda yake bleeding abin ya wuce hankali dole suka futar dashi daga dakin zuwa dakin temakon gaggawa.

Likitoci sun duqufa kansa tuni suka gano ai haemophiliac ne jini duk yadda sukai ya tsaya yaqi gashi babu allurar da ake musu masu cutar a asibitin se ma anje zariya babu tabbacin ma kan aje yana raye.

Jini na zuba ana qara masa wani yaron yayi mugun jiqata rai ahannun Allah hankalin baba mahmud ya tashi tuni ya buga waya zuwa gida.

Ko ummu va'a fadawa ba suka bayyana a asibiti harda su Abbakar kowa ya tausaya ma yaron kowa ya damu dan yaron ya shiga ran kowa.

Minti talatin tsakani Abbakar ya rasu dedai da baba mahmud duk dakiyarsa seda ya zubda hawaye dan mutuwar ta dakeshi kai kace wani babba ya rasu.

Su kansu ma'aikatan sunji mutuwar dan dan awannin da yaron yai gurin kamin fara kaciyar yadda yake da faran faran da surutu har sun saba.

Komi Baba sani ne yayi aka basu gawar sukayo gida dan baba mahmud ya kasa komi gani yake kamar qarya ne yaron be mutu ba yanzu yanzufa suke wasa da dariya dashi ina shibqarya ne be mutu ba......

*Alhamdulilah jiki yau sauqi nagode sosai da addu'oinku gami da fatan alkairi*

Kai tsaye gida akayi da gawar ba wanda bai share hawaye ba cikinsu musanman ma wadanda suka ga yaron ayau da jiya se abin yake ta dawo musu sabo.

Ba abinda mahfuz yake se sharar hawaye haushi da tsanar kansa duk sunbi sun masa yawa shi ne sana diyar zuwan yaron duniya yaso ace yaron ya girma ya masa gata sedai gashi yama tafi besan waye mahaifinsa ba, ya kuma share hawaye lokacin da ya tuna ganinsa da yaron na qarshe.

A wasa yake masa magana my boy yau agurina zaka kwana ko ya maqe qeya a'a ni yau gurin dady na zani to ai nine dady naka yasa dariya kai uncle dina ne dady na biyu dadyn aunty farida(Nasir) da dady me sunana, bemasan sun iso gidanba seda Abbakar ya ta6ashi yai saurin futowa daga motar.

Gawar ce riqe hannun Abbakar ji yake kamar yaron zai farka yasa masa kuka kamar ko yaushe yace se ya bashi alawa kwallah ta tawo masa wadda ya kasa tareta, mahfuz yai saurin Amsar gawar shi kuma ya goge hawayensa.

Nasir kam ya kasa komi qafafunsa ma gabaki daya sunyi sanyi inbanda soyayyar uwa daban take to da nace ba wanda yafi nasir san yaron koda yake ko ummun batakaishi shaquwa da Abbakar dinba, shi har yanzu baima yadda wai yaron ya mutu ba jira yake kawai yaji sunce masa ya farfado.

Se kace ba dazu da safe ne da yazo gidanba yaga yaron yanata wasansa har dazai tafi yake masa wasa dady yau zamu unguwa da baba yace zai sayon kayan dadi cikin tsamin murya ta yara yake magana wadda seka zauna dashi zaka fuskanceshi.

To nima aragen kayan dadi yai dan jim sedai inzaka siyon wasu se insamma ka yai dariya ya lakuce hancin yaron kaji me wayo to naqi wayon naka shima yaron yasa dariya gani yake kamar alokacin abin ke faruwa bema san sanda shi kansa ya saki murmushi ba.

A bangaren Baba mahmud aka ajiye gawar dan anan za'a masa komi ba tare da wani 6ata lokaci ba aka dora ruwa baba mahmud ya kawo likkafani dan akwai da yawa adakinsa.

Ita kuwa ummu baiwar Allah tun lokacin da tasaka Abbakar amota takejin wani iri har dago mata hannun na baibai da yake mata ta kasa mantawa ji take kamar taje daukoshi in ya qara girma ayi kaciyar har motar ta fice bata denajin ba dadi ba duda yaron yasaba mata haka anman yau se takejin daban kodan za'a mai kaciya ne ta fada aranta gami da komawa bangarenta.

Tun dawowarta gidan bata shiga ko ina sai taje ta gaishesu shi kenan se karatunta kawai tasa agaba se kuma in yaronta yanan ta kunna musu kallo ko yaita mata hirarsa ta yara.

Tunani kala kala ya dabaibaye mata zuciya hakan yasa ta miqe ta shige daki danyin walaha kamar yadda ta saba.

Bayan ta idar ne ta dan kwanta danta huta batamasan sanda bacci yai gaba da ita ba.

Se wajen sha biyu ta farka adan firgigit ta farka tai saurin yin falo dan tasan yanzu Abbakar andawo dashi tasan yanacan yanata zuba shagwabar tasa daman qaqa balle an masa kaciya ita kam yau gurin Hajiya zai kwan dan bazai hanata bacci ba abinda take ta ayyanawa arai kenan.

Ganin falonta wayam yasata yin murmushi tasan yana gun hajiya kodai ta mahfuz ko kuma ta bilkisu wato matar baba mahmud.

Gyalenta ta dauka tai waje kai tsaye bangaren su mahfuz tai duda batasan zuwa sosai sedai takan danne dansu yadda dagaske ta haqura komi ya wuce din

Ba kowa anan ta danji wani abu aranta anman da ta tuna yadda kowa keji da Abbakar tasan kowa yana gurinsa hakan yasa ta juya zuwa 6angarenta.

Alawar da yafi so da madarar da ta hada masa tun safe kan inya dawo ta bashi ta dauka, dan tasan indai taje yaganta ko kasuwa ce gabansa se yasa kuka seta lallashe shi ta bashi alawar zai shiru.

Tunda taci karo da ummi qanwar Abbakar jikinta ta bata wani abu ta share tunaninta ko ran ummin ne a6ace kawai.

Tana shiga an kammala hadashi yaro yai tsawo kamar badan shekara uku zuwa hudu ba yai kyau fuskar nan ta kara haske kwance yake san6al kan tabarma kamar kai masa magana ya amsa.

Da sallamarta gami da fara'a ta shiga falon sedai yadda taga mutan ciki yasata tsayawa soro tai turus tana binsu da kallo.

Kowa ita ya zubama ido bawanda yai zaton ganinta ayanzu ta tsaya kawai tana binsu da kallo ta kasa gaba ta kasa baya ciki zatai ko waje.

Me makon taga yaronta yana mata kuka yana auke shi saidai ta ganshi kwance cikin siffar wanda ya mutu ina ita yaronta be mutu ba da sake abinda take fade cikin ranta kenan kama ce kawai Abbakar dina da ransa wallahi.

Jitai ana jan hannunta tai saurin kallon ko waye Nasir ne ta gani har gaban gawar ya kaita ya durkusar ta gami da saurin barin gurin dan baisan mai zaice mata ba.

Waye wannan take fade cikin daga murya kai kace bata sanshi ba ku fadin kuma karku cemin wannan yarona ne danni yarona da ransa.

Abbakar yazo ya riqeta ki nutsu ummu kar soyyar yaronnan tasa ki kasa fahintar gaskiya gabaki daya ta kasa kukan ma ta miqe gami da yin waje baba mahmud yace da hajiya subi bayanta.

Kai tsaye 6angarenta tayi ta dauko zaninta na atamfa guda biyu ta dawo inda gawar take abu kawai take kamar tababbiya.

Lulluba masa tayi ajikinsa gami da kinkimarsa daqyar tasashi cikin makarar yaran da aka kawo dan kaishi, ta kamo hannun baba mahmud babu ku yi saurin kaishi inda take mazauninmu na gaskiya gaggauta kaishi shine mun masa gata ta koma kansa gami da kuma bude fuskarsa ta shafata se alokacin kwalla ta kawo mata.

Tai saurin shanyeta gami da fadin Allah ya jiqanka yarona Allah yasa kaidin me cetonmu ne se munzo muma munan tafe ta miqe har taikai bakin qofa ta dawo ta dauke alawar da madarar da ta kawo masa da kayansa da aka cire masa tai waje.

Kowa ya cika da tausayinta  kwallar su duk ta qaru.

Tsam ta rungume kayan inta tuna basu tai niyar saka masa ba yasa kuka sesu dan tare dashi ake za6o masa kayan sawa.

Tana shiga daki ta rufo qofa gami da tsayawa jikin taga tana kallo aka fito dashi akai waje dashi ba abinda ke bakinta se Allah ya jiqanka yaro na yayinda idaninta keta hango mata shi dazunnan da yake mata bai- bai zasu fita a mota yanzu gashi za'a fitar dashi a motarsa ta qarshe babu damar ya mata bai baidin.......
[1/13, 4:25 PM] 🅰️ " AXEEX✌🏻 D'🅱️🅾️Y😎: _POST BY GROUP OF HYPE HAUSA NOVELS BOOK WHATSAPP 08064400100_ 📚📚
[1/13, 4:27 PM] 🅰️ " AXEEX✌🏻 D'🅱️🅾️Y😎: I*ABBAKAR*

*190---200*

Tananan tsaye bakin qofa cike da tunani fal ciki bama tajin bugun da tun d'azu ummi mariqiyar Abbakar keyi.

Ita kuma ganin tayi bugun shiru yasa ta juyawa dan yin bangaren su Bilkisu kamar ance ta kalli jikin taga  takai kallonta nan, antin tata tagani tsaye tai saurin komawa ta tabota tai firgigit takai duba inda taji an ta6atan.

Ummi ta gani tsaye riqe da sweet campo tana mata murmushi tai saurin zuwa ta bud'e mata qofar yarinyar tai ciki tana kwalawa Abbakar kira tana waqa ina kake ne dan kaciya da warin

tusa nazo da alawata bani baka se kayi tusa me wari naji.

Ummu kasa ce mata komi tai tashige cikin daki ganin ta dube ko ina baya nan yasata fitowa anti ina aka kaimin baby na dan haka take kiransa kalli har tsarabar kaciya nayo nasa shine za'a kaishi wani gurin ni wallahi adawon da yarona ni da kaina zan iya kula dashi tun ganin gawar danta se yanzu taji kuka ya tawo mata na sosai.

Sosai ta fashe da kuka ganin kayan da ke riqe hannun ummi alawa ce, sai fan milk guda biyu da mangwaro irin katon nan duda tasan sunada su a fridge hakan besata siyo masa ba.

Saurin watsar da kayan hannunta ummi tai tayo gurin antin nata tana tambayarta me yasata kuka hakan ya qara sawa ta rushe da sabon kukan

Seda tai me isarta sannan tai shiru inda ita ummi ganin taqiyin shiru yasa ta tuni fashewa da nata kukan, ganin haka yasa ummu daurewa tai shiru.

Miqewa tayi taje ta zuboma ummi Abinci ta miqa mata ta kalleta da zimmar yin magana ta juyar dakai karki cemin komi kici abinci kawai tun jiya rabonki da abinci ina kallonki baki ci abinci ba kika tafi.

Seda ta gama ci sannan ummu tace kije ki kwa6e kayan in yaso sekije can bangaren baba mahmud ki zauna insan zama ni kadai bata kawo komi ranta ba ta miqe tai daki duda tanasan jin dalilin kukan antin tata sedai batasan ta kuma sata kukan.

Acan 6angaren baba mshmud ummi ta shiga tasha jinin jikinta ganin duk mutan gidan anan babu kuma alamar wai suna farin ciki ne.

Fadila ce yar gidan Baba kabiru ta mstso dab da ita ta dafata tace ummi ya haquri kumi ta kalleta soroso haquri kuma ta fada eh mana haqurin danmu wato Abbakar ta miqe wane Abbakar kuma.

Zee ta matso babyn ki mana da yake duk sun san haka take ce masa tai saurin barin falon rasa inda ma zata tayi kasa shiga inda ummu take tai tai bayan gidan tahau rusa kuka.

Iya shaquwa ta shaqu da yaron ashe bazai girma ta ga aurensa ba kamar yadda kullin take buri tun yana zanin goye ta saba dashi da masa komi har ya bude ido yai wayo yake kiranta da umma ashe dazu ganin qarshe tamai da zata tafi makaranta ta makara sun fito tana riqe dashi tai masa wanka ummu ta fito tana fada banace inkin makara ki dinga tafiyarki ba banishi nan ta amshe shi maza jeki ki shirya.

Ta fito ta biya ta dakin ummu yana zaune kan cinyar mumyn tasa suna za6ar kayan dazaisa tace anti ni natafi to Allah bada sa'a kije ki amshi kudinki gurin kawu to tace gami da lakace masa hanci baby se na dawo yasa dariya tai waje.

Jitai an dafa ta tai saurin goge hawayenta gami da juyowa Yah Abbakar ta gani ya komar da ita yazaunar shima ya zauna.

Haba ummi ki dena kuka duk me rai mamaci ne addu'a zaki masa ki kuma dena kukan kinga in momy dinsa taga kin tada hankalinki ita nata kuma tashi zaiti ki daure ko ita take kukan kiyi ta rarrashinta kinji ko to tace gami da kuma share sabon hawayen da yazo mata da sharje majinar a hijabinta irin na me kuka.

Yaita mata nasiha seda yaga tai shiru ya miqe yanzu kije can kisa taci abinci nasan tun safennan bata ci komi ba to tace ta miqe tai cikin gida.

Duk qawayenta sun zo mata gaisuwa har wasu cikin mazan ajinsu Ahmad har mum dinsa seda tazo dan ita har Abbakar din tasani.

Su Aisha ma kullin suna tafe kullin kuma basa gajiyawa da yima ummu nasiha duda tana qoqari sosai wajen boye damuwarta.

*Bayan wata hudu da rasuwar Baby Abbakar.*

Sannu a hankali ummu ta fawwalawa Allah ta riqi karatunta da diyar ruqonta duda wani sa'in takan tuna da yaronta sedai addu'a kawai take masa.

Yan abu daya ke damunta shi ne san mijinta wanda ala dole ake san rabasu gabaki daya baba mahmud ya hanashi zuwa gidan nasu.

In makaranta zata ya daukar mata driver shi ke kaita ya tsaya ko zatakai yanma ya dawo da ita gashi wannan semester din Abbakar din baya daukansu ko zuwa yai department dinsu sedai su kalli juna daga nesa dan bata isa tai masa magana ba dan in driver din yaganta kamar a idon Baban nata ne.

Zaune take gaban  gaban iyayen nata baba mahmud ya fara da gyaran murya kamin ya kira sunanta, ta daga ido ta kalleshi yace ba komai yasa muka kiraki ba se dan mu gabatar miki da lawyer din da zai kareki a kotu dan munyi munyi da yaroncan ya sake ki ya qi.

Tai saurin daqowa ta kuma kallonsu wannan shine lawyer din wanda aka nuna yasaki murmushi gami da fadin sunana Barrister Bashir salman ni zan kula da shari'ar taku ta kuma kallonsa tama kasa magana gabaki daya ta rasa abin fade.

Ki tashi kije gobe ne zaman kotun zai fara in ana buqatar wani abu daga gareki zan kiraki to Baba tace dan bata cewa kawun ma ta miqe tai waje.

Tana fita kukan da ta kwace ya tawo mata tai saurin barin bangaren tana shiga falonta ta

rushe da kuka...
[1/13, 4:27 PM] 🅰 " AXEEX✌🏼 D'🅱🅾Y😎: _POST BY GROUP OF HYPE HAUSA NOVELS BOOK WHATSAPP 08064400100_ 📚📚
[1/13, 4:28 PM] 🅰 " AXEEX✌🏼 D'🅱🅾Y😎: *ABBAKAR*

*200---210*

Jitai an dafa ta cikin sauri ta dago dan ganin waye ummi ta gani anti mene kike kuka dan Allah ki rage damuwa kinji tasa hannu ta goge mata hawayen da ya 6ata mata fuska.

Anti dan Allah ki fadan meke damunki ko addu'a ce na tayaki ba komi ummi kawai na tuna da baya ne.

Ummi tace anti kan Yaya Abbakar ne ko ummu tai saurin kallonta da mama ki ummi ta qara da cewa insha Allah bazasu rabaku ba anti.

Ummu cike take fal da mamaki wato tana ma ummi kallon yarinya, bata qara shiga mamaku ga seda taji ummin na fadin anman anti kince musu kina sansa ta kalleta sororo alamar me kike nufi.

Anti kema se kinyi wani abu ni inaji ajiki na bawai sunasan rabaku ba ne suna son ji daga gare ki ne sunasan suji kince karsu rabaku da bakinki.

Ummu tace to inba san rabamu suke ba me yasa gobe zasu fara zaman court narasa me yasa suke san rabamu na rasa me ya musu.

Ummi tace anti kiyi haquri ki daure kije kice musu kinasansa ina cewa sukai zasu rabaku dan suna zaton auren dole ya miki dan baki da gata yanzu inya sakeki se wanda kike so zasu baki indai haka ne kenan ko shi din kika ce kinaso zasu baki.

Mamaki fal ran ummu me yasa dani banyi tunanin haka ba da ita kallon yarinya qarama takema ummi ashe duk tana sane da abinda ke faruwa agidan nace "ummu kenan daman yawancin iyaye kan ma yaransu kallon yara qanana irin basu san komi bacin da wasu yaran sunfi wani babban fahinta da iya zance"

Ruqo hannunta ummi tai anti ki daure kije ki fada musu har bakin falon baba mahfud ummin ta rakota seda taga tashiga sannan ta juya zuwa gurinsu.

Da baba Bashir ummu taci karo yace ummulkairi ba yanzu kika bar nan bane tai saurin cewa eh Daman magana nakesan muyi to to yace ai se mu koma cikin tabi bayansa.

Sauran da suma suka miqe da zummar fita suka dawo suka zauna ganin ya zauna itama ta zauna yace tace zata fadi magana ne.

Baba mahmud yace munajinki ummulkairi tai ta maza gami da nemo duk nutsuwarta kamin tace daman roqarku zanyi dan Allah karku rabamu da shi wallahi inasansa.

Gabaki daya suka kalli juna gami da sakin murmushi kamin Baba mahmud ya dora kika ce kinasansa tai shiro da kinsan haka kikai shiru ai da bata kai ga haka ba ma.

Yanzu kije maganar shiga kotu anbarta zan nemeshi dan shirya yadda tarewar zata kasance jitai kamar tasa ihu dan murna ta miqe tana sun sun dakai yayin da fuskarta ke dauke da murmushin farin ciki.

Hartakai bakin qofa Baba mahmud yace ummulkairi tai saurin kintsa kanta dan niyarta tana fita tasa tsalle ta juyo inda wata matsala zaki iya samun ko wanne cikinmu kinji to tace tai waje.

Alhamdulillah take ta fade gami da dansa gudu tai bangarenta tana shiga ta rungume ummi tana murna.

Seda ta nutsu ta fara tunanin ko ta ya zata ma Abbakar albishir tunda yanzu bata da waya tun kwanan Babyn ta arba'in da rasuwa aka kwace wayar duk dan karsuyi waya da abin sonta.

Ummi kije gidansu Takwararki kice tazo inji ni ta tawo da wayarta to anti tace ta miqe tai waje.

Afalo ta taddasu sunata fira ta gaida hajiya dasu Abbakar dinma kamin tace anti takwara daman mum(da yake wani zubin haka take cewa ummun) ce tace kizo kuma ki  tawo da wayarki in kina wani abun kiban wayarki kawai in kai mata.

Ta6 wa ni rufan asiri muje inkai da kaina haka kawai a bunciken waya suka saka dariya gabaki daya ta ware mayafin abatar dake daure kanta ta yafa dan daman ashirye take sukai waje.

Abbakar ne ya biyo su yace yar mu zonan ta qarasa na'am yaya ya dan hade rai wato ita mum ni yaya to da ita dani waye ma yafi kama da wanda ya haife ki tasa dariya ita mana yadan hade rai alamar serious magana zaiyi itama ta nutsu.

Me mamar taki zatai da waya tadan kalleshi ko bajiki ni bane tace ai kai zata kira yai saurin cewa ni kuma eh yaya to me zata fadan a'a yaya kadai bari ta kirakan tukunna.

Pls ki fadan bazan ma nuna kin fadan ba yo daman cewa zatai anfasa zaman kotun yanzu su Baba sun yadda da aurenku da gaske kike eh mana yai dariya kije tukwicinki nanan tafe ya ja ya tsaya gami da tsurama wayarsa idanu jiran kiran ummu.

Ummi na shiga falon ummu ta amshe wayarta gami da yin daki ummi tace haba anti kofa gaisawa bamuyi ba bakuna ki fadan me zakiyi da waya ba ta juyo kindai san cikin samarinki ba

wanda yakai matsayin in snatching dinsa ko tasa dariya waya sani ko kin hango wani ne da an raba auren ki maqale masa tsaki taja gami da fadin wushe nan yarinya ummi ta qara da inji dan fillo ba.

Tana shiga daki ta hau kiran Abbakar dan ko number dinsa bata tsaya nema ba takanta ta saka dan ta haddace number dinsa.

Bugu daya ya daga duda yasan komi abinka da namijin duniya se mazewa yai a'a ummi lafiya kika kirani bacun kinsan ina gida shiru tai can yace wai bazakiyi magana bane.

Daurewa tai tace Barka da safiya barka dai ya fada cikin sanyin murya dan tuni jin muryarta ya rage masa kuzari a'a ummulkairi kece lafiya dai ko tai shiru kamin tace daman kirawo ka nai mu gaisa yadanyi shiru aransa yace nikam zanso ganin randa yarinyar nan zata sake dani da yawa" nace araina kamar yau ne".

Daman kan zaman kotunnan ne yai saurin cewa gobe ko tace eh karkiji komi ki dena damuwa kinji insha Allah baza'a rabamu ba tai murmushi yai  yace kinji dadi ko nace bazamu rabu  ba ko tai dariya eh mana.

Kan yace wani abu ta kuma magana daman fada ma zanyi anfasa zaman kotun yanzu su baba sun yadda da aurenmu bata jura cewarsa ba ta kashe wayar gami da yowa waje.

Ummi ta miqama wayarta tace gashi nan nagode tasa dariya anti irin wannan dadewa ana duben waya tai dariya se gashi duk ba number ko hoton wanda ya burgeni ciki kai anti har yayan nawa tasa dariya to shi saurayinki ne ummi tace dadina dake anti kwai iya baqa.

Kiransa ne ya kuma shigowa wayar ummi ta miqo mata wayar anti yaya a'a bazan daga ba pls anti wallahi bazan daga ba kice masa na shiga toilet .

Ummi ta daga wayar yaya tace bazata kar6a ba kuma wai tace ince tana toilet yai dariya to inta fito kice nace to tace kai yaya cewa fa nai ta fadan bawai tana ciki da gaske ba ya kuma yin dariya hoo ummi sarkin hada husuma to batai lefi ba inkin wasa kece ma zakiyi tasa qara ni kuma eh ke ya kashe wayar.

Ta kalli ummu cike da barkwanci tace eyye angama da yaya na tasa dariya to ance miki nidin wasa ce.

Shi kuwa yana kashe wayar yai cikin falo besan sanda farin ciki yasashi sakin qara ba irinta farin ciki hajiya tace kai kuma mene haka nan ya fada mata komi da ya faru itama tai murna sosai.

Tun wayarsu da ummu yake faman baza idanu dan ganin kiransu Baban ummu anman shiru yai sati guda kenan duda an aiko musu an janye batun zaman kotun anman  ba'a musu bayanin

komi ba duk ranshi babu dadi shi ya qagu yaganta a gidansa.

Zaune yake a office dinsa yana duba takardun da yama dalibai test kira ya shigo wayarsa kamar karya daga yana dubawa yaga Baba mahmud ne yai saurin karawa a kunne gami da sallama cikin girmamawa ya gaidashi kafin baba mahmud din yace yau kazo gida inasan ganinka bai jira yace to bama ya kashe wayar.

Murna ce ta cika masa rai agonsa ya duba yaga yanxu warfe biyu ne yanma batai ba yace ya ninke takardun da yake dubawa yai inda yake da koyarwa yau.

Biyar dedai agidansu mahfuz din ta masa kai tsaye gurin baba mahmud yai dan rabonsa da mahfuz tun mutuwar ko ya kirashi baya dagawa se yaga dama duda bayasan haka sedai babu yadda ya iya.

Cikin mutunci sika gaisa kafin baba mahmud ya dora da bakomi yasa na kiraka ba sedan in sanar da kai ko kuma mu tatttauna kan batun auranku da ummu.

Abbakar yadan muskuta cike da farin ciki Baba mahmud ya dora inasan in fada ma ada bawai qiyayya yasa muka tilasta seka saketa ba bakuma qi bane yasa muka takura se anje kotu ba duda daman ba xuwan zamuyi ha sedan munasan samun tabbaci daga gareta na tana sanka dan bamasan za6a mata wanda bata so.

Yanzu zamuso muji a ina kake ganin zata zauna seka fada mana dan kai mata kayan daki kuma inasan in fada maka mu agaskiya bamu yadda da kunyi aure ba Abbakar yai saurin kallonsa eh bamu yadda ba gaskiya.

Hakan yasa muka yanke nanda wata guda zamu daura muku sabon aure sannan doke ka kuma bata sadaki danmu bamusan ka bata ba kuma inasan kasani yarinyarmu kamar ko wacce mace take dan haka dole ka kawo lefe kamar yadda ake a al'adance dan bama san barin wani sarari da za'a mata gori a rayuwarta duda abaya mun riga munyi sake.

Dan haka kaje ka turo wakilanka kamar yadda kowa yake inyaso semuyi magana dashi.

Wakilan Abbakar sunzo anyi maganar komi wata daya kacal aka saka dan gudanar da bikin nasu.

Amarya ummu se gyara takesha kowa da irin tasa gudun mawar sedai Baba mahmud ya hana Hajiyar Mahfuz kawo komi indai naci ne kosha ko shafawa da sunan abaima ummu dan gyaran amar sabida yace ba'a sake da maqiyi.

Taji ba dadi sedai tasan ita taja ma kanta ummu duk batasan sunyi haka ba duda haka Hajiyar batai fushi ba komi da ita ake.

Ummu tai kyau tai wani fresh gashi daman sunyi hutun mid semester tai wata yar qiba.

Yau take juma'a yau kuma aka saka dan daurin auren nasu a masallacin old campus na BUK za'a daura bayan sallar juma'a.

Zaune take cikin qawayenta su Aisha sunata tsokanarta wayar Aisha tai qara ganin sunan da ke yawo kan screen din wayar yasata miqawa ummu.

Abinda ya ziyarci kunnenta ne yasata sakin ajiyar zuciya wani farin ciki ya ziyarce ta ba komi bane face lasifiqa da taji ana fadin Alhamdulillah an daura auren ummulkairi Yasir Mahmud da Abbakar Fahad kan sadaki dubu Hansin.

Yace Baby kinji me naji tai dan dariya a'a my Habu yai dariya kema ko Habun nanfa Hajiya kawai ke fade tadan miqe to aini nace My a'a kinadai san muyi fada kenan tai dariya wato nayi lefi tun ba'aje ko ina ba to kuwa anya amaryar ce ni yai dariya kan yace wani abu ta kashe wayar.

Aiko tana kashewa su Hafsa na shigowa wato har an fara soyewar ko tace to da tsayawa kallonku zan.

Yau asabar ita ce yini shagali kawai ake sha gidan ya dinke ba masaka tsinke abu daya ke damun ummu rashin ganin ko mutun daya daga ummanta itakam agaskiya bata ga anfanin mutun ya aure wanda ba yar garinsu ba.

Goma dedai masu kai amarya suka kai ummu gidanta dake Nan waje jen state road gida ne na alfarma da ya kunshi duk wani abin more rayuwa da jin dadin dan adam.

Anan da yawa suka kwana yayin da wasu suka tafi.

Washe gari da rana masu gyara inda za'ai walima suka hallara kan yanma sun gama komi guri ya fito tas kai kace gurin yin biki ne na taskeba ba gida ba.

Itama ummu masu kwalliya sunzo sun shiryata sun mata kwalliya irin wadda ake yayi yanzu su Aisha ma duk anan suka kwana sune qirgin biki dasu ake ta hidima.

Wajen hudu gida ya fara daukan harama mutane sun fara hallara ango ma kamar amarya dinne yai kyau sosai komai irin na amarya yasa shima milk shadda yasa mai dinkin kofi da golding kamar dai  Amar yar tasa.

Sunyi kyau sosai atare suka futi bayansu qawayenta ne se nasa suma biye dasu fadin kyan dasukai bata lokaci ne kaidai kana kallonsu kasan dansu akayi junansu.

Ba'abinda yaima ummu dadi se ganin innar Ummi tazo harda gwaggo da qawarta Ta Niger

aikam tai murna sosai.

Aisha ce ta bude taro da addu'a gami dayin taqaitaccen yarihin amarya da turanci sannan mahfuz yai na ango Abbakar yai mamaki dan be ta6a zaton Mahfux zaizo gurinba balle har yamayi jawabi kowa zazzaune yake sai music me sanyi dake tashi awajen.

Kamar ance ummu ta dago ta hangi ummanta da qannenta sun fito a mota da sauri ta miqe tai gunsu cike da farin ciki bama tasan sa'adda kuka ya kufce mata ba dagyar suka lallasheta Fadya qanwarta ta gyara mata kwalliyarta suka tawo gurin tare.

Kana ganinsu kaga jini daya koda yake ummu tama fisu kyau kawai dai ita baqa ce nasan da ita tayo farin su kyau ba'a magana.

Ummanta itama tai bayani cikin harshen larabci gami da saka musu albarka.

Kowa yaci yasha ya gyatse kowa se saka musu albarka yake se isha kowa ya watse anman duk yadda ummanta tai kan su tafi can main house ummu taqi dole anan suka kwan.

Satinsu daya suka shirya se jordan bayan karamci da suka sha gurin dangin ummu mijinta da yan uwansa.

Rayuwar gidan ummu rayuwa gwanin sha'awa komi atsare suke yinsa shi yake kaita makaranta in ta tashi lokacin ya tashi su tawo tare in be tashi ba ta tawo ita kadai tun yan sch din na gulmarta har sun fara gajiya.

Wasu ma daga wata department din ko faculty dinma har zuwa ganin wace me sa'ar ce tai nasarar auren Mutun mafi farinjini da burge yan mata.

Wasu yan matan ma in sunzo da niyar kusheta se su raina kansu dan gani suke tafisu komi wasu ma sekaji sun koma fadin ai shine ma yai sa'a ba ita ba nace "Hmm students se abarmu"

Bayan shekara uku da auren ummu da Abbakar zaune take suna fira dan basu da wata damu inka dauke rashin haihuwar da suke fama dashi anman in ba haka ba kam rayuwarsu fal take da farin ciki.

Abotar Abbakar da mahfuz ta koma kamar da sedai gidan Abbakar din ne baya zuwa daqyar ya fara zuwa shi kome Abbakar zemsai bazai shiga ciki ba iyakarsa farfajiya.

Aure kam mahfux yaqiyi sunyi sunyi yaqi inma kai masa maganar aure yanzu zakuyi fada
Cikin sa ne ya motsa masa duda ya dade be motsa ba tun yana daurewa har yafara kasawa ta dube shi ganin yana yamutsa fuska tace my me ke damunka kan yafe wani abu cikin ya kuma murdawa tuni ya zubo daga kan kujetar tai saurin yin gurin sa ganin kamar baya nunfashi yasa qoqarin daga shi sedai banbancin halitta wato raunin mace yasa ta kasa.

Waje tai ta kira me gadi driver baya nan su biyu da ita dashi suka daukeshi sukai mota hijabi kawai ta dauka da key din mota tai waje me gadi ya ja mata falon dan yaga bata hayyacinta.

Hajiya ki jira Bala yazo seku tafi No buden qofa kawai ya bude gate din ta ja motar da gudu tai waje dan tuni ta koyi mota.

Kai kawo kawai take aqofar dakin da aka shigar dashi doctor ya fito gami da fadin madan abin ya zama worse ki kira namiji muna buqatar sa hannun wani namiji dan mu masa aiki qodarsa ce ta ta6u sosai kasantuwarta jaruma sosai yasata kasa fashewa da kuka.

Doctor pls ban aron wayarka yadan kalleta kamin yace ok biyo ni office tabi shi yana bata tahau kiran Yah nasir dan ta haddace number dinsa.

Yana dagawa tace yah ummu ce muna asibitin malan Yaya ne ba lafiya pls kazo da wuri ka biya ka fadawa hajiyarsa bata jira cewarsa ba ta katse wayar.

Hankali tashe ya kira ummi qanwar Abbakar ya fada mata ya kira mahfuz kan ya fada agida shi kuma yai asibitin seda yace ya tambayi inda suke ta fada masa.

Mahfuz dinma hankali tashe yai asibitin hajiya kam se kuka take har sukazo asibitin.

Duk suna tsai tsaye gefensa dan ansamu yadan farfado ido kawai yake binsu dashi har yakai kan ummu ya miqa mata hannu tai saurin zuwa cikin dashasshiyar murya irin ta mara lafiya yake magana.

Ummulkairi na yafe miki kema ki yafe min inaso ki sani ni Abbakar me sanki ne har abada sedai inaji a jikina ba'a yomu dan mu rayu tare har abada ba inaji ajiki na bazan tashi ba tai saurin rufe masa baki tana girgiza kai hawayen da tun dazu take qarfin halin boyesu suka kwaranyo kan fuskarta yasa hannu ya goge mata su.

Ya ce ummu ki dena kuka banasan ko bayan raina ki shiga damuwa pls kinji ko ta gyada kai gami da fadin bazaka mutu kaji yai  murmushi kawai ummu mutuwa nakan kowa intazo ba yadda za'ai eh tace anman insha Allahu ba yanzu zaka mutu ba.

Ya ruqo hannunta yace inaso in roqeki alfarma dan Allah bayan bana raye karki auri ko wa inba mahfuz ba dan Allah alfarma zaki mun danni badan shi ba dan kuma Allah.

Ya miqo hannunsa gun hajiyarsa yace hajiya ki yafemin cikin kuka take fadin na yafe ma Abbakar anman bazaka mutu ba kaji sannu a hankali nunfashinsa ke qasa tuni tari ta turniqeshi Nasir yai waje ya kira doctor duk aka ce su fice.

Jiki a salu6e doctor ya fito ummu tabishi tana tambayarsa jikin Abbakar yai mata banza nasir

ya bishi da sauri.

Kasantuwar yasan Nasir yasa shi tsayawa Baka fada mana komi ba kayi gaba yakamata ka fada mana jikin nasa doctor din ya dan share gumi da fadin am sorry we lost him abinda ummu taji kenan ta zube agurin kowa har doctor din akayo kanta.....
[1/13, 4:28 PM] 🅰 " AXEEX✌🏻 D'🅱🅾Y😎: _POST BY GROUP OF HYPE HAUSA NOVELS BOOK WHATSAPP 08064400100_ 📚📚
[1/13, 4:32 PM] 🅰 " AXEEX✌🏻 D'🅱🅾Y😎: *ABBAKAR*

*PAGE 210---220*

Cigaban labari

Kai tsaye mota sukai da gawar Muktasir da driver suka kama ma Nasir suka saka shi ciki me mota ya tsinki ganye ya maqalama mota alamar sun dauko gawa ne.

Mahfuz ne yai ta maza ya miqe yai waje gurin hajiyar Abbakar yai da take ta faman kuka umma tashi muje a hada shi agabanmu dan muyi sallamar qarshe.

Ta dube shi ido jawur cikin da shasshiyar murya take magana pls mahfuz karfa ka fadan da gaske ya mutu din ya dafa ta nima ban yadda ba gani nake kamar mafarki ne sedai yanzu na yadda tunda sun tafi dashi ki taso muje kar akaishi.

Miqewa tai tabishi abaya motarsa da yazo da ita suka shiga ya jasu sai gida.

Ita kuwa ummu Allurar da aka mata ta fara sakinta firgigit ta farka cikin kuka gami da qoqarin miqewa Farida tai saurin riqota tana girgiza mata kai alamar ta koma cikin zafin nama ta tura farida gami da tsinke drip din dake jikinta.

A sukwane ta miqe tai waje sedai kasan tuwar allurar bata gama sakinta ba jikinta kuma ba qwari yasa tuni jiri ya debeta ta fadi gurin da gudu Farida tai gunta cikin kuka ganin kamar bata numfashi yasata fita aguje daga dakin tai inda nurses ke.

Suna isa da gawar ana kiran la'asar hakan yasa da suka shigarta gidansu Abbakar dan can suka kaita ko wannensu ya daura alwala sukai masallaci.

Bayan an idar ne Nasir ke fadawa liman nan da nan ya sanar a lasifiqa hakan yasa tuni wanda suka halarci sallah din suka gar zaya dan ayi jana iza tare dasu.

Kafin wani lokaci tuni lokon ya cika danqam ba wanda baiji mutuwarba dan Abbakar mutun ne me kirki ba ruwansa bashi kuma da abokin rikici.

Tuni yaya Babba ta iso seda su nasir suka qaraso suka fito da gawar zuwa inda za'a mata

wanta dan har an dora komi likkafani ma Baba mahmud ya kawo.

Kawunsa wato yayan babansa da kuma qanin habansa sune zasu masa wanka ruwa kawai suke jira.

An kammala hada gawar kwance yake cikin shigar da sedai amaka kuma in anyi babu me cire ma wato sanye yake cikin likkafani jira kawai gawarsa take akaita masaukinta na har abada.

Hajiyarsa aka fara kira tai masa addu'a ba abinda take fade se Allah ya jiqanka kuka kawai take ashe shine zai rigata tafiya abinda kawai tunani kenan tana tuno rana irin wannan da aka ce tazo tai sallama da mahaifinsa.

Alokacin gani take kamar zai dawo sedai gashi shekara ashirin da shida da rasuwarsa be dawoba kenan shima Habunta tafiya zaiyi ta har abada tuni ta fashe da kuka tabar dakin.

Kowa yai sallama da shi masu daukan gawa suka dauka sukai waje ummi.

Ummi qanwarsa ta dawo daga makaranta taga mutane jingim qofar gidansu anata alwla hankalinta ya tashi to wa ya mutu bacin lafiya  tabar gidan daqyar ta qarasa zuwa ciki.

Tana shiga taga anyo waje da makara kasa tambayar mene tai kawai ta fashe da kuka me tsuma zuciya.

Daruruwan jama'a suka sallaci Abbakar daruruwa suka bi gawar dan mata rakiya zuwa makwancinta na gaskiya.

Kasan tuwar maqabartar da nisa yasa a motar gawa za'a kaishi ta masallaci wadda daman shi ya siya matsayin sadaqatujjariya.

Mahfuz tare sukaje suka sayo motar ganin Abbakar kwance cikin motar matsayin gawa yasa shi kuka sedai hawaye kawai kebin fuskarsa yayin da yake tuna yarintarsu da samar takarsu har yazuwa shigowar ummu rayuwarsu.

Yasani Abbakar amini ne bashi da kamarsa sansa yake so na tsakani da Allah wanda shi yasan baya masa irinsa takuma san duniya bazai samu wanda ke masa irin sa ba cikin abokansa yasan ko yan uwansa basa masa shi haqiqa nayi rashi ya fada.

A hankula ya bude lullubin da aka masa fuskar nan shar kamar yace Aminin ya Amsa.

Tuni an haqa kabari dan haka suna isa suka hau kiciniyar binne shi.

Ita kuwa farida tana kiran nurses suka qaraso daya cikinsu ta fita dan kira Doctor yayin da

sauran suka maida ummu gado se faman fada suke ma farida dan mene zata barta ta miqe ita dai tai shiru dan tasan halin nurses da bala'i.

Koda doctor yazo ya dubata gami da yima Farida kashedin karta kuma barinta ta miqe dan za'a iya rasa cikin jikinta to kawai farida tace dan gabaki daya yaudin bata iya komi tun lokacin da doctor din yace Abbakar ya rasu.

Ummi na shiga gida aka fada mata ai Abbakar ya rasu nan tai waje ita dole adawo mata da yayanta dan be mutu ba dazunnan fa sukai waya bata da kudi ya mata transfer kuma ace mata ya mutu ina qarya ne dagyar aka kamota aka dawo da ita gida tana kuka.

Lokacin da suke shigar da gawar ne cikin kabari mahfuz yai saurin dakatar da fara zuba qasa wallahi da ransa yake fade Nasir ya ruqeshi haba mahfuz me kake haka ne yafa mutu.

Dasauri ya tan kada Nasir gami da juyawa ga kawun Abbakar yana fadin kawu wallahi da ransa da karfi kawu ya girgizashi haba mahfuz wai yaushe zakasan kaddara ne karfa ka kafirta kanka mutuwar ce baka yadda da ita ba kome.

Cikin kuka yake magana wallahi kawu na yadda da mutuwa kawai dai Aminina ne be mutuba naga yai motsi ba motsi yaiba mahfuz gizo ne yake maka.

Wallahi kawu yayi motsi in kuma kun bunneshi to kuwa ku kuka kasheshi zan kuma dinga kallonku matsayin masu kisa dan kun kashemin dan uwa.

Kawu ne ya dubi Nasir kasantuwar yasan Nasir din karatun likitanci yai yana kuma koyar da masu karatun likitanci yasa ce masa Nasiru kuma duba manashi zaka fimu ganewa ko ya mutu din ko da ransa.

Nace yace Kawu wallahi ya mutu tun dazu muka tabbatar a asibiti nace ka dubamin ko so kake mu binneshi qarshe mu dawwama cikin kokonton ko da ransa muka binne shi eyye.

Sosai nasir ya doba shi baya numfashi babu alamar yanada rai zaiyi magana yaji shima kamar yana motsi abin ya bashi mamaki zuciyarsa fa babu alamun tana bugawa.

Hannun yasa dedai jijiyar kansa yai shiru gami da maida hankalinsa kanta tabbas tana bugawa alamar harbawar jini sedai kadan kadan take wato zai iya mutuwa ko yaushe in ba'ai wani abinba.

Da sauri ya juyo da ransa sedai yana cikin danger da sauri suka ciro shi daga kabarin gami da cire audigar da ke hancin sa da karkade kasar da aka fara zuba masa sukai asibiti.

Yadda yake cikin likkafani haka suka kaishi asibitin, batare da 6ata lokaci ba likitoci suka dunguma kansa oxygen aka saka masa dan te maka masa wajen yin nunfashi seda suka samu

dagyar zuciyarsa ta fara bugawa yadda ya kamata suka dedaita numfashinsa sannan suka fito.

Mahfuz ka fadan meke damunsa ina ciwon qoda ne inji Nasir eh yaya qarya kake mahfuz alamun ciwonsa bana qoda bane.

Ciwon zuciya ne ya fada anman yana ciwon qodar wallahi nayi zaton ciwon zuciyarsa ya dade da warkewa tun yaushe yake ciwon zuciyar tun mutuwar babansu shi kenan Allah ya bashi lafiya amin yace.

Nasir ya kuma duban mahfuz yace kaje ka fadawa Hajiyarsa be mutu ba bazani ba yace Nasir yace bazaka fa kace eh inkaga nabar nan se ance min Aminin ya farfado.

Gyada kai kawai Nasir yai yai waje dan ya fuskanci mahfuz din yanzu baya hayyacinsa.

Gabaki daya hankalin kowa ya koma kan ganin farfadowar Abbakar sunma mance da baiwar Allah Ummu dake can kwance.

Se washe gari ummu ta farfado allurar ta saketa ta kuma dena jirin cikin kuka ta miqe tana fadin Anti Farida dan Allah karki cemin Yah Abbakar ya mutu ta dafa ta ummu nasanki da juriya ki zama jaruma pls mutuwa dole ce.

Ta miqe cikin kuka ba wata jaruma da zan zama ni inasan mijin kar abinne minshi wallahi zan zauna koda gawarsa ne wallahi.

Seda Hajiyar Abbakar tazo sannan ta tambayi ina Ummu se alokacin suka tuna da ita ba shiri sukai can bangaren da suka barta.

Tana ganinsu tahau kuka da sauri Nasir ya qarasa ya ruqo hannunta cikin kuka take tambayarsa mijinta yaja hannunta se inda Abbakar yake.

Kwanan Abbakar biyu a asibitun malan su mahfuz suka gama komi dan kaishi can qasar waje inda za'a kula dashi sosai duda suma nan din basu gajiya ba.

Da ummu aka tafi dan duk yadda sukai kan ta yi haquri ta zauna taqi.

Satinsu uku a india Abbakar ya farfado sedai baya iya komi se kallo da ido kawai.

Watansu biyu a india Abbakar yaji sauqi sosai jiki yai kyau komai yana iya yi da kansa sa6anin da dasaidai ummu tamai in bata kusa mahfuz.

Lokacin da yaji ummunsa nada ciki murna yai sosai harda dagata yana juyawa da ita tai saurin kwace kanta tana dariya tana fadin rufan asiri kaida baka da lpy da dai zan iya ai da na daga ka.

Shaquwarsu da abotarsu da mahfuz ta dawo kamar da koma fiye.

Daga india jordan suka wuce can gurin mahaifiyar ummu taji dadi sosai seda suka mata wata guda suka baro jordan zuwa Nigeria cike da kewa.

Lokacin da suka dawo Abbakar yai kyau yai qiba kaikace bai jinya ba cikin ummu ma ya dan fara fitowa.

Seda ta tabbatar ya ji sauqi sosai sannan ta kawo batun 6oye mata ciwon sa da yai wato be dauketa da mahin manci ba cikin kuka take magana jin kukanta yake har cikin ransa.

Ya jawota jikinsa yahau lallashinta dagyar tai shiru ummu ban boye miki ba nayi zaton na warke ai na fada miki ciwon qodar da nake.

Abin mata da miji yaita bata baki harta haqura kan alqawarin ya dena boye mata damuwarsa dan mahfuz ya fada mata yawan boye abu ransa da cunkushe damuwa ya jaza masa ciwon dan shima se ya takura yake fada masa meke damunsa.

Shi din mutunne da baya fadin abinda ke damunsa duk girman takaici yakan kunshe shi cikin ransa ne yaita in abu yai yawa ne yakan danyi kuka shima a boye.

Watansu biyar da dawowa ummi ta haifi yaranta yan biyu duk maza murna gurin uban gayya Abbakar bafa a magana.

Ranar suna yara suka ci sunan mahaifin ummu da na Abbakar suke kiransu da Walid da Amir.

Suna akai sosai bana wasa ba anyi gayya sosai.

Akullim inta kalli yan biyunta ta takalli tafkeken hotonsu dake jikin bangon dakin wanda sukai ita da Abbakar da babyn ta da ummi me rainonsa setaga kamar shine ahannunta banbancin kawai wannan biyu ne shi kuma daya ne.

Lokacin da rai arba'in har Niger sukaje ita da Abbakar da ummi dan ko bayan Rasuwar Baby Abbakar bata maida ita ba.

Sosai suka sami kar6uwa abinda ya baima ummu mamaki shine gani jarin fulawarta ya bunqasa ba wai yanzu iya magarya da zender ba state da dama na Niger kanzo siye buhu buhu.

Wajen miliyan biyar innar Ummi ta bata wanda tai tara tarawa cikin riba qin amsa tayi tace innar tasa ayi borehole da masallaci a unguwar dan lokacin data zauna agarin taga yadda suke matsalar ruwa tace sadaqatujjariya ga mahaifinta da kakarta da babansu mahfuz.

Sauran riba kuma tace in an samu araba biyu a ajiye mata daya daya inna ta dauka.

Qawarta Fiddo tayi aure har ya mutu bataji dadin gidan mijinba ummu ta tawo da ita dan ta cigaba da karatu a Nigeri.

Har can inda akama Abbakar masauki a niyame suka je sunyi murna sosai malan musa yace oh ashe zaka tuna damu bayan shekara biyar da tafuyarka Abbakar yai dariya na tafi cikin gaggawa bamuyi sallama ba zanso zumuncin mu ya dore sosai yai musu alkairi sukaita murna.

Ummu tuni ta gama degree dinta dan hartai masters lauya din da baban mahfuz yace dukiyarta nagunsa ma tuni ta nemo shi ta amshi komi nata gami da masa kyauta.

Kamfanin qere qere ta bude gami da tallafawa yara masu kwakwalwa duk yaron dake da fasaha ta qere qere ummu kan daukoshi musanman mara gata ta kaishi makaranta me kyau ta bashi aiki kamfaninta dan baje irin tasa fasahar in ka kammala jami'a inkaga zakai aiki da kamfaninta to in kuma bazakai ba takan tsaya maka dan samun inda kake so sedai bata ta6a tsayawa mutun dan barin nigeri da sunan aiki.

Tuni su Aisha sukai aure suma duk da yaransu zumuncinsu kuwa se abinda ya qaru.

Zaman Fiddo gidan ummu yasa suka saba da mahfuz dan yanzu yana zuwa gidan harsuyi fira da ummu dan itama ta saki jiki bakamar daba da take kullin cikin daure masa fuska yanxu ta mance da komi ta kuma yafe masa.

Ansha bikin Fiddo da mahfuz sosai iyayen fiddo sukaji dadi yayin da take BUk tana karantar BSC nursing, lokacin yaran ummu shida haihuwa biyar maza uku mata uku.

Muktar qanin Abbakar ma ya dawo ya zama kwararren likita yazama shi ke kula da asibitin da mahaifinsu yabar musu gado.

Maryam qanwar Abbakar kuni ta jima da yin aure harda diyarta mace tana da wani tsohon cikin.

Ummi ma qanwar Abbakar tai aure ta auri muktasir qanin Mahfuz zumuncinsu kullin qaruwa yake.

Ummu diyar wato ummi yanxu ana level 3 yayin da tuni suka dedai ta kansu da Ahmad amin ummu jira kawai ake ta kammala asha biki.

Zaman auren ummu da Abbakar abune abin sha'awa ga kowa koyaushe cikin san junansu suke sedai kunsan ako yaushe aka ce aure dole ana samun matsaltsalu nanda can anman in ma'auratan suka iya zamantakewa ba mejin kansu.

*Bayan shekara Ashirin da biyar zuwa da bakwai..*

Duniya ba gurin zama bace tuni Hajiyar mahfuz ta jima da rasuwa, itama ta Abbakar din tsufa sosai kullin gidanta cike yake da jikoki harda tattaba kunne dansu Nur din yaya babba sun jima da haihuwa.

Yau jikinta yaqi dadi hakan yasa sukai asibiti da ita sedai kansuje ta rasu kowa yaji mutuwar nan sosai su Abbakar harda kuka.

Walid dan wajen ummu tuni suka dedai ta da Shukra yar gidan Aisha bayan wata biyu da rasuwar kakar tasu aka sha biki.

Shima Amir yar gidan mahfuz yakeso basu wani bata lokaci ba akai nasu auren.

Fatima kuwa tuni ta jima da mutuwa qawar ummu da Aisha wata sch mate dinsu a buk sedai ta bar diyarta daya wadda ummu ta dauketa take kula da ita duda kuwa dangin fatiman sunso su hanata da temakon Abbakar suka bata.

Itama Kairat din ta girma ansa ranarta lokaci kawai ake jira asha biki.

*Bayan shekara goma sha daya.*

Ummu ce zaune jikoki sun ke wayeta na yaranta dana gurin ummi da na gurin kairat sun cikata da hayani kowa da abinda ke fade daga wancan yace gwaggo kinga wane ko se wancan yace gwaggwo a ina kika ajiye min kazana.

Abbakar ya shigo duk an tsofe  kannan ya furfure dan tuni yai ritaya yaransu ke musu komi duda kuwa ummu nada kamfaninta se abinda yai gaba shima.yanada nasa anman basa zuwa ko ina kamfanin ma kula musu ake dashi.

Ya dubeta sweetheart wai yaushe yaran nan zasu tafi ne ta dubesu kowa da abinda yake tai dari se nanda.sati uku what ya fada aikam iyayensu zan kira kowa yazo ya kwashe dansa haba ni nagaji abarnima in hutawa tsofa na da mata ta se ankawon jikoki tai dariya mu lokacin da muke kaima hajiya me tace yai dariya ita daban ai.

Na'im babban jikansu dan wajen ummi ya dubi kakan nin nasa yace kajifa wai Sweetheart har tsoffi sunsan love, Fadila yar wajen kairat tasa dariya bari kawai yah na'im ko kunya basa ji.

Eyye kingani ko yarannan samana ido kawai suke dole su tattafi Husain dan gurin walid yace ta6 ai ba inda zamuje Abbakar ya cilla masa lemar hannunsa kaji mara kunya to dole ku tafi Usman dan qarami da befi shekara hudu ba yazo ya fada kan Abbakar yana dariya.

Nana ma ta fada kansa Abbakar yace kai nidai na banu ummu yasa dariya.

An koma makaranta kowa ya koma gidansu anbar Abbakar daga shi sai ummunsa zaune suke yana shan fura kamar yadda al'adarsa take ya dan jawota jikinsa sweetheart ta ce na'am my D yaushe za'a kuma bada hutu nai missing din yaran nan tai dariya se bayan wata uku yai dan tsaki kamin yace.

Kai duniya ba komi bace ada mu biyu muke zaune muka haifi yaranmu sun tafi se jikoki suma tanzu sun tafi ta shafo gefen fuskarsa haka ne my D qarshe ma mutun shi daya zai dawwama akabari to Allah yasa mu cika da imani tace Amin ya kuma riqeta sosai ajikinsa sukai dan shiru na mintina kamin ummun tace my D yace na'am tace nagode.

Me akayi u support me alot yai dariya duty nane matsayin miji no need ki godemin tai dariya inasanka mijina shima yai dariya inasanki nima Allah yasa mu rayu a aljannah tare amin my D.

Alhamdullah nan nakawo qarshen littafin Abbakar.

*Abin lura*

_*Arayuwa muna buqatar yafiya gami da mantuwa kamar yadda ummulkairi ta mance da abinda mahfuz yai mata suka ci gaba da rqyuwarsu cikin jin dadi_

_*Mutun baya taba wuce rabonsa duk rintsi seka ci abinda Allah ya tsaga shine naka sannan zaka mutu inka nema baka samu ba to abinnan tabbas ba raboknka bane kamar yadda Abbakar har ansashi a kabari sedai kasantuwar rabonsa aduniya be qareba ya dawo ya ci gaba da rayuwa._

_*mutane da dama suna fadin me yasa bansama littafin suna Nasir ko ummulkairi ba sedai ni ina ganin Sunan Abbakar yafi dacewa da littafin Abbakar mutun ne me sadaukarwa kamar yadda yake ganin zai iya sadaukar da sosayyarsa ga aminsa._

_Abbakar mutun ne me iya tankwara zuciyarsa kamar yadda lokacin da zuciyarsa ta amince kan yin masha'a da ummu ya tankwarata yaqi yi duda alokacin tanada dama anman be hakanba se yazama mutumin kamsa kuma ni aguri hakan ya kamata mu zama masu danne san zuciyarmu in ba dedai bane._

_Abbakar mutunne me haquri da sanin ya.kamata duda kasantuwar rashin mutuncin mahfuz gareshi lokacin da mahfuz din ya shiga matsalar asiri shi ya shiga ya fita seda yaga yazama normal._

_Duda kasantuwar ummul kairi nada yaro bashi yai cikin ba bakuma da aure ta haifeshi ba anman hakan besa da sukai aure ya wulaqanta ta ba sannan kasantuwar yaron ba nasa ba baisa ya tsani yaronba yaso yaron tun kan yai nasa dan._

_Tabbas da zansa sunan wani ba Abbakar ba to kuwa na Nasir ne dan akoyaushe muna muqatar tausayi da san yan uwa muna buqatar muzamto jarumai alokacin da yazamto mana na baqin ciki._

_Nasir mutunne me san yan uwansa kulawa dasu ako wanne hali duda kasan tuwar farida yakeso da yaga auren ummu zak iya sauqaqa mata lamarinta ya akiye buqatar zuciyarsa dan ceto yar uwarsa._

_Nasir mutun ne da duk girman matsala yakan iya tattara nutsuwarsa guri guda kamin ya tunkareta kamar lokacin mutuwar baby Abbakar da shi kansa Habu din wanda kuna kowa anso yazamto mutun mai jarimtar nutsuwa a kowa ne hali._

_Miqama Allah lammuranmu akoyaushe shi yafi dan babu me maka abinda be ma ba zuwa gurin bokaye ba namu bane musanman mu mata komi kike buqata tashi cikin darw ki nema Allah na kowa ne zai baki duk girman buqata in kuwa kika riqi wani sa zaki qare cikin nadama kamar yadda Hajiya Batul tai._

_Kishi da yassada ba namu bane musanman kan yara inba haka ba zasu kaimu su baro kamar yadda suka kai Hajiyar mahfuz da shi kansa Mahfuz din danshi sharri dan aike ne in yaje ya dawo kan ka ke koma._

_Duk girman matsala in mukai haquri akwai sauqi kamar yadda ummu da tai haquri komi ya zamto labari_

*Godiya me tarin yawa ga duk wata ko wani da suka karanta fatan kukkuren da ke ciki za'a min afuwa ajizanci ne na dan adam.*
[1/13, 4:32 PM] 🅰️ " AXEEX✌🏻 D'🅱️🅾️Y😎: _POST BY GROUP OF HYPE HAUSA NOVELS BOOK WHATSAPP 08064400100_ 📚📚